□□□□□□□□□□□
DIYANA
□□□□□□□□□□□

Whtsapp: 08141799224

BIRNIN TARAIYYA ABUJA WUSE TWO.

Anguwa ce mai cike da manyan masu kuɗi ga kuma tsararun gidaje kamar a ƙasar turai .

A cikin anguwar akwai wani ƙeraren gida mai kyan gaske gidane daya sami ƙwararun magina masu aiki da ilimi , tun daga wajen gidan zaka gane mai gidan hamshaƙi ne wato Alhaji Sani ana kiransa da Alherin Allah , babban ɗan kasuwa ne sananne a kowace ƙasa kuma kowane fanni yanada kamfanoni da dama dakuma motoci wanan kenan.
daga gefe ɗakin mai gadi ne can kuma gefen kudu da arewa shuke shuke ne na wasu kyawawan flowers gwanin sha'awa , ga wasu ɗawisu da suke kaiwa suna komowa guwanin birgewa .
Iyalan gidan ne zaune a palon da za'a iya kiransa da aljannar duniya iya tsaruwa ya tsaru nera tayi kuka musamman ma danƙara danƙaran kujerun da suka mamaye palon ,wata farar mata ce zaune a ɗaya daga cikin jerin kujeru sai wasu yan mata su biyu masu kama da ita amma sun fita haske matashiyar matar ce ta dubi ɗaya daga cikin yan matan tace "Diyana zakuyi dare fa kinga har yanzu dadynku bai fito ba ,
Wace aka kira da Diyana ce ta taɓe baki tare da lumshe fararen idanunta masu ɗauke da zara zaran gashin gira tace "mom ni dama bason zuwa ƙauyen nan nakeyi ba dady ne ya matsa mini wai nice banison zuwa duk cikinmu ,
Budurwar dake gefe ce ta dubi momy fuskarta da alamun ɓacin rai tace " mom village ɗinnan ya cika sauro gakuma rashin tsafta ,
Diyana ce tace " good Afreeda ashe kin gane ,jin maganar tasu zatayi yawa ne momy tace " shiii alamar suyi shiru dan tajiyo takun mai gidan nata ,
ƙarasowa yayi da shiga ta alfarma a jikinsa shadda ce gezna fara wace tasha aiki , momy ce take ƙare masa kallo da murmishi a fuskarta shima mayar mata yayi tare da kallon su Diyana da Afreeda da hankalinsu ke kan wayar dake hanunsu ,
Dady ne yace " to nagama so ke nake jira rau rau Diyana tayi da ido tana kallon mom ganin batace mata komai ba yasata miƙewa tana bubuga ƙafa Afreeda na dariya ƙasa ƙasa ,
Dan tasan ita zata iya jure wuyar ƙauyennan amma Diyana kam tana tausaya mata, dady waje yayi dan shima ba mai son yawan magana bane kamar mom ,
Hand bag ɗinta Afreeda ta ɗauko mata tare da wata jaka mai kyau da alamu itace jakar kayan nata ,
mom ce ta miƙe ta nufi step ɗin dake tsakiyar palon bata ɗau lokaci ba sai gata ta fito da wato leda fara yar baba ta miƙawa Diyana , buɗewa Diyana tayi taga su man shafawa ne masu tsada dakuma takalma harda atamfa itama mai tsada kana ga turaruka , taɓe baki Diyana tayi tace "mom wanan kayan wa za'a kaiwa granny ɗinku taɓɓ hmm Diyana tasa kai ba tare da takuma cewa komai ba ,
Jerowa sukayi tare da Afreeda idan kaga yanayin tafiyarsu kai kace yayan sarakuna ,
Fuskar Diyana babu fara'a kasancewar dady na cikin mota yana waya hakan ya basu damar yin magana , Afreeda ce tace "Anty Diyana saifa kin daure da mutanen village ɗinnan dan lokacin da mukaje wlh cemin sukeyi anyi jar fata tashigo ƙauye kokuma sudinga bina suna kallo na ,

Dafe kai Diyana tayi kana tace " nashiga uku nikam nima haka zasuyimin ? har Afreeda zata yimata magana dady ' ya katsesu zo mu tafi ,
dady na back side ita kuma ta shige gaba dan batason zama kusa dashi kasancewar ba tun yanzu ba ya hanasu chart eyepice tasa a kunnen ta kana ta jingina kanta da kujera ta lumshe ido driver na shiga suka ɗauki hanyar ƙauye .

KANO. KƇAUYEN SHAFA
Kƈauye ne mai gidaje jifa jifa dakuma mutane iri iri yawancin gidaje nasu duk rufin ɗakin anyishi ne da jinka basu damu dayin katangu ba wasu kuma sunayi kana babu ginin siminti sai a wani gida dake gefe shi kaɗai .

Bacci mai daɗi ne ya ɗauki Diyana dady kam hankalinshi na hanya dan sun shiga kano a halin yanzu ma hanyar ƙauyen suka dosa , wata irin gargada suka shiga wace tayi nasarar farkawar Diyana a tsorace ihu ne kawai bata kurma ba ga mumunan faɗuwar gaba ,
Kƈarewa ƙauyakun kallo tashiga yi tana salati badai nan ne kauyen ba taɓɓ gashi dady yace " 5 days zanyi ina bazan iya ba , duk cikin zuciyarta take wanan maganar jin anyi parking yasata ɗago kai tare da juyawa ta kalli dady dake tattara wayoyinsa a kan siddin motar dady har mun iso ne ?" yes daughter yau zakiga granny ɗinki , yana maganar da murmishi a fuskarsa,
driver ne ya fito ya buɗewa dady mota kana ya buɗewa Diyana , a tare suka fito daga motar hanunta riƙe da wayoyinta guda biyu tabi bayan dadyn ,
Daga bakin ƙofa dady yai sallama jin muryar wata tsohuwa yasa Diyana waro ido dan ganin wacce mata ce zata fito ?".
Wata tsohuwar mata ce fuskarta taɗan tamushe haƙoranta sunji jiki tsabar cin goro tasa riga da zani dakuma ɗankwalin yadi barka da zuwa Alhaji tanata faɗaɗa fara'arta ywwa Hajiya , Hajiya ce tace " to kuzo mushiga jikalle ansha hanya ta dubi Diyana ,
Yamutsa fuska Diyana tayi batare da tace " komai ba suka shige ciki .
Tsakar gidan da yaji siminti fess yake a share ko tsinke babu amma hakan bai sa Diyana dena yatsina fuska ba tana tattare kayanta wai karsu ja ƙasa , shiga cikin ɗakin sukayi da yake malale da leda babu kujera sai yƈar tuguno Hajiya ta miƙawa Diyana batare da tayi magana ba ta karɓa ,Hajiya ce tace " Alhaji a ina ka samo wanan yƈar gwallin ?"dan naga kamar ba wannan bace da ta taɓa zuwa shekarun baya ?.
Kawar da zancen dady yayi ta hanyar durƙusawa yace " Hajiya bamu gaisa ba ina wuni washe baki Hajiya tayi tace" lafiya lao Alhaji ya aiki ya hidima yakuma Faɗimatun buɗe baki Diyana tayi cikin zuciyarta tace " waye Faɗimatun komai sai an ɓatawa mutum suna mom ce Faɗimatu taɓɓ ,
Dady ne yace " tana gaisheki Diyana ce ta kalli driver tace " kaje motor ka ɗauko wata farar leda ka kawo min , to driver yace " cikin rawar jiki ya fice Hajiya ce ta miƙe ta fita sai gatanan da kwanon fura da nono a wani baban kwanon silba da suga a leda dakuma ludayi ,
Tunda Hajiya ta shigo da nonon Diyana take keɓe baki dan inba na kanti ba batashan wanan , driver ne ya dawo hanunshi riƙe da ledar ya durƙusa yace " ranki shi daɗe gashi karɓa tayi ta ajiyesu gaban Hajiya batayi magana ba , kallonta kawai Hajiya takeyi dan a bisa dukka halamu jininsu bai haɗu da Diyana ba , dady ma ya lura da rashin sakewarta dama yasan halin abarsa ko anyi abinci a gida bataci inba tayi ra'ayi ba drinks sune kayan shanta sai cake da shauransu .

Alhaji nayima magana a inaka samo wanan yarinyar mai kamada aljana kayimin kunen uwar shegu ko ? dady ne yace "Hajiya Diyana ce fa ko kin manta ta yayar Afreeda ,kaji ai kusawa yara sunan mutunci bazaku sa ba sai wani suna mai kamada na biririka ,dariya ce taso kuɓucewa Diyana amma ta make , miƙawa dady haɗin furar tayi kana ta miƙawa driver dake zaune can gefe a tabarma takuma ajiyewa

Diyana a gabanta yatsina fuska Diyana tayi kana tace "I dont like this thing dady ta miƙe tana tari , la haula wala ƙuwata illabillah Hjiya take ta mai maitawa tana tafa hannu ta dubi Alhaji tace " mudai bamu ɗauko wanan mugun halin ba gaskiya ɗayar yʏar uwarta tafi dadɗin sha'ani ,
Nikam yaushe zamu jitu da wanan mai kamada zabiyoyin chaɓɗijan ,
Diyana dai na zaune dan hankalinta na kan wayarta maganar da taji dady nayi ne yasa ta juyo a tsorace " zaku jitu ita da zata yimiki sati ,
Washe baki Hajiya tayi tace "aiko dana sami yʏa suka haɗa ido da Hajiya Diyana ta sakar mata harara ,
Dady ne ya kalli Diyana yace " wai kin mance gurin wacce nace miki zanzo ne ?" wanan fa da kike gani mahaifiyata ce walh zan saɓa miki , Diyana dai kanta na ƙasa ba ma'abociyar surutu bace , wata yarinya ce ta shigo da gudu tana cewa kaka yau bazakije itacen bane ? Hajiya dake shan rahowar furar da dady ya rage tace " nayi baƙi jeki cewa mamanki Alhaji yazo to yarinyar tace " kana ta fice da gudu .
Da isarta gidan nasu dake zagaye da dangar kara tafara ƙwalawa mahaifiyar tata kira tana cewa " Talatu ki fito wanan yayan naki na bini yazo wlh harda baturiya kiyi sauri ,
Talatu dake ɗaki tana fere rogo ta leƙo tare da cewa da gaske kike yi tinene eh ? yasin kizo zaki ganhi harda baturiya ,
Yafo gyale talatu tayi jiki na rawa ta saka takalmin ta ' ta fice ta kwashi sauri dan tasan yau ta warke .
Kasancewar basuda nisa sosai dan danan sai gata a ƙofar gidan ganin sabuwar mota ne yasata tabatarwa ,tinene ce ta biyota da gudu tana cewa " Talatu kinga zahiri ko ga motarhi nan , ƙarasawa sukayi tayi sallama Hajiya ce ta amsa gimbiya Diyana na sallah a sallayar da ta ɗauko a mota ,
Harkin iso Hajiya tace tana washe baki yayanki ne yazo kuma yau ze wuce shine nace "tinene ta kirawo ki , Talatu na fama da susar kai tace " ai ganinan Inna ina yaje ne ? Hajiya ce tace?yaje sallah ai ba jimawa zaiyi ba yanzu zai dawo,
Talatu ce ta cire mayafin kanta tare da cire ɗankwali tasa hanu biyu tana sosa kanta , Hajiya ce ta dubeta tace " wai talatu har yanzu baki sawa ƙwarƙwatar magani bane ? dagudu Diyana ta miƙe ta daka tsalle sai gata a waje , shigowar dady ne yasata sunkuyar da kai tace "sannu da dawowa dady ywwa daughter lafiya na ganki a nan ?" kafin tayi magana Hajiya tace " uwarta Talatu take gudu dady ne yace " to maiya faru ? Diyana idanunta cike da hawaye tace " Dady ka tafi dani wlh bazan iya zama a nan garin ba ,

Kinci gidanku dady ya cewa Diyana , ya shige ɗakin Hajiya washe haƙora Talatu tayi tace " yaya hannu da zuwa kunsha hanya , wlh kuwa ya yara ? lafiyansu lau Alhaji ya hidimomi mungode fa , babu komai Alhaji yace " yana kallon tinene wanan yʏar gurin waye ?, Hajiya ce tace " ɗiyar Talatu ce fa gatanan kamar ka kifeta da kwando ga guru gurun idanuwa kamar na waccan ta wajen ,

Kwashewa da dariya sukayi Alhaji ya miƙe yace "toni zan tafi Diyana kiramin driver kokuma kice ya kwaso kaya a mota oky tace " ta fice tare suka shigo da drivern hanunsa ɗauke da buhunnan shinkafa da katan ɗin taliya da jarkar man gyaɗa da maggi da gishiri , dubu arba'in dady ya miƙawa Hajiya ita kuma Talatu ya bata dubu ashirin ai kamar an jefata a aljanna tahau zuba godiya tana ƙarawa ,
Dady ne yace "hajiya nanda wata ɗaya zaki dawo ABUJA dan wlh kina kusa abin zai fi ,zaro ido Diyana tayi tana nazarin irin zaman da zasuyi da wanan tsohuwar mai bala'in sa ido amma babu komai da ƙafarta zata nemi ta dawo ƙauyensu , hajiya na kuka tana sanyawa dady albarka tare da duk abinda yasa gaba ,
Shigewa cikin palon Diyana tayi tare da ɗauko jakarta ta dubi dady zan bika bazan iya zama a nan garin ba cikin ɓacin rai dady yace " anan na girma komai nawa anan yake kaf cikin yʏayʏana kece mai tsananin ƙyamar jinina ,to dole ki zauna har sati ya zagayo saboda zumunci abu ne mai ƙarfi , kuka Diyana takeyi kamar ranta zai fita da

ajinta da komai ta zauna a wanan banzan gidan wanda ko ɗakin zuba shararsu bai kai ba wajen kyau , niko nace wanan gida da kike rainawa shine ƙurewa gurin kyau a wanan ƙauyen ,
20k dady ya bata yace " to mu mun tafi Hajiya najin duk dramar da sukeyi taƙi kulasu Talatu ko tsabar murna har yanzu murmishin fuskarta bai ɗauke ba, dady 20k is to shot tana bubuga ƙafa 5k ya ciro ya daɗa mata yana bata haƙuri akan zai turo driver ya zo ya ɗauketa , Hajiya ce ta matso tana cewa maganar sai kace ta munafurci da wani yare kukeyi dan kar ajiku ko , wlh Alhaji ka sakalta yayanka da kashe kuɗi , dariya dady yasa dan inya biyewa Hajiya bazai tafi yanzu ba , shigewa mota yayi yana ɗaga musu hannu ,
Tinene dake gefe tana ƙarewa Diyana kallo gaskiya kaf cikin ƙauyenan bata taɓa ganin mai kyau irinta ba gaskiya yan binni sunji daɗi ko kaushi basuyi bare faso, Hajiya ce tace " baiwar Allah taso mu higa gida yamma tayi Talatu ce tace " Hajiya nikam nayi gida yau zamu hyarɓi jar miya yasin yaya Sani ya jiƙani da nera ai wlh ko Ado bazan nunawa ba dan yana ƙyala ido to zai rabani dasu ,
Hajiya ce tace " harkin gama abincin ne ? a'a wlh ina cikin gyaran rogo he ga tinens tazo kirana wai Alhaji yazo inafa zan gama tinene ce ta kwashe da dariya kana tace " wayaga kaka a binni yasin sai sun koroki ,

Hajiya da haushi ya ɗebeta tace " cin uwaki niɗin bzan iya zama a can ɗin bane to kikasa wasa ma dake zani , Diyana ce takuma cika a zuciye ta shige tabarsu anan sunata surkulllen maganarsu....!

Kubiyo ni dan jin cigaban labarin ya rayuwar Diyana zata ƙare a ƙauye biya 200 ki karance shi cikin kwanciyar hankali .
[

Mangariba ta sako kai Talatu ta wuce gida itama kamar ba mai son mutane ba dan kamar batasan Diyana yarinyar Alhaji bace kodan yangar da taga tanayi ne oho ,
Tinene da bata wuce gida ba ta dawo gidan Hajiya ta zauna a bakin kofa ,
Hajiya ce tace " tahi karki janyo mana fitina kina sane almuru tayi ,tinene ce ta harari Hajiya kana tace " wlh sa ido yayi yawa yar birninnan da wuya ta iya zama dake wataran sai tayi kamar zata gudu ga ki da gani babu ƙyalewa ,
Tafa hannu Hajiya tashiga yi tana salati tare da cewa" au ni zakiyiwa cin mutunci wlh Ado kika yiwa ba niba hyahya hya kawai wanan kalmar tabawa Diyana dariya dan duk ɓacin randa take ciki sai da ta dara ,
Tinene ce ta miƙe tare da karkaɗe zani tace " ha muzo muyi daka tsami dan yasin bazanyi wanka ba ko kallonta Hajiya batayi ba da alamu anyi faɗa kenan .
Wayar Diyana ce tafara ring cikin farinciki ta duba number dan tun ɗazu take ta neman network babu ,
Da sauri ta ɗaga wayar tare da karawa a kunnenta tace " hello Afreeda yakike ?"
daga can ɓangaren Afreeda tace "sis kina jina kuwa ? alamu dai na rashin network babu ya ɗauke ,
Diyana rasa me zatayi kawai tahau kuka tana kiran ta shiga uku harda shure shure gata ƙatuwa ,
Da gudu Hajiya tayo ɗakin har tana shirin faɗuwa ta sameta a zaune kan jakar kayanta tana shure shuren ƙafafunta ,
Nidai naga ta kaina yanzu waccan mai kamada bulaliyar ta gama gayamin magana yanzu kuma ga wanan mai kamada yan ruwan aljanunta sun motsa Hajiya harda yar kwallarta wai ta tausayawa Diyana hhh,
Batasan ciwon rashin network bane ya motsa ,ƙwalawa tinene kira ta farayi tinene dake goge kaushi da dutsen goge ƙafa taƙi kulata , can kuma tace "ashedai mutum yanada rana eh naji koma mai zakice zoki kirayo min malam fari ya duba yarinyar nan ,

Diyana ji takeyi kamar ta ɓarar da Hajiya saboda tun farko jininsu bai haɗu ba rasa inda zatayi ta hukunta hajiya tayi can wata dabara ta faɗo mata aikuwa ta tuntsire da dariya ,
wanan karon saura kaɗan Hajiya tasa ihu ,
tinene ce tace " toshi malam farin me zaiyi miki wlh kincika fitina ,
Hajiya ce tace " kice inada mara lafiya a gidannan ni dare ma nake tsoro wlh,
Ficewa tinene tayi tana tafiya tana mita da isarta gidan ta ganshi zaune akan wani dutse yana alwala ina wuni tace " lafiya lau yʼar budurwa , tinene ce tace " wai kazo inji Hajiya tanada mara lafiya a ɗakinta ,
Subhanllahi wacece ?" malam fari ya tambaya,
Wata baturiya ce wlh kazo zaka ganta,
washe baki malam fari yayi kana yace " bari a fito sallaj kice mata ganinan zuwa yanzu ,
To tinene tace " ta koma gidan ta samu Hajiya na sallah ta koma waje ta kwaso kwandan soso ta shige cikin uwar ɗakin Hajiya da murmishi a fuskarta , Hajiya na idarwa ta zabura tayo uwar ɗakin tana cewa ubanme zakiyimin wlh ban yarda dake ba kitafi gidan ubanki ni banison shishigi yanzu ma badan dare yayi ba wlh dana watso miki kayanki kin wuce tunda ni yanzu kin rainani ,
Hajiya nata banbamin faɗa itako Tinene na shafa mai ko a jikinta dan inda sabo ta saba baya damunta ,
Ko uffan batace wa Hajiya ba sai ma waƙa data kamayi .
Sallamar malam fari ce tasa Hajiya fitowa tana washe baki suka gaisa yake tabyarta ya mai jiki da sauƙi Hajiya tace " amma fa bata dena kukan ba ,
Malam ne ya matso kusada Diyana yana tambayarta maiya sameta ,
Wani azababben tsami dataji yana tashi ta gefensa yasata ficewa da gudu tana kuka ,
Hajiya ma fitowar tayi ta riƙota Diyana na ƙwacewa dan kaf mutanen gurinnan ɗaukar ƙazamai take yimusu har Hajiyan ma ,
Samun kujera Diyana tayi yʼar tsuguno ta zauna amma fa a dole tacigaba da kuka , takalmi malam yasa kana ya sami kujera shima ya zauna dan bai fahimci mai yasa ta gudu ba ya ɗauka aljanunne tunda basa tsoron adu'a ko kaɗan.
Tinene tunda taji anfara artabu da Diyana ta daka tsalle tana dariya kujera ta taka ta janyo wani ƙaton kwanon silba mai cike da soyayyen nama da cincin tasan koda yaushe Hajiya bata rabo dashi wanan zuwan na dady ma sai da ya kawo mata wani na yau kam ta cika baƙar leda tam dan ledar ma daga mararta take .
Hajiya ta mance Tinene na ɗaki saboda ta ruɗe malamin ne yace " baiwar Allah maiya sameki ?"da kamar Diyana bazatayi magana ba can kuma tace "nifa lafiyata ƙalau rashin network ne yasani kuka ,
Hajiya ce ta mai maita newak ? no am say network shima dai malamin ba fahimta yayi ba amma yafi bada ƙarkin abin cine kokuma abin sha miƙewa yayi jiki babu ƙwari garin kallon Diyana ya bige da bango ,
Fitowar Tinene daga ɗakin Hajiya ta dubeta tace " kakalliya nayi kyau kuwa ? yaufa haladu zai zo kinga ya kamata na tsara kwaliya tana fari da ido ,
Diyana ce ta ɗago kai ta kalli Tinene fuskar nan tasha jar hoda ga farin janbaki ƙamshim man ma da ta shafa bai yiwa Diyana daɗi ba dariya Diyana tasa kana ta miƙe tabar Hajiya a gurin,
Hajiya na tsaye kamar gunki har yanzu bata yarda Diyana batada aljanu ba .
Tinene dataga Hajiya taƙi kulata tayi hanyar waje zuciyarta farinciki dama a gidansu daga sallah sai cika ciki suke cin nama ,
Diyana ce ta ciro hijab a cikin kayanta ta fito batare da ta kula Hajiya dake tsaye tun ɗazu ba itako Hajiya wanan abun yafara yimata ciwo amma tabari duk lokacin da Alhaji yakuma zuwa zasuje gurin wani malami mai aganin Aljanu.
Fita tayi batasan ina zata nufa ba tafara tafiya tana dube dube wani yaro ne yazo wucewa da alamu aikansa akayi , Diyana ce tace " kai dan Allah innane ake siyarda Swan water tsayawa yaron yayi yana kallon ta tunowa tayi da maganar sis tanta ,

tace " am sorry to ko kasan shagon da ake siyarda ruwan gora ko ruwan leda ? eh yaron yace " wancan hyagon ne can zani ok to nagode ,
Yana gaba tana binsa a baya cikin salo da iya taku har suka iso shagon ,
Jitayi yaron yace "Idi abani ƙarago da garin kwaki zaro ido tayi badai shine zai ci ba ? a zuciyarta take maganar ,
Yaron yazo wucewa ta kira shi ta miƙa masa ɗari biyar kallonta yayi yace " me za'a sawo miki ?"Diyana sai da taɗan lumshe ido dan ɗabi'arta ce hakan tace "nabaka ne , cikin murna ya hau yimata godiya Idi ne yace " wlh kazo mu raba dan idona yagani abinka da basusan zasu samu ba suka raba ɗari biyu da hamsin kowannen su ,
mai shago kabani ruwan leda bag ɗaya dakuma Faro in akwai ,
Idi ne ya dubi Diyana da sai yamutsa fuskarta takeyi yace " Hajiya akwai ruwan leda amma banida jakar saka miki ,Diyana taso yin dariya amma ta fizge tace " duka ledar cikin rawar jiki ya ɗauko ya bata , kana yace " ammafa babu ruwan gora ,okay Diyana tace " bani canji yaron da tabawa kuɗi ne yace" kawo in kai miki , badan kayan sunyi mata nauyi ba da bazata bashi ruƙon ɗaukar leda ba kasancewar duk yɑn ƙauyen ƙyamarsu takeyi, haka dai ta barshi ya ɗauka bayan ta karɓi chanjin ta suka wuce gida .
Hajiya na tsaye a bakin ƙofa tayi zugum tana jiran shigowar Diyana tsoronta ɗaya kar yɑr mutane tabi wani ƙauyen ,
Jin sallamarta yasa Hajiya washe baki tace " ina kika higa ne yɑr albarka ?" Diyana ce ta taɓe baki kana tace " naje siyo ruwa ne ,yaron yana ajiyewa ya fita .
Salati Hajiya tahau rafkawa tare da cewa"au yanzu duk tsaftatacen ruwan dake tuluncan be i'heki ba saikin siyo ruwan bature ? dont worry Diyana tacewa Hajiya ,
A' lallai kuwa wlh Alhaji ya ɗauko hanya marar ɓulewa amma zai kuma dawowa wlh bazata saɓu ba ,
Ita dai Diyana tama wuce abinta ta ɗauki ruwan alwalah tana idarwa ta tada sallah janyo jakarta tayi ta ɗauki cake ɗin da momy tayi mata tafara ci da nutrimilk , ƙara duba wayarta tayi chaji saura 20% gashi tunda tazo bata sami lambar momynta ba sunfara waya da Afreeda network ya ɗauke , dafe kanta tayi tana tunanin anya zamanta zai yi a ƙauyen nan,
Bayan sallahar isha'i Hajiya ta zubowa Diyana tuwo miyar kuka da man shanu tunda Hajiya ta shigoda tuwon tafara jin tashin zuciya da sauri ta kawar da kwanon tana toshe hanci , wata uwar harara Hajiya ta wurga wa Diyana dan yau ta ƙureta ,
Hajiya ce ta kama ƙugu tace " ke yɑrnan banison kinibibi wlh inbaki fita idona ba zan dakaki ,
dariya ma tabawa Diyana aikuwa tahau ƙyaƙyatawa dukda ita ɗin ba mai son yawan dariya bace , aikuwa Hajiya ta ƙara ƙuluwa ta kuma girgiza ƙugu niko nace kamar muciya lol Diyana kam zanyo blanket ɗinta tayi ta shimfiɗa a palo ta yi filo da jakar kayanta , tsabar bakinciki da ya isheta ma waƙa ta kunna ta toshe kunenta ,
mita Hajiya taci gaba dayi kamar zata ari baki oh ni Hafsu naga ta kaina indai birni ne wlh Allah wadai nikam tayi uwar ɗaki tana kakaɓe zaninta ,
tana zama tayi bakin gado tana lilo da ƙafarta ,kasancewar gado mai rumfa ,
juyawar da zatayi taji cizo innalilahi to mai ya sameni ?" hango cinnaka tayi yana tafiya ta gefenta sai yanzu ma tafara jin cizon , abinka da jikin tsohuwa yaji jiki tafara susa lalubar ƙarƙashin filo tayi koda zataga man zafi gurin harya kwaile tsabar susa tana ganin man tahau sharɓawa aikuwa tasha zafi ƙaramin hauka ne batayi ba, Diyana tana jiyo surutunta tayi shiru tana bin waƙar Hamisu breaker mai taken Jarumar mata anan gurin ma Hajiya tana jiyo saurin muryarta dan taƙi jinin tayi magana ayi kunnen uwar shegu da ita ,tofa da alamu dai Hajiya bazasu jitu da Diyana ba ..
Diyana kuwa cikin ranta cewa takeyi ai tunda kince sa ido ne aikinki to wlh nafiki bari dare yayi sosai zaki gane .
Bayan wasu mintuna bacci ya ɗauki Diyana bata samu tayiwa Hajiya hukunci ba .

Washe gari da asbha Hajiya ce tafara tashi sai da ta idar da nafil filinta tazo ta tashi Diyana ganin taƙi tashi yasa Hajiya fara sana'ar tata wato mita komawa tayi ta kwanta tunda ta tasheta taƙi tashi ,
Saida gari yayi haske misalin ƙarfe bakwai Diyana ta motsa lokacin Hajiya ta kuma tashi tana gaban murhu ɗumama tuwo ,
Sannu Diyana tacewa Hajiya kanta a ƙasa ,
Yawwa yʼar albarka Hajiya tace " shigewa banɗakin da ya zame mata dole tayi bayan ta fito ne ta sunkuya zatayi alwalah taji Hajiya na masifa Diyana ce tace " shidai mutum kullum cikin masifa yake ,
ashe Hajiya ta ji, aikuwa takuma ɗorawa tana cewa yanzu ban isa nayi ajiya ba sai anyimin sata ankwahe nama ankwahe abinnan da akeyi da fulawa to yau zanci uwar ɓarawon nan bari Tinene ta shigo yʼar kan uba datanada gaskiya da asubar fari zaka jiyo sallaɓarta tazo cin ɗumamen tuwo .
Diyana dai bata sake magana ba tana gamawa taje ta fara sallah tana idarwa tayi adu'oin ta, ɗibi ruwa a randa badan ranta yaso ba ta koma ɗakin ta ɗauki soso da sabulu tashiga wanka , ta daɗe tana wanka kasancewar jiya bata samu tayi wankan dare ba ,
Tsaye Hajiya take tana jiran shigowar Tinene ganin ta shafe mintuna bata shigo ba yasa Hajiya komawa ɗaki tafara cin tuwonta ,
sai da rana tayi sosai har anyi azhar Tinene ta kwaɗo sallama , gyan gyaɗi Hajiya takeyi a kan kujera amma dake tasa abin a ranta a zabure ta miƙe tanajin Tinene ta shigo ta cakumo ta tare da cewa yanzu kin kyauta kenan? " Tinene ce tahau borin ƙarya tana cewa wlh kaka kidena ƙalamin sata nice kaɗai a ɗakin ? Hajiya ce takai dubanta ga Diyana dake tsara kwaliya tana shirin sa kaya tace " to wazan ƙalawa inba keba waccan mai kamada zabiyoyin ba komai takeci ba bare nace ita to wlh zan haɗaki da Talatu dan bazan yarda ba, haka dai Tinene tasamu ta zulle dama ba yau suka fara ba .
Kwanci tashi asarar mai rai yau kwanan Diyana shida a ƙauyen SHAFA babu abinda ya sauya na daga ɗabi'unta sai dai takanci abinci intaga yayi mata .
Diyana ta gyara kayanta sbda basuyi datti ba ta ninkesu ta saka a jaka a yʼan kwanakinnan suna ɗan magana da Hajiya ,
Gobe takesa ran driver zai zo ɗaukarta wayoyinta babu caji duka sbda garin babu gurin caji tun tana baƙincikin hakan har tazo ta haƙura ,
A daren yau ne Diyana ta shirya yiwa Hajiya mugunta .
7:pm na dare bayan Talatu tazo sunɗan taɓa hira da Hajiya har Diyana ta gaishe ta ,ta jima a gidan sanan ta tafi yau dai tunda Tinene ta tafi gida bata shigo ba gashi dare yayi sosai lokacin ƙarfe tara da rabi , Diyana ce ta ɗauko bredin da Hajiya ta bada aka siyo mata da madara kasancewar yanzu dai ƙyan ƙyamin ba kamar da ba amma fa akwai ,
yanzu damuwarta ɗaya Allah yasa kar ace za'a tafi da Hajiya dan tanada yaƙinin zata dinga haɗasu faɗa da dadynsu amma daga yau zata fara tsorara ta ta ,
Hajiya tagama gyan gyaɗin da tasaba akan kujera ta miƙe tacewa "Diyana yʼar albarka sai da safe, Allah ya tashemu lpy Diyana tace " yaukam bacci babushi a idanunta duk akan za'ayiwa Hajiya hukunci .
Kʼarfe goma da rabi kamar an tsikari Diyana ta miƙe ta juya ta ciro wani farin hijab nata mai niƙab dogo har ƙasa da ' alama na sallah ne ,
Shiga cikin uwar ɗakin tayi tana ƙarewa jeren ɗakin kallo taɓ wasu ɗakuna ma sai ƙauye wai yazuma anan gidan a dol gidan masu kuɗi kenen ko uhm ,
Tunowa tayi da abinda ya kawota , tsinken tsintsiya tasamu tafara shafo fuskar Hajiya dashi kana ta ɗauko kujera ta zauna tanata bin fuskar da tsinken tsintsiya , jin anyo ta wajen kunnen Hajiya yasata farkawa a zabure tana cewa yauma shazumamun ne suka kuma shigowa bayan na rannan dana kwashe ,
Bata lura da Diyana dake gefe ba sauya murya Diyana tayi tace " nazo tayaki kwana ne nice yarinyar Aljani ɗan kutub wata uwar durowa Hajiya tayi ganin farin abu, babu fuska kamar likafani...!

Dan Allah kuyi haƙuri kuji tausayin bil adama wata uwar dariya Diyana ta saki badan tasan tanada babbar murya haka ba, tsumar jikin da Hajiya takeyi ne ga ɓurma mmen baki gaskiya comedy.com taci dariya ita da bata dariya sosai ,
Girgiza kai Diyana ta fara yi da farin hijab ɗin da ya rufe mata fuska , itako Hajiya ta haɗe hannuwa biyu tana cewa kuyi haƙuri nidai bansan laifin danayi muku ba tunda kwana biyu ba higa jejin nakeyi ba bare kuce naje na yimuku wani abin ,
Wata uwar ƙara da Diyana ta saki ne yasa Hajiya zabura zatayi palo dosota Diyana tafarayi kana tace " kwanta kuma da safe mukaji kinyi maganar mu sai mun juya miki baki gefe maza ki kwanta Allah sarki Hajiya an maidata kamar baby .
Ta koma ta kwanta tare da runtse ido Diyana ko yin alamun kamar mai fita tayi ta shigo a hankali ta kwanta .
Washe gari Hajiya a makare ta tashi lokacin ma anyi sallar asbha tunda ta tashi yau ko mita babu juyawa tayi taga inda Diyana ke kwance taje kusa da ita tace " ke yar albarka tashi gari ya waye , tom kawai Diyana tace "jiki a sanyaye Hajiya taje ta haɗa wuta ta je yin alawalh kafin taje sallah wutar ta kama ta ɗora ruwan kunu ta je sallah tana idarwa ta koma uwar ɗaki ta riƙe baki tana mamakin abinda ya faru da ita jiya gashi ance karta gayawa kowa , girgiza kai tayi tana nazarin inhar Alhaji yazo yau to bazata zauna a garinnan ba sbda tunda aka fara yimata haka to gaba ranta za'a nema ta miƙe tayi waje ,
Diyana na lura da yanayin Hajiya jitayi kuma taɗan bata tausayi wata zuciyar tace " ai da bakiyi mata haka ba da tana nan tana mitar da tasaba .
Tinene ce ta shigo tana kiran kaka ! kaka ! jin Hajiya taƙi kulata yasata ƙarasowa tace " kaka lafiya kuwa ? Hajiya ta sako tuwo a kwano zatakai ɗaki tace " ke ni kauce kibani gu , kaucewa Tinene tayi ganin yau babu masifa kuma babu alamun wasa .
ƙarfe goma na safe driver ya iso ƙauye lokacin Diyana ta shirya shi kawai take jira ai tanajin horn ɗin mota ta miƙe tana cewa to Hajiya a yafemu ,
Hajiya dake ɗaki tanayi walha sallamar ta kenan ko adu'a batayi ba ta taso tana mita ,
"Saikace ina cizonki ai kyabari in fito ke ga ganɗoki ko kokuma mun gundureki ne ?".
Lumshe ido Diyana tayi batace komai ba , hakadai Hajiya tayi ta gama tayi shiru .
Driver ne ya fito daga mota ya shigo gidan Hajiya durƙusawa yayi har ƙasa ya gaisheta cikin fara'a ta amsa tana tambayarsa yasu Alhaji da Faɗimatu ?"..,
duk suna lpy suna gaidaki driver yace " ya miƙe tare da kallon Diyana ya gaisheta a yangace ta amsa dama ɗabi'arta kenan,
Kana yace " inkin shirya hajiya sai mu tafi ai kafin yakai ga ƙarasa magana Diyana tace " nafa shirya dama kai nake jira Hajiya dai taga ikon Allah wata ƙatuwar leda tabawa driver ya bawa momy zasu fita kenan sai ga Talatu ta shigo ,
Ina kwana Diyana tace "da fara'a Talatu ta amsa da lpy yaune tafiyar ne ? eh Diyana tace suka ɗunguma sukayi waje ,
back side ta shiga suka kuma yin sallama Diyana ce ta kalli Hajiya kana ta ɗan yamutsa fuska tace " ina wanan yarinyar ? washe baki Talatu takuma yi tace " ai na aiketa hyagon Haliru 1k Diyana ta bawa Talatu ta ajiyewa Tinene aikuwa sun sanya mata albarka .
Motar na shirin tashi Hajiya tace "to yar albarka sai Allah yayi zuwanmu killer small Diyana tayi kana tace " saikin zo driver yafara tafiya .
Shunyi tafiya mai nisan gaske kana suka ɗauki hanyar Abuja Diyana takan tuna rayuwarta ta ƙauye jifa jifa tayita murmushi musamman farin hijab ɗunnan data sawa Hajiya yana matuƙar sata nishaɗi ,
Jin horn da driver yakeyi ne yasata ɗago kai Alhmdulilh tace cikin ranta ,mai gadi na wangale get ta
Hango momy da Afreeda suna tahowa da murmishi a fuskar su hawaye ne suka zubo mata tarasa na miye ,
Mai gadi ne ya buɗe mata murfin mota ta fito da gudu ta faɗa jikin momy ta saki kuka ,

Afreeda ganin kukan sistan ta yasata fara kuka ,
Momy ce ta hausu da faɗa tana cewa " meye kuma na kuka bayan Allah ya dawo dake lafiya ,
Diyana batayi magana ba suka ɗunguma zuwa palo zama sukayi a kujera momy sai kallon ɗiyar tata takeyi ga wata muguwar ramar da tayi kuma jikinta ta gefen fuskarta ga cizon sauro nan, jinina kai momy tayi batare da tace komai ba ,
Tunani ta fara batada ikon hana Alhaji tafiya da Diyana ƙauye .
Jin hirarsu ce ta dawo da ita daga duniyar tunani Diyana tace " momy mai kuka dafa ne ? Afreeda ce tace " tuwon shinkafa miyar shuwaka ,
Yamutsa fuska tayi kana ta ƙara da shagwaɓe fuska kamar zatayi kuka tace " acan ma mutum baiji daɗi ba , anan ma bazanji ba ?" momy dai batace komai ba sbda rigimar Diyana tafi ta ɗan yaye wani time ɗin ,
Diyana ce ta miƙe tana fushi ta nufi fridge hango fanta tayi mai sanyi hakan ya sata ɗaukowa ta ciro ragowar cake ɗinta a hanbag tafara ci kamar an aikota ,
Niko nace su Diyana an daɗe ba'a haɗu ba .
Saida ta shanye babbar ƙwalba kana tayi gyatsa ta maida kanta ga kujera ta jingina ,
Momy da Afreeda banda kallonta babu abinda sukeyi ,
Afreeda ce ta ƙunshe dariya tace " sis yaushe rabon da kisha fanta ?".
Shigowar dady ne ya hana Diyana bawa Afreeda amsa .
Momy ce ta miƙe tayi masa barka da dawowa tare da karɓo wata takarda dake riƙe a hanunsa ,
Diyana da Afreeda ma sannu da dawowa sukayi masa ,
Cikin farinciki ya amsa yace " daughter ansha ƙauye ina kika baro Hajiya ?" Diyana ce tace " ai tana gaishe ka wai sai tazo ,
Madallah dady yace " ai takusa zuwa ma nanda two weeks insha Allah ,
sunkuyar da kai momy tayi dan batada ta cewa a wanan gaɓar haka dai suka dinga hira da dady .
Afreeda ce suka haɗa ido da Diyana tayi mata alamun ta, taso akwai labari da sauri sukayi ciki suka bar momy da dady a palo suma tashin sukayi kowa ya watse akabar palon shi kaɗai .
bayan sunyi sallahr magrib Afreeda ta gyara zama ta dawo kusa da Diyana tace " my sis kinsan me ? nayi sabon saurayi a bikin Hindu da naje shekaran jiya ,
Diyana ce ta dubi Afreeda kana tace " sis karfa ace soyayya zaki fara a ƙarancin shekarunki yanzu fa kina 18 years ne amma kike maganar soyayya .
Ɓata rai Afreeda tayi tace " haba sis mai yasa aduk lokacin da na kawo miki shawara sai kin nemi hanani yin abu ,
Afreeda tafara kuka. gyara zama Diyana tayi ta rungumo Afreeda tace " my little sis ina sonki banison ta sanadiyar soyayya karatunki da brain ɗinki su shiga wani hali , so yanzu dai kibari zuwa tomorrow zamuyi magana karki damu .
Haka dai suka bar zancen sai zuwa gobe amma ran Afreeda ya ɓaci bata bari sistern ta ' ta fahimta ba kasancewarta mace mai fushi sosai.
Kawar da ɓacin ran tayi ta hanyar cewa " sis ya kikayi da zaman village ? naga kin rame sosai kuma kinyi baƙi .
Hmm kedai bari wlh nasha wuya ko a mafarki bana burin sake zuwa wanan ƙauyen sbda wlh ni nasan halin da na shiga ga tsohuwar nan masifa tayi mata yawa , Diyana ce ta kwashe labarin bidirin da tayiwa Hajiya aikuwa suka dinga dariya .
Afreeda ce ta riƙe haɓa tace " sis ashe wanan tsohuwar zata dawo gidannan ? gaskiya tana dawowa mun shiga uku .
"hmm ai bakisan wani abu ba wlh inhar tadawo saita gwammace dan wlh momy zata dinga sawa ido , muma dai ba barinmu zatayi ba aikuwa zata gwammace kiɗa da karatu dan wlh duk dare sai na horata dariya suka sa kana ko wacce taje toilet tayi wanka Afreeda saida ta fita sbda cikinta baya jurar yunwa ,tasami abinda zatasa a bakin ta suna ƙarasa salolinsu kowa ya kwanta .
9am kow yayi sallahr asbha ya koma bacci kasancewar yau weekend sai 11:am suke breakfast ,

Yʻar aikin su na kitchen tana ta haɗa musu abinci ,
Afreeda ce ta fara motsawa brush ta shiga toilet tayi kana ta nufi kitchen dan cikinta baya yimata uzuri ,
Diyana kam anata sharar bacci anji katifa mai laushi lol,
Kʻarfe sha ɗaya kowa ya hallara a palo kan dining momy dady Diyana dakuma Afreeda kowa yai wnka da shiga ta alfarma a jikinsa , bayan sun gaisa ne kowa ya maida hankali ga cin bincinsa saɓanin Diyana da takecin soyayyen dankali da shayi ,
Dady ne ya kalli momy yace " Hajiya fa gobe zata zo Fatima , momy ce tace "Allah yasa muga goben lfiya Alhaji amen dady yace " Diyana da Afreeda suka haɗa ido kowacce ta buɗe baki basu bari dady ya gansu ba kowacce ta maida hankali ga plet ɗin gabanta , suna gamawa dady ya miƙe ya shige ciki binsa momy tayi kasancewar tun jiya ya gaya mata sunada meeting a office .
Diyana ce tace " wlh dady yasa wanan tsohuwar a rai bai san inhar ya kawota aiki zata basa ba hmm , haka dai suka dinga hira wacce duk ta Hajiya ce dakuma abubuwan da zau shirya mata .
gari na wayewa dady ya fara ƙwalawa driver kira da azama ya ƙaraso ya durƙusa gaban dady,
Dady ne yace "inason ka ɗauko Hajiya ne amma karka bari ta kwaso komai iya kayanta kawai,
Angama Alhaji driver yace " kana ya miƙe .
Lokacin da ya ɗauki hanya ƙarfe tara na safe sai dai muyi masa fatan isa lafiya ,
Da isarsa yai sallama Hajiya na girka daddawa gidan ya gurme da wari ya durƙusa ya gaisheta amsawa tayi tana cewa" lalle lale da yʻan binni barka da zuwa ,yawwa driver ya amsa Hajiya .
Wanke hannu tayi tace " to shiga ɗakin man, da shigarshi Hajiya ta miƙo masa kwanon fura da nono aikuwa driver yayi murna sosai dama yana abota da fura da nono ita kuma Hajiya bata rabo dashi , sai da ya cika cikinsa dam sanan ya dubi Hajiya dake zaune hankalinta na kan kalwarta yace " Alhaji ne yace " inzo in taho dake , hajiya ce tace " har satin ya zagayo ne dahar zai turoka , driver ne yace " to yadai ce inzo in tafi dake , jinjina kai Hajiya tayi tace " leƙa ƙwar gida ka kiramin yaro to driver yace " ya miƙe yana fita yayi sa'ar ganin wata yayarinya tana doso gidan ,
ina wuni tace masa 'amsawa dtiver yayi da lafiya lao ,
Nan gidan zaki shiga?
Eh yarinyar tace " okay suka shiga a tare , tun daga tsakar gida Tinene tafara wankawa Hajiya kira ,kaka kizo Talatu ta aikoni wai ki hammata gihiri ,
Hajiya na mita ta fito tana cewa Tinene kiyi maza ki hirya yau binni zamu kwana ki gayawa Talatu ta haɗo miki kayanki ,
Driver dai komawa mota yayi yabarsu a gurin.
Wani uban tsalle Tinene ta doka harda taka rawa tace "hikenan zamu zamo yʻan binni tafara tafiya tana yarfe hannu tasa dariya , takuma canza tafiya wai zatayi kalar tafiyar Diyana .
Hajiya dai tashige gurin shirya kayanta ,
Kamar wacce aka zabura tayi waje da gudu driver dake mota ya hangota dariya yasa yace " yʻan matan ƙauye hhh.
Tinene na isa gida tafara wankawa Talatu kira fitowa tayi tafara yimata faɗa akan wanan kiraye kirayen da takeyi tun daga ƙofar gida , to albishir zan yimiki yau kaka zata binni ,
Da sauri Talatu ta ajiye ledar gyaɗar da take ɓarewa tace " kai dan Allah ?" wlh kuwa to zomu tafi gidan Tinene ce tace " a'a nidai kayana zan tsaya shiryawa Talatu bata jira ta saurari Tinene ba tayi waje , a ƙofar gida ta ƙarasa sa mayafin.
Tana shiga tasami Hajiya a tsakar gida ta fito da buhu , cikin azama ta ƙarasa tace " inna wai yau zaku tafi binni ? gashi kuma kina gani , ina tace tana ciciɓar buhun ,
Talatu ce tace inna yanzu tafiya zakiyi ki barni ?" kuka Hajiya tasa tana cewa " zan dinga zuwa karki damu nima ba ason raina zanyi tafiyar nan yau ba ,ina Tinene tazo ta kawo buhun nata in haɗa da nawa Talatu ce ta share hawayen da suka kwaranyo

mata tace "inna inkika tafi wazai dinga bani wani abin idan na nema , Hajiya ce ta kunce ɗaurin zaninta kana ta ciro kuɗi a lalitarta, sunkai dubu goma ta miƙawa Talatu da keta share idanunta da mayafi ,
Cikin farinciki ta karɓa tana godiya .
Hajiya tasan wuyar da Talatu kesha a gidan mijinta wata rana baya bada kuɗin cefane kokuma yace" ta auni masara ta kai niƙa babu kuɗin girkawa hakan yasa Hajiya take matuƙar tausaya mata amma bata cika nuna mata a fili ba sbda gudun wata rana ,
Hasali ma shine yasa takeson ɗaukar Tinene duk da ta zamo budurwa dan a ƙalla zatayi shekara goma sha huɗu ,
Hajiya nada tabbacin kakar baɗi ubanta zai ce aure zaiyi mata kuma gidansu haɗin zumunci sukeyi .
Hajiya ce ta ƙara kai kallonta ga Talatu tace " inada buhun masara a ɗaki dana wake kuma ga shinkafa nan rabin buhu akwai mangyaɗa , duk ranar da bakida kayan awo ga mukulli nan kizo ki buɗe ,
Wani sabon kukan Talatu ta ƙara fashewa dashi tana tunanin ƙowa ya rasa mahaifiya yayi kuka tabbasmahaifiya itace abin alfahari ga kowane ɗa kuma itace take sanin ɗanta yaci ko bai ciba dazarar taga bai ciba zata fasa cin nata ta miƙa masa ,
haka dai sukayi sallama jikinsu duk a mace Tinene kam murna ta cika zuciyarta burinta taje birni ta waye tadinga kalar tafiyar Diyana dan komai na Diyana birgeta yakeyi .
Hajiya na kulle ƙofar ta miƙawa Talatu mukulli takuma ce mata akwai dambun nama a kwallah ki ɗauka mukan mun fito.
To Inna Allah ya saukeku lafiya cewar Talatu , Hajiya ma dauriya takeyi haka dai akasa abubuwan da takeso suka shiga mota ,
Tinene ta ƙwalawa Talatu kira , tana matsowa tace " Talatu dan Allah ki gayawa Bashiru nayi tafiya , maketa Talatu tayi kana tace " bakida kunya ne kifa kintsu Tinene rayuwar binni ba irin tamu bace ki nitsu ina gaya miki , sallama suka kuma yi motarsu ta tashi zuwa garin shugaban ƙasa wato Abuja ,
Basuyi wata tafiya mai nisa ba dan basu fita a kano ba Hajiya ta tsayar da driver tana cewa" kai baka tsayawa mutane suyi fitsari ne ? ko kuma so kakeyi yarinya tayi a wando ,
Ayi haƙuri Hajiya driver yace yana parking ɗin motarsa a gefen titi fita sukayi tare da wani galan da suka ɗuro ruwa a cikinsa,
Hajiya ma fitsarin tayi suka dawo mota .
Fitarsu Kano keda wuya Tinene ta hango mai gasa masara shirin kuka tahau yi tana cewa Hajiya itafa yunwa takeji ,
Shidai driver badan uwar mai gidanshi ya ɗauko ba babu abinda zai hana baiyi musu magana ba ,
Hajiya ce tace " kai tsaya a siya mata wani abun tasa a bakin salati ,
Driver ne yace " Hajiya nan basu siyar da komai fa , Tinene ce ta karɓe da cewa ga mai masara can wlh ko ita nasamu ai yayan cikina sa barni na huta ,
Hajiya ce ta ciro nera ɗari tace " driver ya siyo musu yan uku hamsin ,
driver yasan babu hakan yasa ya ciro kuɗi a aljihunsa ya miƙawa mai masara dan yasan inhar yakoma bai siyo ba Hajiya zata iya tsigaleshi , yana miƙa musu ,ya tada mota .
Sunyi tafiya mai nisa sbda sun wuce garuruwa da dama , jin motar tayi shiru yasa shi leƙa wa ta mudubi , hamdallah driver yayi ganin mai damun mutane tayi bacci , cikin ikon Allah sai gasu a Abuja har sunkusa layin su , Hajiya ba taɓa zuwa tayi ba shiyasa tayi gum da bakinta ,
Horn ya shiga yi , mai gadi ne ya wangale get ɗin yana ɗaga musu hannu ,
Hajiya ƙarewa gidan kallo takeyi badan ta ɗan yarda da drivern nan ba da zata iya cewa gidan yan yankan kai ya kawota amma bari ta zuba masa ido tagani ,
Yana parking ya fito tare da buɗewa su Hajiya ,

Tinene tayi bacci Hajiya ce ta ɗaka mata duka a razane ta tashi takalli Hajiya sanan ta kalli ina suke , mutsuke ido tayi tace " alkur'ani da gaske ne nayi mafarkin gani a wata sabuwar duniyar Hajiya ce ta sharara mata mari kana tace " zaki fito ko zaki zauna ni gaba zanyi dan inama tunanin kamar ba gidan Alhajin ya kawomu ba sbda babu ko wulƙawar mutane sai tsintsaye , Tinene ce ta fito tana shafa kumatunta ,
Ta nufi gurin mai gadi , gaishe sa tayi kana tace " muna neman masu gidannan , mai gadi ne yace "ciki zaku shiga bazasu jiku daga nan ba amma kuzo muje ,
Sai da ya kaisu har bakin wata ƙofa mai glass kana ya ƙwanƙwasa ,
Da sauri ta fito jikinta sanye da kayan bacci da alamu bugun ƙofar ne ya tasheta ,
Tsawa ta dakawa mai gadi kana tace " waye ya baka izinin shigowa nan ?" durƙusawa yayi har ƙasa yana bawa Diyana haƙuri saboda kaf cikin ma'aikatan gidan tsoronta sukeji sosai ,
Kasancewarta mace mai wani irin hali wato ƙasai ta bugu da ƙari kwarjini , Hjiya ce tayi saurin leƙowa tana cewa " waye yake mgna Diyana da bata gane ko wacece ke magana ba kasancewar Hajiya na can baya mai gadi kuma yana kusa da ƙofar ,Tinenuwa kumatanacan gurin tsintsaye tana kallonsu ,
Diyana tace " nice nan Diyana ,
Ai da sauri Hajiya ta matso tana cewa kauce kibani guri iyayi yayi muku yawa ,in mutum zai shigo har sai an tambaya ,
tunda Diyana ta tabbatar Hajiya ce ta iso tayi shiru kamar ruwa ya cinyeta Allah ne kaɗai yasan irin abinda zuciyarta ke shirya mata,
Kutsawa Hajiya tayi tana tana sana'ar tata wato mita , shikam mai gadi ya wuce tuni . juyawar da Tinene zatayi taga babu Hajiya ai da gudu ta ƙara taje ta tura ƙofar ta shige ,
Samun su Hajiya da momy da Diyana da Afreeda tayi suna zaune a kujera anata gaisawa , samun guri tayi itama ta zauna tare da cewa " ina wuninku , lpy momy da Afreeda sukace banda Diyana daketa yamutsa fuska , Hajiya kam anbaje akan kujera anata zubawa momy labari , Tinene ce ta kalli Diyana ta nunata da yatsa tace " kaka wanan ce tazo gidanmu hekaran jiya ko ?" eh Hajiya tace " ai wanan da kike gani bansan gadon waye tayo ba , sam batason mutane .
Momy ce tayi dariya kana tace " ai wlh Hajiya nima ina tunanin hali irinna Diyana amma inaga halitta ce kawai ,
Hajiya ce ta gyara zama tace" inason Alhaji yazo muje gurin wani babban malami ƙila tanada matsalar aljanu dan naga kamar ba ita kaɗai bace ,
Tuntsirewa da dariya Afreeda tayi tana kallon bakin Hajiya sai kai lomar shinkafa takeyi ita da Tinene ,
Kuma kai wata lomar Hajiya tayi tace " tun lokacin da tazo gurina naga take taken hakan , momy ce tac" to Allah yabasu haƙuri , amen suka amsa banda Diyana da haushi ya cikata ,
Cikin ranta tace wato wanan tsohuwar tun yanzu zata fara ɓatamin rai ko ?" to wlh mu zuba zata gane batada wayo ta miƙe tayi bedroom ɗinsu, da yamma bayan la'asar kowa ya shige ɗaki Hajiya da Alhaji ne a zaune sai Tinene dake ƙasa a gefe tana kallo a tv hango wani mutum tayi yana kuka da alamu wani abinne ya sameshi a shirin film ɗin ai itama tahau share hawaye tana cewa" Allah sarki hankalinsu Hajiya bai kai gurinba sai da taji anja mata ƙafa tayi ƙasa ,wani wawan ihu Hajiya tasa tana riƙe da gurin ,Tinene da tayi abun hankalin na gurin tv tana kuma kaiwa Alhaji shirin naushi ,
Kaucewa Alhaji yayi yana tunanin anya wanan yarinyar mai lafiya ce kuwa ?.
Sannu Hajiya dady yace " yana kallon ƙafarta ,
Fitowar momy da Diyana da Afreeda ne yasa dady cewa zoki ɗaga Hajiya da azama momy ta ƙaraso tana cewa mai ya sami Hajiya ? abinda ya faru dady ya gayawa momy , ji sukayi an kwashe da dariya ,juyawa sukayi dukkansu harda mai kallo , ba kowa bace sai Diyana da ta riƙe ciki tana dariya , dady ne ya ɓata rai kana yace " ke Diyana kinci gidanku dan bakida kunya Hajiyar ce abin yiwa dariya kina gani tana fama da ƙafa wanan sakaran takuma jibga mata naushi ,

Da gudu Diyana tayi ɗaki saboda wata sabuwar dariyar ce takuma kawo mata ziyara, riƙe haɓa Hajiya tayi tace "Faɗimatu kingani ko kinga abin da nake gaya miki ko ?" to Alhaji tun wuri kayiwa tufka hanci tun kafin suyi mata illa ,
dady da bai fahimci abinda Hajiya take cewa ba yafara tambayar mai ya faru ,mayar masa Hajiya tayi kana ta ƙara da cewa " a gaggauta wlh .
Itadai momy batada bakin magana sai eh da eh , dady ne yafara yiwa Tinene faɗa yake gaya mata mutanen tv ba fitowa sukeyi ba kuma basujin mutane , shiru tayi kai kace ba ita ta aikata ba ,
Miƙewa Afreeda tayi ta nufi bedroom ɗinsu tinda comedy ya ƙare , da dare yayi bayan isha'i mai aiki ta jera musu abinci a dining , Hajiya tunda taga anan za'aci abinci tace " bata yarda ba a kawo mata nata ƙasa , babu mai yimata musu kaf ɗinsu momy ta sauko mata dashi akan faranti ,
Diyana bata fito cin abinci ba sai Afreeda da ta zuba farfesun kifi tana ci ,
ina daughter ?"dady ya tambayi Afreeda ,
Afreeda ce tace " tana bedroom tunda tayi sallah ta kwanta ,
Buɗar bakin Hajiya tace " ba dole kaga mutum kamar muciya ba babu auki saboda baici abincin gidansu ya ƙohi ba,
Kai lomar tuwon shinkafa tayi tana mita ,
Tinene dake zaune da shinkafa da miyar kifi a gabanta tace " Allah sarki Talatu ko taci hinkafar da kika barmata oho ,
Hajiya ce ta dubi Tinene tace " maza kiyi kici kije ki kwanta , Faɗimatu ki nuna mata ɗaki karta cika mutane da surutu ,
Miƙewa dady yayi ya yiwa su Hajiya sallama ya shige ciki .
Washe gari takama laraba Diyana da Afreeda zasuje bikin wata classmate ɗinsu ko wacce burinta tayi kwaliya ta kece raini kasancewar yarinyar wani babban ma'aikaci ne amma bai kai dadynsu Diyana kuɗi ba,
Kar mai karatu ya ɗauka shima mahaifin amaryar talaka ne , no yanada kuɗi sosai kuma babu wanda bashida labarin mahaifin amaryar harnyanzu ana damawa dashi ,
Sai dai shi mahaifinsu Diyana wani attajiri ne wanda ko shi bai san iya adadin dukiyarsa ba , kasancewar sa mai kuɗish sosai ,
Kayane anko suka ɗinka kala uku uku kowane ɗaya zaiyi 50k ɗinki kuwa anyi masa na 5k atamfa da less da material babu na kushewa a cikinsu ,
Yau akeyi ɗaurin aure , in suka tafi yau sai gobe zasu dawo .
Diyana ce ta kalli Afreeda tace " sis yanzu mai zamu kaiwa amarya a matsayin tamu gudun mawar kinsan dai in muka bata kuɗi ba karɓa zatayi ba ,
Afreeda na saka skirt da ƙyar tace " sis yanzu dai gurin momy zamu dan wlh nima kaina yayi zafi burina inganni a gurin bikinnan ,
ƙarfe huɗu duk sun gama shiri Maltina Diyana ta ɗauko a fridge kaɗan tasha ta riƙe ragowar a hanunta suka nufi bedroom ɗin momy .
Samunta sukayi tana sa kaya ,zama Diyana tayi a bakin gado ita kuma Afreeda ta zauna a kan stool dake gaban mirror ,
Kallonsu momy tayi da fara'a tace " harkun shirya ne ?" eh suka ce Diyana ce ta shagwaɓe fuska tace " mom munrasa abinda zamu kaiwa Khairat a matsayin namu kyautar , riƙe baki momy tayi kana tace "karku damu ga wani haɗin humra da turaren wuta da nasa aka yimin haɗinsa tun daga maiduguri so ku tafi dashi kawai duka inyaso zanyiwa Hajiya Falmata magana ta ajiye min in tanada ragowa , rungume momy sukayi suna godiya ,
Afreeda ce tace " momy bakice munyi kyau ba , dariya momy tasa tace " ai wanan kwaliyar taku ko maƙiyi ,
sukasa dariya dukkansu lokacin da suka kammala shiri ƙarfe biyar na yamma , sunyi kyau kamar ka sacesu ka gudu Diyana ce ta ɗora baƙin glass ɗinta a ido kasancewar ta ma'abociyar son sakashi amma Afreeda bata damu da sanyawa ba,
yɑar aiki suka aika kiran driver , sai gasu sun dawo a tare Diyana ce tace " driver sabuwar mota zaka fito da ita , kafin ta ƙarasa magana driver yace " to Hajiya angama insha Allah , fitowar momy taci karo dasu sai ga Hajiya nan ta ɓullo tana

ɗingishi , wayar Diyana ce ta fara ring ko kallon Hajiya bata yi ba ta ɗaga wayar , Khairat ce take magana kamar zatayi kuka ,
Haba sis kufa ake jira a gurin reception ɗinnan pls kuyi sauri , Hajiya ce ta gyara tsayuwarta tace "yau naga duniya yara su koma kamar zabiyoyi jibeku ko kyau bakuyi ba ,
Afreeda da hankalinta yayi gurin shagali tace " bye momy Hajiya bye tana ɗaga musu hannu , ganin cikinsu babu wacce ta kulata yasata cewa " ke zabiya zoki tafi da Auta itama taga gari ,
Ai da gudu suka fice,
Suka shige mota sai gurin biki , sunyi tafiya mai nisa kana suka iso ƙawataccen gurin da idan ka ganshi sai ka rantse a ƙasar waje ne , iya tsaruwa gurin yayi, suna sauka a mota na hango wata budurwa batada jiki tana sanye da doguwar riga fara ta yafa mayafin rigar a kanta ,
da gudu tayo gutinsu Diyana tana faɗin barkan ku sists wato munce bamuson let sai da kukayi ko ? ga anty Khairat can taƙi sakin jiki wai dan babu anty Diyana , lumshe ido Diyana tayi kana tace "am sorry amaryar mu tayi haƙuri ganinan na ƙaraso ,
Afreeda ce taja budurwar mai suna Siyama sukayi gefe ita kuma Diyana ta shige ciki ,
Da shigarta kallo ya dawo kanta kowane saurayi mai ji da kansa ita yake kallo hatt MC ma ita yake kallo ,

Gashi dai kayane da kowa na gurin yasan tsadarsa da kyansa kuma ba wata fayattaciyar makeup tayi ba amma hakan bai sa sundena kallonta ba ,
Cikin sauri tayi hanyar da zata sadata da gurin zaman amarya,
Tun daga nesa Khairat tafara fara'a da dariya ɗauke a fuskarta , Diyana ma maida mata da dariyar takeyi tana tafiya ,
Batasan da mutum a gabanta ba ta bigeshi wayarta ta faɗi ƙasa ta watse gefe ,
A, zuciye ta ɗago kai ta waysawa wanda ta bige harara kana ta ƙara masa da mari ,
Baice komai ba sai shafa gurin da yayi kafin kace me hankalin kowa ya dawo gurinsu bodyguard ne guda uku suka yi kana da shirin duka ,
Matashin saurayin ya dakatar dasu yana huci .
Durƙusawa Diyana tayi ta cire sim ɗinta tabar wayar a gurin , ta ƙarasa gurinsu Khairat da taketa zubda hawaye tana kallon Diyana , zama Diyana tayi takai dubanta ga Khairat da idanunta sun fara ja tsabar kuka ,
"afuwan amaryar mu cewar Diyana , Kamill wato ango da yanzu ya dawo gurin zamansa , kasancewar yaje bawa babban amininsa haƙuri ya dubi Diyana ,
yace "amma Diyana kinyi ganganci maiya kaiki kula wanan bawan Allahan?",
Lumshe ido Diyana tayi tace " Kamill sanin kanka ne bana ɗaukar raini shiɗin waye waye babansa ? shiii!!!, Kamill yace " karki ƙara magana ,
Yʼan matan dake gefe sai kallon Diyana sukeyi masu gulma nayi kowa yana ganin Diyana batada tarbiya wasu kuma daga can gefe , suna cewa ai gara da tayi masa haka ,
Maganin mutumin da bai ɗauki ɗan adan da daraja ba kenan ,
Shigowar Afreeda kenan taga anata nuna Diyana , kai dubanta tayi gurin da Diyana take zaune ,
ganin fuskarta babu walwalah yasata ƙarasawa da sauri ,
Ruƙo hanun Diyana tayi tace " my sis maiya faru ?" kiyi haƙuri kinga na daɗe ko ?" munje duba wata abaya ne da za'ayi yayi wanan sallahar ,
lumshe ido Diyana tayi kana takuma buɗesu tace " karki damu sis damuwata da ban kizo ki zauna ,
Khairat itama jikinta duk yayi sanyi , haka dai aka kira abokan ango da ƙawayen Amarya , farko sunan Diyana aka fara kira na biyu kuma babban aminin ango wato Kamill , sai da gaban Diyana ya faɗi , komawa gurin Kairat tayi ta raɗa mata a kunne cewar sis bazan iya rawa da wancan banzan ba.....!
Sa sauta murya Khairat tayi kana tace " pls kiyi haƙuri kije na lokaci ɗaya nefa ,
Badan Diyana taso ba ta wuce ta nufi gurin da aka tanadar musu na rawa ,

Mc ne yasa mutanen gurin tafa musu , ya fara kwararo musu yabo , kaga matashin saurayi mai ji da kansa yɑn mata ma wawarka sukeyi , kai ku tafawa Alhaji Kamill ɗa ɗaya tilo a gurin mahaifinsa wato Alhaji Safiyan gidan kuɗi .
A zabure Diyana ta ɗago kai takai dubanta ga Kamill da shi hankalinsa ma ba a gurinta yake ba ta kawar da kai ,
innalilahi ragowar ta maƙale mata ma maƙoshi , tasani ubansa ba sa'an ubanta bane yafi ubanta dukiya hatta mahaifinta yana girmama Alhaji Safiyan kuma yafi mahaifinta suna kasancewar sunansa ya zaga ƙasashe da dama harda na ƙetare ,
Duk da shima ubanta sunanshi ya shahara amma ko kwatan na uban Kamill bai yi ba ,
Jiyo maganar Mc tayi yana cewa " an gaisheki babbar ƙawa aminiya kyakyawa kuma kuma fasihiya a fanin iya kwaliya kai kubata tafi , kowa yakama raf raf hankalin mutanen duk ya dawo gurinsu ,
mc ne ya bada umarni aka sanya waƙar da akayi ta biki , Kamill rawa yakeyi tsakaninsa da Allah matsowa kusa da Diyana yayi yace " yɑn mata ki taka man karki bada manyan mata har video akeyi fa , wanan sunkuyowar da Kamill yayi yana yiwa Diyana magana wasu abokan Kamill suka fara ɗaukarsu hoto aikuwa sun bada kala ,
Ɗan takawa tafara a hankali jikinta a sanyaye amma tanajin inhar Kamill ya kuma ɓata mata rai babu abinda zai hanata ci masa mutunci koda komai zai faru ,
tsayar da kiɗan akayi mc yace suje su huta , ran Diyana ya ɓacci sosai musamman da zasu sauko Kamill yakuma sunkuyawa yayi mata magana .
Khairat ce ta janyo Diyana tace " nagode sis nasaki abinda bakiso ko am sorry , rufe mata baki Diyana tayi da cewa " a'a sis karki damu wancan banzan ne ya ɓatamin rai badan haka ba da komai zai tafi normal,
ƙarfe 8pm an tashi anyi su yanka cake da hotuna, Afreeda ce ta kamo hanun Diyana tana cewa sis momy na kira wai mudawo gida okay Diyana tace ".
Bayan sun bawa ƙanwar Khairat abinda zasu bata sukayi sallama , kasancewar Afreeda ta kira driver yazo ya ɗaukesu , suna fitowa sukaci karo da Kamill yana waya yana murmishi , tsaki Diyana taja kana ta janyo Afreeda sukayi mota , wani killer smile Kamill yayi ya zura hannayensa cikin aljihun shaddarsa , ganin motarsu na shirin tashi ya koma gefe ya tsaya tare da ciro wayarsa , numbar bodyguard naga ya dannawa kira ko 3 mins ba 'ayi ba sai gasu nan sun taho sun tsa tsaya a gabansa tare da sunkuyar da kai ,
sukace barka prince yawancin abokansa da sunan suke kiransa amma ba kowa yasan da wanan sunan ba ,saboda wasu dalilai , haɗe rai yayi yace " kunga waccan motar maza kubita karku bari su gane okay sukace , cikin hanzari suka shige mota ,
Sukabi motar da yanzu ta fice daga harabar gurin.
Tafiya drivern nasu yakeyi cikin ƙwarewa ba kowa zai san yanabin wata mota ba kasancewar ko kwana motarsu Diyana batayi ba .
Tunda Diyana ta shiga mota tafara tuno abinda ya haɗasu da kamill a zahiri itama tanada laifi amma sam batason raini hakan yasata yimasa rashin mutunci ,sai huro hanci takeyi .
Afreeda ta lura da yanayin sis ɗin nata amma bata kulata ba kasancewar tasan halinta inta fiya shiga harkarta a time ɗin da take cikin baƙin ciki sukan iya ɓatawa su kuwana ma basu shirya ba ,
A haka suka isa gida babu mai cewa komai ,
Bata jira driver yazo ya buɗe motar ba ta fice zuciyarta nayi mata ƙuna ,
ko sallama batayi ba ta shiga palon ganin Hajiya da Tinene a palo yasata yamutsa fuska ta wuce bedroom ɗinta ,
Hajiya dake zaune ta riƙe haɓa tana jinjina lamari irin na Diyana ,
A fili tace " nikam wanan wace irin yarinya ce batasan darajar mutane ba , Tinene dake zaune gefen Hajiya tace Hajiya sufa yɑn binni basu damu da sallama ba ,
Hajiya ce ta ranƙwasheta kana tace " badai duka ba ita wanan mai zuciya kamar faɗa wuta bansan gadon wa tayo ba,
Sallamar Afreeda ce ta katse musu zance suka amsa tace " sannu Hajiya ,

Washe baki Hajiya tayi kana tace " ywwa yʻar albarka kun dawo lafiya ?" lafiya Afreeda tace" ta wuce ciki .
Kai tsaye bedroom ɗin momy ta wuce , da sallama ta shiga ta gaida momy , kun dawo sai yanzu ko ? momy ta jerowa Afreeda tambayoyi , am sorry mom wlh matsala aka samu amma yanzu komai yai normal ,
Momy dake kallon fuskar Afreeda tana nazrin ta tace " ina Diyana ?" tana bedroom , Kiramin ita,
Tom Afreeda tace " Afreeda na fita momy tashiga tunani tasan duk lokacin da ran Diyana ya ɓaci bata wai wayar kowa har ita ma to yau kuma maiya faru ?" batada mai bata amsa yasata zama gefen gado tana jiran shigowar Diyana ,
A' ɗakin Diyana Hajiya ce tsaye a bakin ƙofa tana balbale Diyana da masifa akan rashin ladabi , kuka Diyana tasa mai sauti dan a halin yanzu babu abinda zatayi zuciyarta tayi mata daɗi sama da kuka ,
Tafa hannu Hajiya tafara tana salati tace " to sharri zakiyimin ? shigowar Afreeda ne yasa Hajiya yin shiru ta juya bata ƙara magana ba .
Dafata Afreeda tayi kana tace " my sis momy na kira pls ki share hawayennan karki ɗaga mata hankali ,
To kona share hawaye mezan ce mata banison tasan irin target ɗin da na shiryawa wancan jakin dan wlh tunda yasani zubar da hawaye nima sai na wulaƙantashi , Afreeda ce tace " sis wai kina nufin Kamill ?" eh Diyana tace tana girgiza kai alamar tabatarwa ,
Wani marayan nunfashi Afreeda ta sauke kana tace " sis ki janye wanan maganar bazaki iya da Kamill ba mahaifinsa yafi dady komai hasali ma dady zai iya zama ɗan aikensa.....! wani mahaukacin mari Diyana ta sakarwa Afreeda tare da nuna mata hanyar waje,
why zaki ƙara ɓatamin rai kinada hankali kuwa ?" Afreeda ficewa tayi tana kuka a ranta kuwa cewa " tayi da badan tunda suka taso bata taɓa yiwa Diyana rashin kunya ba ,
Da yau sai sunyi dambe ,
ficewarta shine mafita,
Fitowa tayi daga sashin ta rufo door ɗin , mai gadi na hangota yafara miƙo gaisuwa dan jininsu ya haɗu da Afreeda kasancewarta batada wulaƙanci ,
Yanata gaisheta amma ko saurarar shi batayi ba , bai damu ba yasan hakan tana faruwa in tana cikin fushi bata cika magana ba ,
Gurin furannin gidan ta nufa tanata tsinkarsu tana jefarwa , miƙewa tayi ta dawo cikin gida ,
Samun momy da yʻar aiki tayi sunaya jera abinci a dining saita nutsuwarta tayi , kana tace " sannu da aiki momy, murmishi momy tayi kana tace " to ayi magrib azo aci abinci food is ready ,
sunkuyar da kai Afreed tayi tace " okay momy ta shige ciki , jinjina kai momy tayi dan taji faɗansu na ɗazu amma ba komai nasu take shiga ba tunda daga sunyi faɗan suke shiryawa kamar ba suba ,
Kai tsaye Bedroom ɗinsu Afreeda ta wuce ,
Samun Diyana tana sallah yasata shiga toilet tayi alwalar itama ta ɗauki sallaya tafara sallah , bayan sun idar dukansu,
Diyana ta rungume Afreeda tace " am sorry my sis kiyimin afuwa karkiyi fushi da sistanki tana buƙatar taimakonki ,
Sauke ajiyar zuciya Afreeda tayi tace " karki damu komai ya wuce momy na kiranmun,
Afreeda tayi hanyar waje zata fita Diyana ta riƙo mata hannu , haɗe hanuwanta Diyana tayialamun neman alfarma tace " my sis pls karki sanarwa momy abinda ke fariwa kinsanta da saka abu a ranta,oky dont worry i promise bazan faɗa ba zomuje kici abinci yau abinda kikeso ne akayi,
Menene shi?" Diyana ta tambayi Afreeda, plantain and egg Afreeda tabata amsa da sauri suka nufi dining kowacce fuskrta a sake,

Sannu momy ,
Ywwa daughters harkun fito ?".
Eh momy .
Hajiya dake gefe a zaune a kan kafet itada Tinene tace " to sabon salo uwar waye bazaku cewa hannu ba , yara sai kinibi bin tsiya to ba mutuwa zanyi ba , Tinene dake gyara zani tace " kaka wanan abin yayi daɗi aɗan ƙaramin asamin kabejin da yawa , momy ce ta ƙwalawa Nana yar aikinsu kira tace " ta daɗowa Tinene kabej kasancewar Hajiya ce tace " dole ayi mata kwaɗon kabeji da ƙuli kuli ,
Aikuwa basuci abincin kirki ba sai kabeji ,
Afreeda ce ta ƙunshe dariya yanda taga Hajiya na kwasar kabeji to Allah ya kyauta .
Suna gama ci momy tace " in akayi isha'i tanason ganinsu , Hajiya ta miƙe tana dogara ƙafa ta nufi ɗakinsu ,
Sanda Tinene tayi fam da kabeji sanan itama tabi bayan Hajiya ,dan bataga alamar gidan suna wasa da yara ba shiyasa takejin tsoronsu ,
Bayan isha'i Diyana da Afreeda suka shigo ɗakin momy kowacce na jiran taji metayi , dubansu momy tayi kana tace " gaskiya kuna shirin bani kunya ,
Kunga tsohuwar nan duk ranat da ta haɗaku da dadynku wlh zakuji babu daɗi tunda yana amfani da duk abinda ta gaya masa to wlh ku kiyaye ,
Kuma batun gaisuwa kowacce daga cikinku tadinga zuwa da safe tana gaisheta Afreeda banida matsala dake amma Diyana yakamata ki rage abubuwan da kikeyi ke mace ce fa gidan wani zaki,
Haƙuri suka shiga bawa momy da alƙawarin bazasu sake ba lol nidai nasan gimbiya da kamar wuya wai gurguwa da auran nesa ,
Allah yayi muku albarka kuje saida safe , miƙewa sukayi kowacce da abinda take saƙawa a ranta .
Tunda suka shiga ɗaki , Diyana taketa ƙwafa tana tsaki zama tayi a gaban dress mirror kan wata ƙujera mai kyau ta dubi Afreeda tace " wanan tsohuwar tafara kaini maƙura, cikin sauri Afreeda ta ƙarɓi zance tare da cewa wlh kamar kin shiga zuciyata dan dazarar dady ya dawo zata iya haddasa mana fitina,
Diyana ce tace " zokiji , banji mai sukace ba naga sunyi dariya harda tafawa ,
Dare yayi sosai kowa na gidan yayi bacci bakajin ƙarar komai sai na AC da fridge ,
Diyana ce ta farka dan har bacci ya ɗaukesu tashin Afreeda tayi suka farashirin abinda yakamata suyi , wani jan ƙyale Diyana ta ɗauko kana tace " Afreeda ta ɗauko mata teddy , tana ɗaukowa suka fara kiciniyar sanyawa teddy janbaki da jan ƙyale , kana suka ɗauko wata hoton fuska , wace suke sawa in zasuyi wasa a school lokacin suna secondary ,
Nice zansa wanan kekuma ki ɗauki farin hijab ɗinnan kisa ki riƙe teddy ki tabbatar da kin rufe fuskarki.....!.

Afreeda ta sanya farin hijab wanda ya rufe mata fuska ko ina kasancewarsa kamar mai niƙaf , ta ɗauki teddy ta rungume .
Sanya fuskar Diyana tayi ta kalli kanta a mirorr ta kwashe da dariya tana cewa yau zamu birkito musu kabej lol.
Fita daga ɗakin nasu sukayi suka nufi ɗakin da aka bawa Hajiya ,
A buɗe ƙofar take hakan yasa basu sha wuya ba suka kutsa kai ciki ,
Hajiya na kwance ansami katifa mai laushi sai gwarti take kwasa,
Tinene na gefenta itama bacci takeyi yau na gangarowa ,
Afreeda ce ta shafa fuskar Hajiya tana cewa munzo ne muji dalili ,
Buɗe idon da Hajiya zatayi ai taga kammanni kamar na aljanu ta tashi ta zauna dama ɗakin ba wani hasken kirki sbda tunda suka shigo Diyana ta rage Hasken ,
mai kuma yau nayi muku bayin Allah ?"
Maƙale murya sukayi dukkansu sukace , wayace kizo birni ?" bakisan mun maida ɗakin ki na ƙauye turakar babanmu ba ?" a razane Hajiya ta runtse ido tana shirin kurma ihu ,

rufe mata baki sukayi da hanunsu dake sanye da hand globe , kikayi ihu zakisha mamaki zamu tafi da jikarki , Tinene da tun ɗazu ta tashi taƙi ɗago kai dan itama Allah ya zuba mata tsoro, Hajiya duk jikinta rawa yakeyi kasancewarta matsoraciya ba ta wasa ba , haɗe fuskarsu Diyana tayi tanata zaro ido cikin fuskar nan jin fitsari yana ɗiga ta gefe yasa Diyana cewa , shine aka jiƙa mana yayanmu to tun wuri ki kwashe shi kokuma yanzu mu tafi dake ƙasarmu , Hajiya na kuka tana tsane fitsari da zaninta sbda akwai sikel ɗin ciki a jikinta , tagumi ta zuba tana magana , duk inda naje sai kun biyoni?" a 'garin namu ma baku barni ba ,haka anan ma bazaku barni ba ?" .
Hajiya tasa kuka tace " wlh kakanmu ya cucemu da yabar mana gadon aljanu wayoo mun higa uku , nanfa Diyana da Afreeda suka fara kwasar rawa suna takawa kai kace aljanun gaske ,
Jiyo tari sukayi ta gefen Tinene , Afreeda ce ta ƙarasa gurin tace " idan baki tashi ba saimun maidaki akuya , ai da gudu ta miƙe jiki na rawa kan kace me ji kake ɓirrr tana shirin sake musu kashi ,
Waro ido Diyana tayi tace " kifito kizo yanzu birnin mu zamu kaiku ,
Cikin azama Hajiya ta sakko ta durƙusa gaban Afreeda kasancewar tafijin tsoron teddyn hanunta , tace " kuyi haƙuri yarinya ce batasan komai ba kuyi mata aikin gafara dan Allah , nasanku kunfimu haƙuri to ku ƙara , Afreeda ce ta kece da dariya marar sauti sosai ta dubi Hajiya da ta jiƙe da zufa dakuma hawaye , jitayi tausayinta ya shigeta ta dubi Diyana tafara yimata wani irin yare , gani nayi Diyana ta girgiza kai alamar a'a .
Matsowa Diyana tayi tace " nan ɗakin na uban ubanmu ne yatafi misira kuma yabamu ajiyarsa to kufice kokuwa musa a ɗagaku sama ,
Tinene da taƙi fitowa daga bayi , Afreeda ta ƙwanƙwasa ƙofar tace " kigama muna jiranki, ku bakwa ganin mutane a gefenku a kwance zaku shigo mana ɗaki koku bar wanan ɗakin ko gidan gaba ɗaya kokuma mu ɓatar daku daga duniyar .....! kafin su ƙarasa magana Hajiya ta buɗe bayi ta janyo Tinene dake tsaye babu ko wando kasancewar in zatayi kashi saita cire wando , suka nufi palo babu ko magana,
Tafawa sukayi Afreeda tace " zamu gudu , raɓawa sukayi ta gefe suka wuce batare da kowa ya gansu ba , dama momy na can sama sukuma suna ƙasa ,
Suna shiga bedroom ɗinsu suka fara tsalle sunata dariya ,
Duba wayarta Diyana tayi lokacin ƙarfe biyu da rabi na dare, kowacce ta nemi gurin kwanciya asuba ta gari.
Washe gari da safe kowa na gidan na bacci kasancewar weekend ne sai shaɗaya 11am suke breakfast,
Tun shida Hajiya ta tashi taje ɗakin Nana mai aiki ta tasota ,
Sata ɗora ruwa tayi da abinci , babu shiri tafara kiciniyar abinda Hajiya ta sakata ,
Da farko dai ruwan wanka aka miƙowa Hajiya cikin sauri ta karɓa tana sakawa Nana albarka , tashin Tinene tayi tazo tayi wanka yau a garinsu zasu kwana , Tinene dake bacci mai daɗi cikin bacci , tace "Kaka ni kibarni nayi bacci kina ganin jiya gudawa tasani gaba , tsabar haushi da ya cika Hajiya tace " uban gudawa , dan uwaki ni zaki gayawa kinyi gudawa to tun wuri kitashi muje kiyi wanka , dan yau sai Shafa ƙauyenmu , a zabure Tinene ta miƙe ta riƙe ƙugu tace " wlh babu inda zani ,
Kaji kaka dai da wani zance , muna hyan hyayi da burodi kice mutafi to yasin ko dafani akeyi nan naga gurin zaman dan haka kima canza tunani ,
Riƙe baki Hajiya tayi tana tunanin kodai Tinene ta mance halin da suka shiga jiya take batun zama, to bara inje inyi wankan in fito wlh saikin bini bazakisa ubanki ya tambayeni ina kikaje ba ,
Wucewa Hajiya tayi ta nufi ɗakinsu da ya zame mata abin tsoro tashiga da adu'a tana cewa " wa innahu sulaimanu wa innahu bismillahir rahmanir rahim, tashige ta surka ruwan ,
Bayan tayi wanka ta fito ta , tattara kayanta a buhu ta shafa manta da farin kwali ta sanya kaya ta fito palo.

Baccin kuwa ta koma hankali kwance da mamaki inna ta hamɓareta tace " wlh kitahi kokuwa insa masu gadi su ɗaukeki , da sauri ta tashi tayi ɗakinsu , tana shiga aljanun jiya suka faɗo mata ihu tafara kurmawa tana ƙarawa , a na biyun ne ya tashi mutanen gidan dukansu da sauri momy ta fito tana tambayar lpy kuwa? Hajiya da yanzu take shirin shiga ɗakin dan tsoro ya hanata tace " leƙa kigani faɗimatu ko aljanu ne , aljanu kuma ? momy ta mai maita ,
Eh leƙata , Hajiya ta kasa taɓuka komai sai cewa leƙata, shiga momy tayi ta leƙa bedroom ɗin ganin tinene na wanka tana tsala ihu yasa momy shiga tafara tambayar anya lpy kuwa Tinene ? , nan ma hankalin Hajiya yakuma tashi taƙara tattaro kaya tana cewa wlh aljanu sun samu a gaba a gidannan , inna zuwa ƙauyenmu bazan sauka ko ina ba sai gidan malam fari ,dan wlh dole ya yimin istahara akan aljanun gidan Alhaji ,
Duk da nima na gidana basu barni ba dole naɗau mataki , momy dai jin hajiya takeyi dan ba abokiyar yinta bane ,
Amma su da basu taɓa jin hayaniyar komai ba amma ace wai gidansu da aljanu , kodai rikicin tsufanne ya motsa , to Allah ya daɗa karewa momy tace " ta fice , Diyan da Afreeda suna zaune a palo kowacce ranta fess Hajiya zatabar gida , amma basu nuna a fuskarsu ba ,
Ganinsu a palo yasa momy cewa " ku bakusan abinda ke faruwa bane ?" yamutsa fuska Diyana tayi tace " good morning momy , bata amsa ba sai ƙara jero musu tambayar taƙarayi ,
langwaɓar da kai Afreeda tayi kana tace " momy munji ihu ne mafa ya tashemu wlh "mai ya faru ne , kuje ku tambayi Hajiya , daganan momy tayi gaba ,
suna ganin momy ta wuce suka tafa suka miƙe kowacce ta koma gado ,
Ɓangaren Hajiya tagama shiri tsaf Tinene take jira , itama Tinenen tunda Hajiya tace mata inhar bata zo sun tafi ba to babu ruwanta ,
Ko ta mance da takarar da aljanun jiya sukayi na cewa zasu ɓatar damu , aikwa babu shiri Tinene jiki na tsuma tace " zan biki yasin bazan zauna ba ,
Amma fa zamuyi kewar ruwan hyayi mai madara ,
Ke dalla can marar tunani lafiyar mu tafi hyayi dan haka mutafi kawai , basa bibiyar yɑn gidan sai baƙi to dole na nemowa Alhaji magani wataran mutan gidan zasu nema ,
Nafito ina zaure kisameni a can , Tinene dake ɗaura zani tace " ganinan .

Kamill ne zaune a wata ƙayatacciyar kujera ita kanta kujerar abin kallo ce bare wanda ya zauna akan kujerar , dogo ne fari ,
yanada manyan idanu inka ganshi kamar balarabe ,
Gashin kannan nasa luf luf kamar wanda ake shafashi ga baƙin sajen da ya ɗan kewaye bakinsa yana ɗauke da pink lips ,
Yanayin jikinsa kaɗai ya ishi mai kallonsa yasan cewar kuɗi yazauna bai taɓa neman abu ya rasa ba ,
idan kuɗi yakasa samar masa yakan sa basira ,
Idan basira ma bata samo masa ba yakansa ƙarfinsa domin ya mallaki abinda zuciyarsa takeso ,
iyayensa suna zaune a kano unguwa uku , gidansu ya fita daban da shauran gine gine amma shi ba mazauni bane, haka mahaifinsa Alhaji Safiyan gidan kuɗi baya rayuwa a Nigeria , kasancewar sa hamshaƙi , bare uban gayya wato Kamill .
Ɗai ɗai garin da bai mallaki gida ba saboda hutawa aure baya gabansa hakan yasa iyayensa zuba masa ido yakeyin abinda ranshi yakeso,
Juyi yayi a kujerar ya kalli bodyguard ɗin dake zagaye dashi yace " kun gano min gidan su wanan yarinyar ?" yes oga mun ganshi mahaifinta shine Alhaji Sani alherin Allah , buga ƙasa Kamill yayi tare da furzar da isa daga bakinsa ya katse mai maganar da cewa " wato ubanta bama kowa bane amma ta takani , to wlh bazan barta ba saina tozarta ta dole tayi hankali koda a gaba akace ta yiwa wani haka bazatayi ba ,

Miƙewa yayi ya nufi ciki daga bakin ƙofar flowers ne suketa haska ko ina , shiga yayi yana takunsa na ƙasaita ya zauna a kan wata fitinanniyar kujera ,wanan ɗaki na Kamill faɗar kyansa bazai rubutu ba,
Kasancewar ya tsaru shi kansa palon kai kace ɗakin mai mata ne , ga wani ƙamshi dake tasowa ta jikin wasu flawoyi dake manne a bango, ɗaukar apple ya ɗauka yakai bakinsa , kaɗan ya gutsura ya ajiye tare da cewa , natsaneki!!!!.
Ya riƙe kansa dake yimasa wani irin ciwo kasancewar sa inhar yasa damuwa a ransa to sai yayi zazzaɓi ,
wanan karon ma hakan ce zata faru ,
tashi ɗaya jikinsa yai zafi , babu inda ya iya bare ya kira bodyguard ɗin nasa su temaka masa sbda ya hanasu shiga part ɗinsa muddin ba shine ya turosu ba ,
Baccin wahala ne ya ɗaukesa sai wajen ƙarfe uku na rana ya farka ,
Jikin yayi masa sauƙi sosai miƙewa yayi ya zauna kan bed tare da janyo bed side ya ciro maganinsa ya ɗauki ruwa a fridge yasha ,
Jin wayarsa na ring ya dawo kan kujera ya ɗauki wayar , cikin muryar tasa da duk wanda yasansa yasan babu lafiya , yace " Aslamu Alaikum Abba .
Wa'alaikumussalam ɗan albarka ya kake , Kamill ne yace " lpy lou Abba yaushe zaka dawo ?" gobe insha Allah mai kakeso ?" dariya Kamill yasa kana yace " Abba akwai kyakyawan albishir wlh Allah dai ya dawo dakai lafiya , kodai mafarkina na ne zai tabbata zan sami suruka , dariya kamill yayi yace " saidai kazo ɗin sukayi sallama ya kashe wayar.

Hoton fuskar Diyana ne keyi masa yawo da wata shu'umar dariya yayi ya miƙe toilet ya nufa ya ɗauro alwala yafito domin zuwa masallaci.
Da wani buhu Tinene ta fito da alamu buhun kayansu ne , Nana tazo wucewa Hajiya ta kirata , durƙusawa tayi tace " gani hajiya ,
Hajiya dake mamular goro tace " ina abincin namu ?" da sauri Nana ta miƙe tanufi kitchen ta fito da shinkafa , da cokula guda biyu dakuma faranti ,
Bajeshi Hajiya tayi, suka fara ci jin abincin yayi daɗi Tinene ta turo baki tafara shura ƙafa tana cewa" gaskiya kaka inhar na yarda na biki to yasin nayi asara ,
Innalilahi bina hine asara?"
Ƙara kai lomar shinkafa Tinene tayi tana cewa wanan ai hine kaga samu kaga rahi any zan iya bin Kaka kuwa ,
11am momy da iyalanta sun hallara a dining yau kam sun gaishe da Hajiya , breakfast momy da Afreeda sukeyi banda Diyana da ruwan lifton takesha sai juya cokali takeyi a ciki alamar akwai abinda ke damunta, babu wanda ya kulata ,
Wayar momy ce tafara ring ganin sunan dady yasata ɗagawa tare da gaisuwa ,
Ganinan shigowa ma ina bakin get , masha Allah momy tace " Allah ya shigo dakai lafiya ,
Hajiya da ɗan ƙullin buhunta da Tinene suna zaune ,
Sukaji sallamar Alhaji ,
Washe baki Hajiya tayi tace " hannu dai Alhaji ,
ywwa Hajiya munsame ku lafiya ?
Lpy lou Hajiya tace " tana daɗa gyara ɗaurin bakin buhunta ,
Hajiya mekuma muka samu ?"
Diyana da Afreeda ne suka karɓe zancen da cewa barka da dawowa dady , kafin ya amsa Hajiya tace " gida zan wuce bazan ƙara kwana a gidanka ba kaji na gaya maka ,
Sunkuyar da kai momy tayi dan wanan al amarin yafi ƙarfinta da tana ganin abin kamar wasa yanzu ya wuce tunaninta , gara taja bakinta tayi shiru inyaso insun gama ta tofa nata ,
Gyara zama dady yayi yace " Hajiya kina nufin wai ƙauye zaki koma ?" eh Hajiya tace "

maiya faru da zaki ɗago tafiya haka yanzu da bayau zan dawo ba sai dai inji ta tafi kenan , Hajiya ce ta nuna momy tace" laifin matarka ni babu ruwana ehe tafiya zanyi gidanka duk aljanu hatta ɗakin da muke ma saida suka jamana kunne ,
Miƙewa tayi tare da janyo hanun Tinene tace " tahi karmuyi dare, momy da sai yanzu tayi magana tace " kayi haƙuri dan Allah ,
Da' na ɗauka ba tafiyar zatayi ba , shiyasa ban gaya maka ba .
Hanyar fita Hajiya take shirin yi dady yasha gabanta tare da durƙusawa yace " Hajiya dan girman Allah kiyi haƙuri ki zauna babu komai a gidannan ,
Zan kira ayiwa gidan sauka yau ɗinnan dan Allah karki tafi ,
Tausayi ɗa da uwa Hajiya ta juyo ta zauna kan kujera tana cewa " to wlh tun wuri ka kira malamin dan jiya a rumfa muka kwana ,
Dady baiji daɗi ba sam amma baice komai ba ,
Sama ya haura zuciyarsa babu daɗi ,
Bin bayansa momy tayi tana jiran abinda zai biyi baya ,
Salama tayi ta samesa yana cire maɓallin rigarsa ,
Ciki ciki dady ya amsa bai ko kalleta ba ,
Zama momy tayi a gabansa tare da janyo hannayensa ta zaunar dashi ,
haba mijina mai nayi da zakayi fushi dani ?"
Inhar maganar Hajiya ne to kayi haƙuri naɗauki lefin dan girman Allah ,
duk da haka bai kulata ba saima shirin shiga toilet ɗin ɗakinsa daya fara yi ,
Da sauri momy taje ta tara masa ruwan wanka ta tsaya a toilet ɗin tana jiran shigowarsa , tasan mulki da isa irin tasa ,
Har ace gadon wa Diyana tayi hmm , momy taji shiru bai shigo ba ,
tana fitowa ta samesa a zaune yayi shiru yana bubuga ƙafa,
ɗumin hawayen da yaji ne yasa shi ɗago fuska a razane yace " Faty maiya faru , cikin kukan kissa momy tace " nabaka haƙuri kaƙi saurarata kasan bana jurar ɓacin ranka ,
Janyota yayi jikinsa yafara shafa gashin kanta alamar tayi shiru , bakya girma ,
Dady yace " yana murmishi , itama murmishin tayi tace " to kaima ɗin haka ne ,
miƙewa dady yai yace " zoki taimaka min inyi wanka idan na kintsa inason muyi magana dake ,
Miƙewa momy tayi daga kan cinyar dady ta riƙo masa hannu suka nufi toilet ,
Diyana da Afreeda ne a ɗaki kowacce na baƙin cikin dawowar Hajiya gidan , gaskiya dama Allah bai dawo dady yau ba da sunji daɗi ,
Diyana da abin duniya yataru yayi mata yawa tace " kiji ɗazu wai laifin momy take cewa ?" Afreeda ce ta cire tagumin fuskarta tace " ai wlh tadinga haɗa momy da dady faɗa kenan tunda bakinta bashida zip .
Haka dai suka dinga jajantawa gashi sun rasa mafita da zasu ɓullowa lamarin.

Yau Alhaji Safiyan ya sauka a Nigeria bai sanarwa kowa ya sauka ba sai drivern sa , kai tsaye daga airport unguwa uku aka wuce dashi wato gidansa ,
tun daga bakin get bodyguard keyi masa barka har yakai ga shiga cikin gidan ,
Hajiya Amina dake zaune a kujera wata dattijuwar mata tana mammatsa mata ƙafa ta miƙe , tana murmishi tare da cewa " barka Alhaji dawowa babu sanarwa ,
Alhaji ne yace " banda abinki Meena wanan karon nefa ban sanar miki ba to ayi haƙuri , sukasa dariya dukkansu ,
Tunda ma'aikatan gidan sukaga shigowar Alhaji kowacce tashe kitchen mai girki nayi mai haɗa lemo nayi mai farfesu kifi nayi mai farfesun kaji nayi abinci dai kala kala kowacce ta kama dama ƙa'idar gidan kenen ,
Amina ce tace " Alhaji tashi muje kayi wanka sai kaci abinci ,
Babu musu ya miƙe amma a zahiri burinsa yaga Kamill ,
Bayan yayi wanka yai shigar alfarma ya fito shida Ameena suka nufi dining da masu aiki suka cikashi da kayan ciye ciye dakuma abinci masu lafiya ,
jollof ɗin shinkafa Ameena ta nunawa Alhaji tana dariya tana cewa " alhaji ga abinda kakeso yaji kayan lambu ,
Alhaji dake daddana waya yace " zubamin kisamin farfesun kifi a gefe,

Bayan dady yaga cin abinci ya tambayi Kamill ,
yamutsa Fuska Ameena tayi tace " rabona da insashi a ido 3 weeks kenan ,
Jinjina kai Alhaji yayi batare da yace " komai ba ya miƙe ya fice direct ɗakinsa ya nufa ya kwaso wayoyinsa ,ya danna lambar Kamill , ring ɗaya ya ɗauka tare da sallama , Alhaji na amsawa yace " kazo gida ina nemanka ,
Tom Abba harka iso ne ?"
Eh Abban yace " ya kashe waya .
bubuga ƙafa Kamill yashiga yi kamar ƙaramin yaro yana cewa " natsani zuwa gidannan wlh amma babu inda na iya dole na naje ,
wanka ya shiga ransa a ɓace ya fito ya zura jallabiya baƙa mai hula ,
ko shafa mai baiyi ba yafito riƙe da key a hanunsa ,bodyguard ɗinsa ne suka fara jero masa barka ,
Babu wanda ya kula driver ne ya fito da sauri yace " Alhaji wacce motar za'a ɗauko ,
wani mugun kallo kamill ya watsawa driver ,
Babu shiri driver yayi ta kansa , ma'aikatan gidanne suka fara gulma akan yanayin da uban gidansu ya tashi Allah yasa lafiya ,
Jin faɗuwar gaba ta tsanta masa yasa shi ambato innalilahi a rayuwarsa yatsani Amina shiyasa ko gidan baya son zuwa , Allah yasa ba wani bom ɗin ta haɗa masa ba a gurin Abba ,
Shiga wata mota yayi fara kyakyawa ya harba titi , tafiya yakeyi yana tunani yarasa dalilin faɗuwar gabansa ,
wani mahaukacin horn yayi sanin ko waye yasa masu gadi da kowa na gidan saita nutsuwarsa ,
Mai gadi na buɗewa Kamill ya shiga , daga bakin get ɗin yayi parking ya nufi ciki , duk yawan mutanen da suke miƙo masa gaisuwa bai kula kowa ba, ko sallama baiyi ba ya shiga palon , Ameena na zaune tana kallo a tv ta ɗago kai ta kalesa ta mayar da hankali ga tv .
Abba na ciki ?" Kamill yace " kana ya kawar da kansa gefe yayi ,
Ganin bazai sami amsa ba ya wuce ta bai ko ƙara kallon inda take ba ,tofa maiya haɗa Ameena da ɗanta ..
Yana shiga ya sami Abba zaune da laptop a hanunsa yana sanye da farin glass a fuskarsa ,
Cikin fara'a Abba ya ɗago kai yace " oyoyo my son ,
Barka dai Abba Kamill yace " yana neman gurin zama ,
Bayan sun gaisa da Abba shiru ya biyo baya na yɣan wasu mintuna , Kamill ne yafara dana sanin sanarwa da Abba , alƙawarin da yayi ,
Jin shiru yayi yawa Abba yace " to Kamill Abbanka ya dawo cike da farincikin son jin albishir ɗin da zakayi masa ,
Wata mumunar faɗuwar gaba ce takuma ziyartar Kamill zufa na keto masa ,
Cikin ransa yace " zan cuci kaina mai ya kaini gayawa Abba kuma inya faɗi magana baya sauyi , shafa sumar kansa yayi yace " am Abba dama dama...
Abba ne ya fahimci maganar tayiwa ɗan nasa nauyi ya murmusa yace"karka damu koma menene gayamin bakada matsala ko kaɗan ,
Kamill ne yace " Abba yarinya nagani ...
Ragowar maganar ta maƙale masa a maƙoshi , masha Allah Abba yace " yana faɗaɗa fara'arsa , Kamill ko sai yanzu yakeyin asalin dana sani sosai .
Yɣar gidan waye ?" Abba ya tambayi Kamill ,
Yɣar gidan Alhaji Sani alherin Allah ce , Abba ne ya ƙara murmusawa yace " haƙiƙa wanan rana nake jira naji daɗi sosai nayi farinciki , ai mutumuna ne shiɗin babu damuwa komai zai dai daita kaidai kaci gaba da nemanta insha Allah auranku zai zamo alkairi ,
Kan Kamill a sunkuye baice komai ba yanata nazarin maganar da ya yiwa Abba , nasiha Abba yashiga yimasa akan halin rayuwa , daga ƙarshe Abba yace" ka kiramin Amina ,

ɓata rai Kamill yayi yace " tafice daga gidan zan shigo naga tahau mota driver ya jata, what..! Abba yace " yaushe ta tambayeni dahar zata fita , oky jeka idan mukayi magana da uban yarinyar zan kiraka , tom Abba Kamill ya fice ranshi ta wani fannin fess wanan makirar zatasha faɗa , ya fice daga gidan ,
Yana shiga mota maganar da ya gayawa Abba dakuma farincikin da Abba yayi akan maganar auran ba ƙaramin ɗaga masa hankali yayi ba ,
Tabbas Diyana bata cikin jerin matan da yakeso , sbda ita ɗin batada kunya ga rashin sanin darajar mutane ,
" Gaskiya nayiwa kaina da zuciyata rashin adalci Kamill yaketa nana tawa kamar bitar karatu ,
ikon Allah ne ya kaisa gidansa , yana zuwa yayi horn ba'a ɗauki lokaci ba mai gadi ya buɗe get ɗin da gudu tare da durƙusawa yana miƙa gaisuwa , ɗabi'ar Kamill ne in ana gaishesa ƙin daraja mai gaishesa , basajin daɗin abinda uban gidan nasu yake yimusu , amma babu inda suka iya shiyasa suke taka tsan tsan da duk wani abu dazai haɗasu dashi .

bodyguard ɗinsa kuwa kowanne ya shiga tai tayinsa kasancewar oga baya wargi ,
Gashi yafita da ɓacin rai kuma ya dawo dashi .
Fitowa palo Alhaji Safiyan yayi , ganin Ameena na zaune tana danna waya , yasashi neman guri ya zauna , kana yace " meena yaushe zaki dena fita batare da izinina ba ?" waro ido Ameena tayi tace " ina zanje Alhaji ?"
Yanzu na aiko aka cemin kinfita a mota , buɗe baki tayi tasan babu mai yimata wannan sharin sai Kamill ,
Tarasa mai tayi masa ya ɗauki karan tsana ya ɗora mata ,
Hawaye ne suka fara zarya a fuskarta cikin she sheƙar kuka tace " Alhaji sai yaushe ne zaka dena kama maganar wanan yaron ,
Ina nake zuwa ?
Alhaji da ya ƙurawa fuskar Ameena ido yace " naji ya wuce amma kisanj Kamill ba yaro bane yakai time ɗin da zandinga shawara dashi so kin fahimta?"
Kawar da kanta gefe tayi dan intaci gaba da biye masa zasuyi babu daɗi '
Ita kuma batason musayar yawu da mijinta.
Bayan dady ya fito daga wanka momy ta temaka masa ya shafa mai ya sanya kaya , janyota yayi kusada shi suka zauna akan kujera ya kalleta yace " Faty mgnar da nakeson yi dake shine inason mahaifiyata ta zauna tare dani ,
Banison tayi nisa dani duk da akwai mai kula da ita a can ɗin ,nima inason samun nawa ladan , shafo kansa momy tayi kana tace " Habiby nima inason zaman Hajiya a gidannan ,
Ita da kanta ta matsa wai saita koma ƙauye tace " da aljanu a gidanan , nidai a iya sanina bansan dasu ba , amma bansan ko akwai ba .
Gyra zama dady yayi yace " ina tunanin harda rikicin tsufa .
Daganan suka miƙe tare momy ta kashewa dady ido tare da cewa , ga shayinka fa na shigo dashi , okay dady yace " ina zuwa yanzu zan dawo ya fice .
ƙasa ya sauƙo yana tunanin tafiyar mahaifiyarshi , samunsu yayi a palo zaune suna kallo ,
Zama dady yayi kana yace " barka da hutawa Hajiya ,
Ywwa barka Alhaji ya aikin naku ?"
Lpy lou dady yace " yana kallon Tinene da keta baza ido a tv " ke baki iya gaisuwa bane ?" sosa kai ta shigayi tana washe haƙora tace " hannu dai ina uni lpy dady yace " yana murmishi , ring ɗin wayarsa ce ta katse masa maganar da yakeson yi .
Ganin sunan mai kiran nasa yasa shi miƙewa da sauri ya haura steps zuwa ɗakinsa lokacin momy na toilet ɗinsa tana wankewa kasancewar bata yarda da yan aiki sudinga taɓa mata abinda ya shafi mijinta ba .
Zama yayi a bakin gado tare da amsa kiran ,
Sadda kai ƙasa yayi da alama da wani babban yake waya ,

dady ne yace " Allah ya temaki mai gida kuma Allah yaƙara maka lpy , daga can ɓangaren mutumin yace " wata muhimmiyar magana ce ta taso amma dole sai mun haɗu .
Cikin rawar jiki dady yace " to ko inzo me kawai ace kamarka ka shigo layinnan ,
NO. mutumin yace " karka damu dole nine zanzo buƙatar hakan ce ta taso karka damu.
Cikin rawar jiki dady yace " to da ƙarfe nawa zaka iso , mutuminne yace " bayan sallahar isha'i yayi ko ?" dady da fara'arsa yace " yayi Allah ya kawoka lpy ,
Sukayi sallama.
bayan dady ya ajiye wayar ne yafara tunanin mai zai kawo Alhaji....gidannan kodai yayi laifi ne , wata zuciyar tace " kazuba ido koma menene zaka gani Allah dai yasa alkairi ne .
Har momy ta fito daga toilet dady bai sani ba yayi nisa a tunanin Alhaji.... kamo hanunsa momy tayi kana tace " habiby ka zauna man amman dai lpy ko ?"
Da 'alamu na damuwa yace " faty baƙo zanyi maza kisa yɑn aiki su haɗa abinci mai kyau kamar kala biyar haka ,
Ok momy tace " kana ta fice , lokaci babu wuya jiyo kiran sallahar magrib yasa dady miƙewa ya yi alwalah ya nufi masallacin gidan ,
Bai dawo ba sai da akayi isha'i sanan ya shigo , babu kowa a palo ya haura step da sauri yana kiran momy , fitowa momy tayi daga ɗakinta , sai zuba ƙamshi takeyi tasa riga da skirt sun ɗameta amma tayi kyau , rungumota dady yai kana yace " Faty na kullum kamar ana sake maidake baby , shafa fuskarshi momy tayi tana dariya tace " to ya ka ganni nayi kyau ko ?"
Yana shirin bata amsa kira ya shigo wayarsa.
Sadda kansa ƙasa yayi tare da cewa ranka shi daɗe barka har kun iso ne ?"
Eh Alhajin yace " gani a mota anbuɗe min get na shigo ,
Dady na shirin ficewa da sauri momy ta taro shi ,
Maiya faru ne Faty ?"
Haba habiby baka gayamin maike faruwa ba nadai ga kana rawar jiki ,
Cikin alamar yana sauri yace " baƙo nayi kuma yanada muhimmanci a gurina, bugu da ƙari kuma kowane ma'aikaci nada burin ganin wanan bawan Allahn ya raɓesa sbda tsananin dukiyarsa dakuma goyon bayan manya daya samu ,
Riƙe baki momy tayi ,
Kana tace " to Allah ya jishemu alkairi ,
Amma shida kansa yazo har gidanka ?"
Ficewa dady yai batare da yabata amsa ba ,
Momy ta jimama zuwan wanan bawan Allahn daga ƙarshe dai tace " Allah ya tabbatar da alkairi ko me ya kawosa oho , ta koma bedroom ɗinta.
Dady na zuwa ya sami Alhaji ya fito daga mota yana zaune a wata farar kujera ,
Da sauri ya ƙarasa yana cemasa barka da zuwa ,
To tashi mu shiga daga ciki ranka shi daɗe ,
Miƙewa Alhaji yayi dady ya kaisa palonsa , palo ne daya ƙawatu da kayan alatu na zamani sai dai duk wanan ba komai bane a gurinsa kasancewar yatara gidajen da sukafi na Alhaji sani komai ,
Yɑn aikin ne suka fara shigo da abinci kala kala , yɑn aikin suna cikin shiga mai kyau drinks da abinci sunkai kala biyar .
kunun aya Alhaji ya zuba a cup kasancewar baya baƙunta akan abinda yake so ,
Bayan ya ajiye cup ɗinne suka gaisa tare da tambayar iyalai dakuma aiyuka ,
Bayan sun gama gaisawa Alhaji ya gyara zama tare da kallon dady yace " Alfarma nazo nema a gurinka ,
Cikin rawar jiki dady yace " har saikazo daka kirani ai .
Murmishi Alhaji yayi yace " a gurguje dai inason gayamaka abinda ya kawoni .
Dady da ya matsu yaji ko menene yace " to ina jinka?.
Masha Allah cewar Alhaji , yarona ne yaga yɑr gurinka yake sonta.
Nisawa dady yai kana yace " wacce daga ciki ?"

Diyana Alhaji yace " yana faɗaɗa fara'arsa.
Dady sai da ya jinjina sunan Diyana a zuciyarsa yasan inhar bata son mutum to ko inuwarsa bata raɓa garama Afreeda .
Alhaji ya lura da dady ya tafi dogon tunani ,
Baiyi masa magana ba saida suka dau tsawon mintuna kana dady yace " karka damu insha Allah bazai gagara ba ranka shi daɗe ,
Washe baki Alhaji yayi yana ganin alamun nasara ta bayyana .
Daganan Alhaji ya miƙe da niyar wucewa , rakashi har zuwa gurin motarsa dady yai Alhaji yace " to nanda kwana uku zan kuma dawowa inhar Allah ya yarda dakuma yarinyar banason aɗau lokaci mai tsayi , insha Allah kawai dady yace " dan bashida wata kalma dazai faɗa ,
Da haka dai sukayi sallama .
Zuciyar dady babu daɗi kasancewar bayason yiwa yaransa auran dole .
Bazai iya hana Alhaji Safiyan auran yarsa ba dan yayi masa abinda ba kowane zai iya yimasa ba.
Har aka buɗewa Alhaji Safiyan get dady bai motsa ba , saida ya jima a tsaye sanan ya shige ciki .
Momy nata tararradin dady ko lpy .
suna zaune a palo dady ya shigo Hajiya da kecin tuwo tana suɗe hannu tace " Alhaji ina ka shiga munjika shiru ga abincinka nan ko sai yayi sanyi zakaci ?
Ganin yanayinsa yasa momy shan jinin jikinta , a zuciyarta tace " akwai matsala , cigaba da magana hajiya tayi takuma cewa wai lafiya naganka haka ?"
Lapy lau dady yace " hajiya barin watsa ruwa ina zuwa ,
yana tafiya momy tabi bayansa .
Mtsw Hajiya tayi tsaki tare da cewa kwaji da tsohuwar gulmarku ni har zan tambaye shi abu yaƙi gayamin ,
kwashewa da dariya Diyana da Afreeda sukayi dan lamarin yabasu nishaɗi sosai.
Kunci gidanku wlh yarannan kun raina ni ,
Miƙewa sukayi kowacce bakinta a kunshe da alama dariya suke shirin yi akuwa suna isa kusada ɗakinsu suka saki dariya mai sauti ,
Tinene dake kokawa da ƙashi tazaro ido kana tace " wlh Kaka dariya suke yimiki , ƙwafa Hajiya tayi tana jiran shigowar dady.
kwance dady yake a kan gado idanunsa a sama yana tunanin maganar Alhaji Safiyan ,
Momy tayi tambayar harta gaji daga ƙarshe ta miƙe idanunta sun kaɗa sunyi ja zata fice ,
Miƙewa dady yai tare da ruƙo hanunta yace " matsalar nan ta shafemu duka ,
momy dake nazarin maganar dady tace " kanata magana baka faɗi mafarinta ba .
Dady ne yace " yazo nemawa ɗansa auran Diyana ne , kuma kinga duk abinda Alhaji Safiyan ya nema a gurina dole in bashi koda banida shi dole in nemo masa bare jinina yake nemawa ɗansa .
Jinjina zancen momy tayi ,wai hausawa sukace da kamar wuya gurguwa da auran nesa ,
To ai matsalar Diyanan ce akwai taurin kai ni kaina bata cika bin umarni na ba ,
Dama Afreeda ce to da sauƙi .
Haka dai suka dinga saƙa da warwara suka yanke shawarar gobe insha Allah zasu yiwa Diyana magana dakuma Hajiya .
Hajiya tagama zaman jiran fitowar dady shiru babu shi babu dalilinsa ,
Gashi Tinene nata rafka uban gyangyaɗi ,
Tashinta Hajiya tayi suka nufi ɗakinsu tanata mita harda cewa momy tsohuwar munafuka.
7:am Kamill ya tashi kasancewar yayi sallahar asbha shine ya koma ya kwanta , bathroom ya shiga yai wanka yana gama wanka yai brush tare da fesawa bakinsa mouth freshner ya fito ɗaure da towel a ƙugunsa da wani kuma rataye a kafaɗarsa ,
Gaban mirror ɗinsa ya nufa yana ƙarewa kansa kallo ,

tabbas a yan kwanakinnan ya rame , amma wanan yarinyar ta cucesa maiyasa zai sa tunaninta a ransa cox shi ba ƙara bibiyarta yayi ba , ƙwafa yai a fili yace " da ƙafarki zaki tako har cikin gidana zakisha mamaki ,
Ɗauko mansa mai tsada yai kana ya shafe duk jikinsa da turaruka masu ƙamshi ya gyara sumar kansa ,
Ya miƙe ya nufi drower gurin ajiyar kayansa ,
Riga da wando ya jiro na jeans rigar pink color wandon kuma blue ,
Bayan yasa boxer ya sanya wandon da riga yakuma feshe jikinsa da turare , ya fito palo kunna tv yayi tashar mbc action ,
Hankalinsa sam ba gurin tv n yake ba amma duk wanda ya kallesa zaice tv yake kallo time table na abincinsa ya duba , yau farfesun kifi da soyayyan dankalin turawa dakuma shayi mai kayan ƙamshi kana da kunun gyaɗa za'ayi masa ,
Kasancewar sai ƙare shabiyu na rana yake breakfast yasa babu wanda ya shigo masa da safe

Yana tsaka da tunani wayarsa tafara ruri ,duba mai kiran yayi sai da yaɗan jinkirta dan kiran yakusa katsewa ya ɗaga tare da sallama ya langwaɓar da kai kamar yana kusa dashi ,,
Abba daga can ɓangaren yace " my lovely son ka tashi lpy ya hutawa , Kamill dake ɗan yamutsa fuska yace " am fine Abba ya aiyuka , lafiya Abba yace ".
Daganan Kamill yayi shiru , Abba ne yace " jiya naje gidansu yarinyar nan munyi magana da mahaifinta yace " insha Allah bazai gagara ba ,
Kamill da ko son jin sunan Diyana bayayi yace" tom Abba ,
Bakada lafiya ne ?" cewar Abba Cewa" Kamill yayi banajin daɗi ne ,
Subhanallah dady yace " kayi ka fito kaje hospital ,
Kamill ne yace " inada ragowar magani naji sauƙi ,
Alhaji bayason musu yayiwa Kamill sallama ya ajiye wayar .
10:am kowa ya hallara a dining domin karin kumallo inka cire Hajiya da Tinene dake ƙasa kan kafet a zaune suna nasu karin ,
Bayan sun kammala dady ya dubi Hajiya yace " Hajiya ya kike ganin maganar da mukayi ɗazu dake , tunda yanzu ga sunan ,
daga Diyana har Afreeda babu wacce ta fahimci abinda dady yake nufi ,
gyara zama Hajiya tayi kana tace " gaka gasunan ai kokuma ince gatanan ai ,
Komawa kan kujera dady yai Diyana na shirin barin gurin hanunta riƙe da waya dady ya tsayar da ita ,
Juyowa tayi batare da tace " komai ba , sanin dama ba magana zatayi ba yasa momy buɗar baki tace "haba daughter ana yimiki magana kin tsaya kamar kurma?" tahowa tayi ta nemi guri nesa da kujerar dady ta zauna tare da cewa gani dady ,
Yatsina baki Hajiya tayi kana tace " wlh bakida hali mahaifinki na yimiki magana kin wani tsaya kamar sa'anki ,
momy dai batada bakin magana ta rufe bakinta ,
Wata uwar harara Diyana ta dokawa Hajiya , cikin sauri Hajiya ta miƙe tare da saka kururuwa tana salati ,
Alhaji na gaya maka bazan zuna a gidanan ba ka matsa yanzu gashi wanan marar kunyar tana nema ta dokeni wlh kashiga tsakanina da ita tun wuri,
dady kam yarasa ta cewa ga damuwar Hajiya ga damuwar shi , shida Diyana ,
Hajiya kiyi hauri dan Allah zanyi mata magana amma yanzu mu samu mu kashe wutar dake gabanmu ,
Shiru Hajiya tayi tana girgiza ƙafa kamar mai jiran a taɓota .
Diyana " dady ya kira sunanta a hankali .
Na'am dady , Diyana tace " ta maida hankalinta gareshi ,
Alfarma nake nema a gurinki da fatan bazaki watsamin ƙasa a ido ba ?" jimm Diyana tayi kana tace " insha Allah dady bazan watsama ƙasa ba.
good Dady yace " nayi miki miji .....! Jin zancen tayi kamar saukan aradu ba ita kaɗai ba har Afreeda ma saida ta girgiza da jin wanan zance ,

Dady bai bari ya kaleta ba saboda kalonta zai iya sa zuciyarsa karaya ,
Yacigaba da cewa " haƙiƙa ina alfahari daku dakuma tarbiyar da nabaku nidai banida burin yiwa yʻayʻana auran dole ,
yanzu dai inason jin ta bakinki Diyana sbda ba wani ne zaiyi miki zaman auran ba , kuma zaman aure ba abin wasa bane zamane na har abada .
yanzu wace shawara kika yanke ?" Hawaye ne suka fara sintiri a kyakyawar fuskar Diyana babu sautin kuka sai zubar hawaye , tafa hannu Hajiya tashiga yi tana ni yʻasu sai kace " wacce za'a fillewa kai toni lokacin da aka yimin aure bansan kakanku ba ,kuma ban taɓa ganinsa ba sai ranar da yashigo dakina bayan an ɗaura aure ,
Dariya ce taso kuɓucewa momy dake zaune a kujera ta zuba tagumi, toshe bakinta tayi bata bari kowa ya gane ba ,
Bayan Hajiya tayi shiru dady ya kuma tambayar Diyana a karo na biyu ,
kalmar da ta fito daga bakinta ne yayi matuƙar firgita mutane kowa yayi mamaki.
Na 'amince dady na amince ta miƙe tayi bedroom ɗinsu da gudu hawaye na zarya a fuskarta , momy ma hawayen take sharewa kasancewar tasan Diyana ba har cikin zuciyarta ta faɗi wanan kalmar ba,
Liyafa dady yasa a shiryawa Alhaji Safiyan ta bangirma abinci kala2 .
Bayan isha sai ga kiran Alhaji nan ya shigo ,
Dady na ganin kiran ya miƙe jiki na rawa ya fice , samun Alhajin yayi a jingine a jikin motarsa kamar inda yayi rannan da sauri dady yace " haba Alhaji tashi mu shiga ciki dan Allah ,
Miƙewa Alhaji yayi tare da rufawa dady baya suka shiga palon dady ,
Bayan sun gaisa dady ya gabatar masa da abinci , kaɗan Alhaji ya taɓa kana yace " ya ƙoshi kai tsaye suka fara maganar yʻa'yʻan nasu , dady ne yace " na tuntuɓi yʻar gurina tace " ta amince ,
Kafin dady ya kai ga ƙarasa magana Alhaji ya faɗaɗa fara'arsa yana yiwa Allah godiya , cikin zuciyarsa yana cewa haƙiƙa duk da bansan yarinyar ba nasan yarona yayi dace duba da halin mahaifinta na cika alƙawari , masha Allah kowanensu yace " Alhaji ya dubi dady yace " a yanke dukiyar aure atemaka mana banason auran ya wuce wata ɗaya .
Dubu ɗari ma yayi Allah yasa ma dukiyar da auran albarka ,
Dariya Alhaji yasa kana yace " a haba zanbada 1 million yʻarka yʻata ce .
Nasani dady yace " karka manta Alhaji bawai naƙi bane amma mafi ƙanƙantar sadaki yafi daraja dakuma ƙarawa aure ƙarko , daganan sukayi sallama
Akan gobe zai turo magabata ,
dady na komawa bai zarce ko ina ba sai ɗakin mahaifiyarsa , ya bata labarin abinda ke wakana cewa Hajiya tayi " karka damu ka tura direba ya taho da ɗan uwanka hudu sai ya tsaya akan komai , dady yai farinciki yayiwa Hajiya sai da safe .
Duk wanan abin da akeyi Diyana batasan waye mijin ba ita dai ta amsa .
Washe gari abinka da masu shi ƙarfe biyar har yʻan uwan dady sunzo su biyu ,
Bayan sallahar isha'i baƙin dady sun hallara , aka bada dukiyar aure dubu ɗari biyar dady yaƙi karɓa amma sun turje sai da sukasa yʻan uwan dady karɓar kuɗin.
Suka sanyawa dukiyar Albarka tare da auran in an ɗaura , daganan aka saka rana wata ɗaya ,
Dady bai dawo cikin gida ba sai wajen ƙare 11pm na dare direct ɗakin momy ya nufa , tana sanye da sleeping drees wanda ya fito da ilahirin kyanta ,
Dady da yazo bata labarin abinda sukayi ai yama mance ya shiga toile ya yi brush kana ya watsa ruwa ya sanya jallabiya yabi bayan momy , niko nace asbha ta gari dady lol.
Washe gari dady ya dawo daga masallaci da asbha , ya sami momy da zaune kan sallaya tana karatun alqur'ani , saida ya jira ta idar kana ta gaishesa ,
Bayan sun gaisa dady yace " Faty jiya fa ankawo kuɗin auran Diyana wani uban faɗuwar gaba taji amma tarasa dalilin hakan , murmishin yaƙe tayi tare da cewa Allah ya sanya alkairi ,

Suka shiga wata hirar daban , momy ce ta katse musu hirar ta hanyar cewa " niko sunama waya da saurayin kuwa ?" dady dake nazarin maganar momy yace " to wayasani ko zatayi ai ba sani zakiyi ba , shiru momy tayi daganan kowa ya kama gabansa ,
Dady yayi ɗakin Hajiya dan ya gaisheta momy kuma ta shiga wanka ,
Zaune take itada Afreeda suna tattauna abinda ya faru jiya , Afreeada ce ta dubi Diyana tace " sis yanzu kin yarda da auran dole kenan bakima san mijin ba ?" karki damu my sis su dady nayiwa biyayya ina tausayin momy yanzu da ban yarda ba sai kiga Hajiya da dady sunkama jin haushinta , nasani itama bataji daɗin hakan ba , amma a yau ɗinan danaji ance wai ankawo dukiyar aurena , nayi danasanin cewa na yarda , ta fashe da kuka ,
Lil sis ban taɓa soyayya ba bansan ya ake yinta ba to yazanyi da mijin takuma fashewa da kuka mai sauti a karo na biyu ,
Rungumeta Afreeda tayi suka cigaba da kuka .
kira ne ya shigo wayar momy lokacin tana zaune a dining zasu fara breakfast , kasancewar ta shiga ta kira su Diyana ,
Allah ya temaka lokacin sungama kukan har sunyi wanka amma mai lura yaga idanunsu zai gane sun zubarda hawaye ,
Ɗaga kiran momy tayi tana dariya tace " haba mom Khady zan aiko su Afreeda anjima suzo su karɓa min , jinayi momy ta ce sai anjima tare da ajiye wayar , dady ne ya kalli momy yace " dawa kike waya?" murmishi momy tayi kana tace " da matar abokinka man Mom Khady ok dady yace "
Hajiya dake ƙasa ana cin farfesun kaza ta taɓe baki tana zabgawa momy harara , lol ko meye damuwarki yar tsohuwa oho .
Suna gama breakfast sukayi bedroom ɗinsu ,
Shigowa momy tayi riƙe da wata bag a hanunta ta miƙawa Diyana , amsa Diyana tayi tare da cewa meye wanan momy , momy ce tai murmushi tace " kwalabe ne zakiji komai idan kukaje amma karfa ku daɗe dan Allah ,
to sukace kowacce ta canza kaya , iri ɗaya sukasa riga da skirt na atamfa mai ratsin green and wite ba ƙaramin kyau sukayi ba musamman ma Diyana da kamar dan ita akayi atamfar ko ince ɗinkin ,
takalminsu kala ɗaya kai komai ma wayace kowa da kalar tashi suka fito tare da bag ɗin da momy ta basu suka nufi gurin driver , sbda babu wanda zasu aika yar aikinsu ta tafi garinsu gaida mahaifiyarta ba lpy , samun drivern sukayi a tsaye yana jiransu , motar da ya fito da ita Diyana ta kalla tare da yamutsa fuska ta lumshe ido , ta buɗesu kamar mai jin bacci tace " bazamu shiga wanan ba ka fito da sharon nafijin daɗin hawanta ,
Jikin driver na rawa ya fito da motar suka shige , mai gadi ya buɗe suka ɗauki hanya ,
suna cikin tafiya go slow ya haɗu , mutane kowa na tofa albarkacin bakinsa ,
Wata mota mai ɗan karan kyau ce ta fito daga wani titi da yayi hanyar gaban wato titin da su Diyana zasu bi ,
Ran Diyana ya ɓaci a masifa tafara tana shirin buɗe murfin mota tana cewa " wanan ai rainin wayo ne yaushene za'a tare mutane akan wanan banzar motar shi waye mai motar ? ta ƙarasa fitowa tana bam bamin masifa , wani bawan Allah dake kan mashin kana ganinsa zaka gane ya haifi Diyana dan a ƙalla yayi sa'an mahaifinta , yawu Diyana ta tofar tana ƙaƙarin amai , kai kuma waye da zaka zo ina magana kana magana , Allah ya baki haƙuri mutumin yace " tare da jan mashin ɗinsa gefe , sbda kar ya janyowa kansa sanin yayan masu kuɗi basu ganin mutane da daraja,
Leƙa cikin motar tayi tana yiwa drivern su masifa , tana cemasa maza ka tada mota mu tafi inga uban da ya tsayawa wanda suke jira ya wuce , dan rainin wayo ma tafiyar kamar motar bazata wuce ba sukeyi , ta shige mota , Afreeda na tsoron magana karta haɗu da nata kason yasata yin shiru ,
tafiya Drivern yakeyi cikin fargaba dan yana tsoron mutanen gabansa da suketa wucewa motar ogan nasu na gefe.

Zune yake a cikin mota fuskarsa rufe da farin gilashi ba ƙaramin kyau yayi ba,
Wace mota ce ta shiga gabanmu ?" tambayar da ya watsawa securities ɗinsa kenan drivern sa ne yace " wata yarinya ne a cikin motar inaga batasan ko waye a cikin motar bane yasa basu kauce ba ,
Kamill da ransa ya fara ɓaci yace " maxa sha gabansu mu wuce waye ubanta ,
Da gudu drivern Kamill ya wuce su Diyana Masifar da take yiwa drivern su ne yasa shi gogar motar Kamill batare da ya lura ba , wani wawan birki drivern Kamill ya doka yana salati ,
Ba shiri Kamil ya buɗe mota ya fito ya nufi gurin motar su Diyana ,
Kai waye dahar zanzo wucewa kasha gabana .
Cikin tsiwa Diyana ta zuge glass ɗin mota zatayi magana taga Kamill ,saida gabanta ya faɗi tayi ƙarfin halin cewa " kai ɗin waye dazaka tarewa mutane hanya ,
Yana shirin buɗe motar tasu ya figota wani mutum yazo yana cewa " haba babban yaro ba girmanka bane ka ƙyaleta pls , juyawa Kamill yayi ransa a ɓace tareda ƙwafa ,
saida ya wuce su Diyana suka wuce lol.
suna isa ƙofar gidan da momy ta aikosu ta fice daga motar babu wanda ta kula , bubuga get ɗin tayi ba'a ɗau lokaci ba sai ga mai gadi ya buɗe , cikin sauri ta shige gidan tana sallama kamar ansata dole sai tayi,
mom Khady da yanzu ta fito ta iske Diyana zaune a kan kujera tana kuka ,
Shigowar Afreeda ne yasata maida kallonta ga Afrredan tace " yʻata mai ya sami kyakyawa ne naga tana kuka ? dariyar yaƙe Afreeda tayi dan ita duk budurin da Diyana keyi a titi dariyama ya bata , momy ƙila batada lpy ne , Afreeda tace " tana shirin zama akan kujera ,
Driver ne ya shigo da bag a hanunsa ya gaida momy ya miƙawa Afreeda ,
Miƙawa momy Afreeda tayi tare da cewa inji momy tace abaki , oky mom Khady tace tare da karɓa ,
Tayimin bayanin komai .
Diyana ce ta miƙe tare da cewa mom muntafi , haryanzu idanunta basu dena fidda hawaye ba ,
Janta momyn Khady tayi suka nufi bedroom ɗinta ,
zaunar da ita momyn Khady tayi a bakin bed ɗinta, itama ta zauna , fuskantar Diyana tayi kana tace " daughter na nasan problem ɗinki momynki tayimin bayanin komai so insha Allah zamuyi iya bakin ƙoƙarinmu gurin ganin kin sami farinciki ,
A gidan auranki , share hawayenki .
Share hawayenta tayi tace " momy na gode ,
Yanzu saura 29 days bikin zaki dawo gidannan nanda 1 week zan fara haɗa miki magani , kinji ?"
Tom Diyana tace " ta miƙe batare da momy tace " jeki ba ,
Da kallon tausayi momy ta bita tana girgiza kai .
Bayan Diyana ta dawo palo ta sami Afreeda da Khady a zaune sunata hira cikin farinci ,
Zama Diyana tayi nesa dasu ,
Khady ce ta miƙe ta nufi gurin Diyana , kasancewar sa'ar Diyana ce amma da yake su ba ƙawance sukeyi ba yʻan uwantaka suke ,
Khady ce tayiwa Diyana magana a kunne bansan mai tace mata ba naga Diyana na dariya .
Afreeda ce tace " sis zomu tafi okay Diyana tace " ta miƙe Khady tace " barin kira momy ,
Bayan momy ta fito sukayi sallama tace " zata kira momy suyi magana.
Suna fita suka shige mota driver ya kaisu gida kasancewar titin babu yawan motoci ,
Alhaji Safiyan ne zaune shida Amena yana waya , bayan ya ajiye wayar ne Amena ta dubeshi tace " Alhaji maganar kayan auran Kamill lokaci ya ƙarato , gyara zama Alhaji yayi kana yace " aikuwa wlh inason ayi kamar akwatuna dozin biyu , riƙe baki

tayi tana jinjina kai , a ranta tana cewa sai kace zai auri ƴar shugaban ƙasa , Alhaji ne yace " menna naji kinyi shiru ,
Dariyar yaƙe ta ƙaƙalo kana tace " to yaushe za'a fara siyayyar ? gobe insha Allah Alhaji yace " yana washe haƙora ,
Zansa ayau ɗinnan a tanadi komai gobe kawai sai mu wuce london a jirgi , farinciki fall zuciyar Amina sbda koba komai itama zata yagi rabonta .
after 2 weeks Diyana ta koma gidan mom Khady acan ake yimata gyara kama daga tsumi na gargajiya haɗin turaruka da shayin amare tare da kaji ga dilka da halawa da ake yiwa Diyana , abinka da farar mace sai ta koma kamar baturiya .
Wata ranar juma'a suna zaune ita da Khady , Khady na bata labarin wani novels da take karantawa a wattpad suna dariya , taji kira ya shigo wayarta, batasan mai kiran ba hakan yasata ɓata rai ,ta ajiye wayar gefe,
Khady da ta tsaya da karatun ta ɗaga wayar lokacin anyi kira na biyu , ta danna receive ta karawa Diyana a kunne ,
Mai kiran baiyi magana ba haka itama batace komai ba , jin Diyana tayi shiru yasa Khady ƙara volume ɗin wayar ,
Saida aka ɗauki mintuna mai kiran yace " barka dai amarya bakya lefi zaro ido tayi tanason tuno mai muryar ta kasa tayi iya tunaninta amma takasa tunowa ,
Waye kai??" Diyana tace " cikin sanyin muryarta .
Mijinki ne .
A ina ka sami number ta karka ƙara kiran wanan layin dan wanan baiyi kamada mijin da zan aura ba ta katse wayar.
Iya ƙolokuwar ɓacin rai Kamill yayi wani uban ƙara yasa wanda yaja hankalin masu tsaronsa dakuma masu yimasa hidima , suka shigo da saur, lpy oga ? suka tambaya a tsorace , idanunsa sun kaɗa sunyi jawur ya kallesu kana yace " karku damu kowa ya koma gurin aikin sa zan nemeku anjima,
Haka suka fice jiki babu ƙwari dan kwana biyunnan basajin daɗin ganin shugaban nasu haka .
Yanzu burinsa kawai yaga ankawo masa Diyana a matsayin mata Allah ne kaɗai yasan hukuncin da zaiyi mata , Ya miƙe tare da zagaye ko ina na ɗakin ranshi a ɓace .
Biki ya ƙarato shiri akeyi na musamman fanin momy da dady dakuma fanin iyayen ango ,
satin Diyana ɗaya a gidan momyn Khady yau ta dawo gida , kowa ya ganta sai yai sha'awarta .
Momy ce ta jata zuwa ɗaki , Diyana . momy ta kira sunanta
Na 'am Diyana tace " momy ce tace " shi mijin naki ya taɓa kiranki kuwa ?" a'a momy .
Diyana tace " kanta a sunkuye , momy tace " bare har akai ga maganar kuɗin anko taɓɓ , Diyana dai batace komai ba taci gaba da wasa da gezar rigarta , fashewa da kuka momy tayi tana salati , wanan aure shine ake kira da auran dole.
shigowar dady ne yasa momy saurin share hawayenta ta ƙaƙalo murmishin ɗole , tace " barka da dawowa Alhaji , ywwa dady yace " ya nemi guri ya zauna ,
Kalon diyana yayi tare da cewa kibamu guri daughter.
Dama abinda takeson ji kenan dan zaman ɗakin ya isheta kasancewarta ba mai son yawan surutu ba ,
Tana shiga bedroom ɗinsu taga Afreeda a zaune tanata kuka ƙara tashi hankalinta yayi ,
Da sauri ta iso kusada ƙa nwar tata tayi ta rungumeta , meya faru ne my sis ? wani kukan Afreeda takuma saki tana cewa " sis yanzu kin yarda ki auri wanan mutumin sis tafiya zakiyi ki barni , hawaye masu zafi ne suka zubo daga fuskar Diyana ,
Takuma rungume Afreeda sunata kuka .

BAYAN KWANA BIYAR.

Zaune yake kan yayataccen bed ɗinsa da yaji tsadden zanin gado , idan nayiwa yarinyar nan haka banyi mata adalci ba koda yake ta wula ƙanta ni , amma duk da haka kamata yayi nayi ruwa biyu , sai tashigo in tada mata da GUGUWAR ZALUNCI na shi kaɗai yaketa zancen zuci , yaci gaba da cewa" iyayenta zasu fahimci wani abun fa...
janyo wayarsa yayi ya danna lambarta da yai seven da no. ring ɗaya ta ɗauka cikin sanyin murya , kwanciya yayi tare da cewa " barka da wanan lokacin yan mata , ywwa dawa nake magana , ƙara duba number tayi tanajin kamar ta gane mai muryar amma tarasa inda tasanshi , fatan masoyinki ne mijin da zaki aura , zatayi magana ya katseta da cewa " ayimin haƙuri nasan nayi laifi dahar saida lokacin bikinmu ya ƙarato nafara kira ,
Diyana da taji wani sanyi ya mamaye zuciyarta tace " babu komai karka damu ta lunshe ido kamar yana ganinta , janyo fillo Kamill yayi tare da rungumewa ya daɗa kashe murya , yace " ya shirye shiryen bikinmu ni yanzu burina inganki kusa dani saboda in nuna miki zallar soyayya dakuma farinciki , Diyana da tayi nisa cikin love ta gyara kwanciyarta dama a kujerar palo take kwance , batasan Hajiya na gefe a tsaye ba tun ɗazu .
Gaskiya nayi sa'a nima ina fatan hakan amma meye na zumuɗi , dole nayi sbda muryarki nasani bansan kyawunki ba koda yake inada tabbacin kyanki shima ƙarshe ne, dariya tasa marar sauti sosai tace " kaima hakan ai , to yanzu dai nawa kikeda buƙata sbda a halin yanzu zanbar ƙasar sai ana gobe ɗaurin aure zan dawo , cewar Kamill .
Lumshe ido Diyana tayi kana tace "duk abinda ka bada yayi .
Kamill ne yace " 3 hundred thousand yayi ? eh tace " cikin farin ciki .
sallama sukayi kana ta miƙe waigowar da zatayi sukayi ido biyu da Hajiya , ko kallon inda Hajiya take Diyana batayi ba , jiyo maganar Hajiya tayi tana cewa " gulma da ance ba'aso yanzu kuma anzo ana kwarkwasa , wucewa Diyana tayi zuwa bedroom ɗinsu batare da ta kula Hajiya ba jin son lovely ɗinta takeyi kamar zai fasa zuciyarta , shigowar Afreeda yasa Diyana faɗaɗa fara'a tace " sis yanzu my husband ya kiranj , murmishi Afreeda tayi cikin zuciyarta tace " hmm yar uwata har yanzu bakisan wa zaki aura ba ina tausaya miki dakinsan Kamill zaki aura nasan da kina nan kina rusa ihu inma ba'a kaiki asibiti ba da sauƙi , sis sis me kike tunani a firgice Afreeda ta waigo idanunta cike da hawaye tace " banason rabuwar mu my sis , Diyana dariya tasa tana cewa inajin kamar nafi kowa sa'a a duniya sbda mijin da Allah yai min zaɓi, hmm Afreeda tace " tare da kwanciya a gefen Diyana .
Kamill ya turo wa Diyana kuɗi , bayan ta ciro a p o s kasancewar yanzu bata cika zuwa bank ba , dama sunsi komai karɓar kuɗin momy tayi tabata 50k ta riƙe a hanunta , ƙanwar momy data zo daga kano ta tsarawa Diyana haɗaɗen lalle baƙi da ja , ga gyaran gashi da sukaje jiya , ɗinkuna akalla tayi sunkai kala ashirin kuma duba babu marar tsada .
a yan kwanakin nan tayi ƙiba saboda kulawar da take samu daga gurin Kamill , suna tsaka da waya yace " amma baxa'ayi wani event ba ko dan har yanzu ban dawo nigeria ba , my lovely babu abinda za'ayi karka damu cewar Diyana killer smile Kamill yayi yasan yafara sata a layi kafin ya goce ta .

RANAR ƊAURIN AURE
Da safe misalin ƙarfe bakwai yan uwan momy suka sata gaba wai gashi biki na yar fari amma babu wani wasa da akayi , momy da ta jiyosu tace " ku ƙyaleta karku damu Allah dai yabasu zaman haƙuri kowa ya amsa da amen .
Zuwa ƙarfe goma angama tsarawa Diyana kwaliya ta haɗe cikin material less mai tsada anyi mata ɗinkin riga da sikel ba ƙaramin kyau tayi ba ,
wasu magunguna aka dinga ɗura mata da turaruka momy da momyn Khady suka faɗa mata inda zatayi dasu ,
Zuwa sha ɗaya Kamill ya kirata ya sauka a garin kano , wani irin farinciki takeji na daban , iskar ma da take kaɗata ta ranar ta daban ce ,

[

A yau dubban mutane suka sheda ɗaurin auran Kamill Safiyan da amaryarsa Diyana Sani , ɗaurin auran da yasami halartar manyan mutane ta kowane ɓangare musamman ma ɓangaren mahaifin Kamill , kowa ya sanyawa auran Albarka , Kamill kam bai sanarwa yawancin abokansa ba a cewarsa wanan auren nasa auran hukunci ne sbda yanason tada GUGUWAR ZALUNCIN sa bayan amarya tazo , mahaifinsa duk bai fahimci hakan ba , kayan lefen da aka kawo gidansu Diyana ya girgiza mutane tabbas nera tayi kuka duk cikin kayan babu na 50k momy ma tasha mamaki amma ba'a mamaki da ikon Allah yasata jan bakinta tayi shiru .
Hajiya da tinene sunsha ɗinkin atamfa riga da zani suma ba ƙaramin kyau sukayi ba amma Tinene na gefen Hajiya bata bari tayi nisa da ita .
Bayan sallahar magrib Diyana da Afreeda na hango manne da juna sunata kuka kowacce idanunta fal da hawaye , momy da ta shigo kiran Diyana ta gansu a haka , itama kawar da kanta gefe tayi tana share hawayen daya zubo mata daughter kizo dadynku na nemanki , daga haka momy ta fice , sakin juna sukayi Diyana ta tafi kiran dady .
Da sallama ta shiga palon dady kanta a sunkuye , kallon tausayi dady yayi mata yasan tayi masa biyayya kuma shima yana son ya kwatanta kyautata mata ,
Dady gani , ywwa daughter abinda nakeso kisani aure ibada ne yinayi bari na bari karki maida gidan auranki gurin cin kasuwa kokuma filin faɗa da miji karkiga dan bai baki kulawa kina waje kice inkin shiga ciki bazaki bashi kulawa ba , kizamo mai tausasa murya ga mijinki kizamo mai tausayinsa kizamo mai faranta masa kamar inda kika yimin biyayya Allah yabaki yayya masu albarka masu biyayya , cikin muryar kuka Diyana tace " dady ka yafe min.
Dagani kasan ƙarfin halin magana yakeyi yace " na yafe miki Diyana .
yayi mata umarni da ta tafi , tana tafiya tana kuka wata yayar momy ta jata zuwa part ɗin momy , nan ma nasiha suka yimata mai ratsa zuciya kowa tausayinta yakeji kasancewar labarin auran da akayi mata ,
9:pm motar ɗaukar amarya ta ƙaraso tayi wanka ankuma shiryata jikinnan kamar anyi ɓarin turare , duk inda ta zauna ƙamshi ke tashi sai ta barmusu tsaraba ,
rabuwa da momy ba ƙaramin kuka tayi ba sbda sabo turken wawa , Afreeda gata ga amarya suna riƙe da hanun juna , Hajiya cewa tayi bazataje ba sai daga baya zataje taga gida a nutse ,
sunyi tafiya mai nisa sosai sanan suka shigo anguwar da dadyn Kamill ya siya masa gida , tun daga nesa suka hango gidan shi kaɗai , gashi ba wani ƙato sosai ba amma nera tayi kuka , horn drivern nasu yayi aka buɗe masa get ya shige dasu , yana parking wata ƙanwar momy tace " fito da ƙafar dama kiyi bismillah , tana fitowa itama ganin tsaruwa da kyan gidan yasata sunkuyar da kai gefen zuciyarta tanajin tayi sa'ar miji , mai kula da ita ,
rungumeta sukayi kai tsaye suka kutsa cikin gidan gaskiya inhar nace zan tsaya misalta kyan gidannan bansan irin misalin da zanyi muku ba ku ƙaddara gidannan kamar irin ginin turai bedrom aka shige da ita aka zaunar da ita akan gado , cigaba sukayi dayi mata nasiha sanan suka sata tayi wanka ta sauya kaya , suka feshe mata jiki da turare sukabi ko ina na ɗakin da turare mai sanyin ƙamshi ,
Sallama sukayi mata , a lokacin ta gane lallai aure ya wuce tunanin mai tunani , Afreeda da ta kwanta jikinta taba kowa tausayi janta sukayi tare da cewa " yanzu ba'a kwanan gidan amarya kiyi haƙuri kizo muje kiyimata adu'ar zaman lafiya kawai , haka aka janye Afreeda tana kuka suka fice daga ɗakin , kasancewar batada wasu ƙawaye .
Bata gama tsorata ba sai dataga mutane sun watse ita kaɗaice a gidan hankalinta ya fara tashi , miƙewa tayi ta murɗa handle ɗin ƙofar toilet , alwala ta ɗauro sbda batayi magriba da isha ba , tana fitowa ta shimfiɗa dar duma ta tada sallah , bayan ta idar ta kwararo adu'oi ta shafa , lumshe idonta tayi tana mai godiya ga Allah ta ninke dardumar ta koma kan gado ta kwanta kamar wata baby , jin shiru har ƙarfe 10:

yasata janyo wayarta ta lalubo lamar Kamill da tayi seven da my blood danna kira tayi , jin tana ring ba'a ɗaga ba tafara tunanin ko lafiya tunda bai saba yimata haka ba .
Ƙara danna kira tayi a karo na biyu nanma shiru ba'a ɗaga ba , ajiye wayar tayi tare da fashewa da kuka dama idanunta sun kuɓbura daƙyar take buɗesu , shiru shiru har ƙarfe sha biyu na dare , lokacin ma bacci mai nauyi yayi gaba da ita sbda gajiyar biki.
Zaune yake a guest hause ɗinsa dake kano , tofa masu karatu ango baya Abuja yana ma kano .
bacinsa yake shara hankalinsa a kwance kamar ba ango ba bashi ya farka ba sai wajen asbha lokacin anata kiraye kirayen sallah daga ma ban bantan masallatai , kasancewar akwai masallaci a gidan yasashi nufar masallacin .
Har akayi sallahar asbah Diyana na bacci ba ita ta tashi ba sai ƙarfe bakwai na safe , a firgice ta sako daga gado tare da nufar toilet tayi brush ta ɗauro alwalah tafara sallah tana idarwa ta koma ta kwanta inka ganta abin tausayi .
Kogin tunani ta shiga to ina my blood tamayar da take yiwa zuciyarta kenan , babu mai bata amsa yasata janyo filo ta rungume tare da share yar kwallar data zubo mata.
Wayar ta ce tafara ruri cikin sauri ta janyo wayar ta ɗauka Kamill ne mai kiran hakan yasata gyaran murya , tana duba fuskar wayar taga my sis cikin ƙarfin hali ta kara a kunne tare da cewa" yar uwata yakike ? ya momy da dady , Afreeda dake dariya tace " kowa lafiya dafatan dai amarya na cikin ƙoshin lafiya , normal sis ina lafiya yaushe zaki zo ? zaro ido Afreeda tayi kana tace " kema kinsan ba barina fita za'ayi ba amma karki damu inanan zanzo cikin satinnan , daga haka sukayi sallama .
tashi tayi tafara zagaya ko ina na palon babu laifi nera tayi kuka kuma ko ina ƙamshi ke tashi ga kayan kallo nagani na faɗa , haurawa step tayi tana mai ƙarewa fentin kallo kai kace yar ƙauye , ɗakuna uku ne a saman,
Na farkon tafara buɗewa wani fitinannen ƙamshi ne ya daki hancin ta batasan lokacin data kutsa kai ciki ba ,
Hoton da tagani ne yasata faɗi jugub cikin firgici da tashin hankali tafara nuna hoton da yatsanta tana cewa " kardai shine , wayo nashiga uku na lalace badai shine mijina ba dady bakuyimin adalci ba inhar shine baku sanar dani ba , kuka takeyi tana matse kanta lokaci ɗaya ciwon kai yayi mata sallama , amma har yanzu bata dena kallon hoton Kamill ba .
ƙara nuna hoton tayi a karo na biyu tare da cewa " natsaneka na tsaneka bana sonka bana ƙaunarka takuma fashewa da kuka mai ban tausayi , jan ƙafafunta tayi da suke neman ƙin ɗaukarta ta nufi ƙasa nata riƙe da kai , bata sami damar ganin sauran ɗakunan ba tayi gamo da ɓacin rai, gado ta faɗa zuciyarta fal baƙinciki inta tuno maƙiyinta shine mijinta lallai akwai aiki tasan auran hukunci yayi bawai na tsakani da Allah ba , tabbas shine mai kirana a waya tabbas shine , magana takeyi kamar zararriya tana riƙe da kanta har yanzu .
Bayan tagama juye juyenta bacci mai nauyi yai nasarar ɗaukarta , baccinta takeyi cike da mafarkai iri iri duk na Kamill dakuma yanayin zamansu .
sai ƙarfe ɗaya ta farka tana tashi yunwa tayi mata sallama , kitchen ta nufa cikin sanyi jiki ta buɗe handle ɗin ƙofar ,komai akwai a kitchen ɗin babu abinda babu , in baku manta ba dama ba gwanar cin abinci bace , fridge ta buɗe shima cike yake da lemu kala kala , nutrimilk ta ɗauka mai sanyi ta koma kitchen ta ɗauko cake ta ɗora kan plet ta dawo palo tafara ci , bawani daɗi yake yimata ba amma saboda yunwar data addabeta yasata maida hankali ga ci .

Zaune momy suke a dining kowa da sakwara a gabansa da miyar egusi da naman kaza gefen kowanen su shayi ne mai kauri gakuma bredi da wainar ƙwai .
Hajiya dake kan kafet a zaune ita da Tinene ta dubi dady tace " Alhaji gobe in Allah ya yarda zanje gidan wanan zabiyar in dubota , to Hajiya dady yace " yaƙara da cewa " Allah ya tsare hanya driver zai kaiki , dady nima zani cewar Afreeda Allah ya tsare dady yace " musu momy kam tunda ta tashi takejin jikinta babu daɗi tanajin kamar

akwai abinda ke faruwa da Diyana kasancewar ta mai zurfin ciki yasata yin shiru batare da ta gayawa dady ba .
Haka dai suka gama breakfast ɗinsu kowa ya watse .

yau kwanansu biyu da aure ko leƙowa bai yi ba ,a iya kwana biyu Diyana ta rame sosai fuskarta babu wani farinciki kana ganinta zaka gane .
Sallamar su Hajiya ne yasata amsawa cikin fara'a niko nace aure mai gyara hmm .
Guri Hajiya da Tinene da Afreeda suka nema tare da kallon Diyana dake zaune da remote a hanunta , bayan sun gaisa Hajiya tace " yarnan mai yaja miki rama haka ? kinfara nuna masa halinki na ragwanta da raki ko ?" sunkuyar da kai Diyana tayi dan bazata iya sanar da wanan tsohuwar damuwarta ba , miƙewa Afreeda tayi ta koma kusa da ita suka rungume juna , tashi ki kawo musu wani abin akwai drinks a fridge ɗauko musu kiduba kitchen akwai cin cin.
Riƙe baki Hajiya tayi tare da cewa kinci gidanku ta watsawa Diyana daƙuwa , waye yace "miki yanajin yunwa kokuma kawo ko bazanci ba sai naci ehe ,Diyana ba surutun Hajiya ne a gabanta ba hakan yasa ta gyara kwanciya a doguwar kujerar da take zaune tayi matashi da cinyar Afreeda .
Riƙe baki Hajiya tayi bata ƙara cewa komai ba , ta miƙe tare da juye abinda Afreeda ta ɗebo a gaban hijab ɗin Tinene ,to kitaso mu tafi inkuma kinzo zaman ɗaki ne sai muji , Hajiya tace tana shirin ficewa , miƙewa Afreeda tayi idanunta sun ciko da hawaye tace " my sis sai munyi waya .
Kasa magana Diyana tayi saboda kukan da ya ƙwace mata , tanaji tana gani suka tafi suka barta a gidan da shida kurkuku duk ɗaya.
Yau kwaanta uku a gidan bayan tayi sallahar Azhar ta jingina kanta da gado tun tana wani tunani daban har bacci yai nasarar ɗaukarta , jin an watsa mata ruwa mai kamada na ƙanƙara yasata saurin buɗe ido ta miƙe cikin tsoro , Kamill ne tsaye yana sanye da shadda fara tasha aiki kannan yasha hula sajens luf luf ba ƙaramin kyau yayi ba , wayabaki lokacin bacci a gidana ? cikin tsiwa Diyana ta taɓe baki kana tace " inbanyi bacci ba mai kakeso nayi ? ke karki kuskura kiyimin rashin kunya dan ni da kike ganina ina hukunta marasa kunya so ki kiyaye kisan ko da wa kike magana , taɓe baki takuma yi a karo na biyu tace " mtsw har ya ɗaga hannu zai kai mata mari ko mai ya tuna oho sai ya fasa ya fice daga ɗakin
Part ɗinsa ya wuce ya watsa ruwa kana ya fito ya shafa mayukansa masu ƙamshi ya nufi drower ya ciro gajeren wando da farar singlet ya sanya , ɗaukar wayoyinsa yayi kana ya sauka ƙasa , yana sauka yaji wani ƙamshi mai daɗu ya bugi hancin sa , leƙe ya shiga yi ta ina ne jin ko ta ko ina ƙamshin ke fitowa yasa shi nufar ɗakin Diyana cikin ƙasaita ,
samunta yayi a kwance kan gado hawaye sun bushe a fuskarta keee...! tashi ki dafamin indomie Diyana da takejin maganar kamar a mafarki ta kuma juyawa tana gyara kwanciya , fincikota yayi tare da cewa " gidanku babu manya ne ? karki manta yazu daga ni sai ke a gidannan so kuma kinsan matsayina a gurinki ko kin mance my blood ɗinne yau ? kuka Diyana ta fara mai sauti tana cewa "wlh ka cuceni Allah sai ya sakamin danasan kai ne zaɓin da iyayena sukayi min wlh bazan amince ba , zama gefe gado yayi tare da janyota yana riƙe da bakin maganar yace " sai kuma gashi kin yarda kuma inyi abinda nakeso dake , runtse ido tayi tana tuno irin tsanar da tayi masa tabbas bazata taɓa son sa ba koda nan gaba.
Ƙara matsowa yayi kusa da ita suna jin nunfashin juna yace " baby tashi ki dafamin indomie kuma wlh nabaki 3mins zaro ido Diyana tayi dan wanan lokacin yayi kaɗan , tunowa tayi to inma bata dafa ba uban me ya isa yayi mata , yana ficewa ta koma ta kwanta,kamar daga sama taji saukar bulala mai tsafi , innalilahi ta ambata cikin muryar kuka .
Mai nayi maka ? jaka aka kawo maka? to wlh ka kuma dukana ka gani, duk wanan maganar da Diyana takeyi idanunta a rufe , janyota Kamil yayi haɗi da cigaba da janta har hanyar kitchen , haka tadinga jin zafin janta da yayi a step ga kurjewa da tayi bugu da ƙari ƙarfinsu ma ba ɗaya ba , tayi iya yinta gurin ganin ta ƙwace amma

abin ya citura , babu tausayi ko imani ya wurgata kitchen yana mayarda nunfashi tare da gurnani kamar zaki , oya ki wuce ki dafamin ko inyi miki abinda yafi haka , babu shiri Diyana ta miƙe bakinta da guwai war hanunta duk ya ƙuje ta kuna gas kana ta ɗora ruwa yana tafasa tasa komai tare da mangyaɗa da sauransu , sai da ta juye a plet ganin baya kallonta ta zabga gishiri a ciki ta miƙa masa , banza kalmar da ta fito daga bakinsa kenan , sai da Diyana ta ruga da gudu tace " ai ba'a banza ɗaya sai dai biyu ta shige bedroom tana cigaba da kuka tare da murɗa key ɗin ƙofar.
Kwafa yayi dan yasan bakinta ba mutuwa zai yi ba , dining ya nufa ya zauna tare da ɗaukar cokali ya fara juya indomien lomar farko yaji ɗan karen gishiri kamar iya shine a abincin , Diyana ....bazaki fito ba wlh yau sai kin gane bakida wayo uban wa yace miki haka ake girki ? shiru batare da ta amsa ba ya sashi ƙara tunzura yana huci ya haura up step , kai tsaye ɗakinsa ya nufa ya faɗa gado zuciyarsa nayi masa saƙe saƙe , ring ɗin wayarsa ne yasa shi ɗago kai ya nuba mai kiran nasa Abba ne , Kamill yace " tare da ɗaukar kiran ya kara a kunne , Aslamu alaikum Abba barka , cikin farinciki Abba yace " dafatan kuna lafiya ya ɗiyata ? tana lafiya Kamill yace " to masha Allah ka nutsu my son yanzu kayi aure fa .
To insha Allah Kamill yace " daga nan sukayi sallama .
Kwanciya yayi kansa na kallon sama yana tuno kalar muguntar da zai sake yiwa Diyana a karo na biyu , daga haka bacci mai nauyi yayi nasarar saceshi , jinshi shiru yasa ta buɗe ƙofa ta fito saɗaf saɗaf tayi kitchen flaks ɗin ruwan zafi ta ɗauka kasancewar tunda masu kawota suka cikashi da tafasashen ruwa batayi amfani dashi ba , ɗibo kayan haɗa tea tayi da duk wani abinda zata buƙata harda ragowar cake ɗinta da butter duk ta kawosu ɗakinta ta jeresu kan bedsite ɗinta kana takuma dannawa ƙofar key , haɗa shayinta tayi mai kauri tanasha tana gutsirar cake , da haka har ta ƙoshi sosai , ajiye cup ɗin tayi tare da gyatsa ta lumshe idanunta , tunowa tayi rabonta da waya da momyn ta tun safe dan haka ta ɗauki wayarta ta danna number my mom , ring ɗaya momy ta ɗauka cikin farinciki tace " my daughter dafatan kina nan lafiya ? eh ina lafiya momy ya Afreeda dakuma wanan tsohuwar ? dariya momy tayi tace " duk suna nan lafiya amma babu wata matsala ko ? naji muryarki babu daɗi ? uhm babu komai Diyana tace " akwai fa naji muryarki ta sauya ni mahaifiyarki bazaki sanar dani ba ko to wa zaki gayawa ? kuka Diyana ta fashe dashi dan zuciyarta ta tsinke da kalamin momy.
Bankaɗo ƙofar da taji anyi ne ya hanata gayawa momy halin da take ciki , bata ankara ba taji an fizge wayar daga hanunta , Aslamu alaikum momy ya gida ya aiki yakuma lil sis , dagajin muryar tasan mijin Diyana ne , washe baki momy tayi tace " lafiya lao ya ƙoƙari Allah yayi muku albarka Allah ya albarkaci rayuwarku , amen Kamill yace " tare da cewa mun gode momy muna nan zuwa gobe insha Allah, momy ta mance da maganar su da Diyana cikin farinciki sukayi sallama da Kamill .
wurgo mata wayar yayi Allah ya temaka bata faɗi ƙasa ba , tare da cewa " wlh duk ranar da naji kin gayawa wani yanayin zaman mu sai na illata ki , lumshe ido tayi batare da ta kalli inda yake ba , sai da ya gama surutansa sanan ya fice .
Washe gari bayan sallahar ashba garin ya tashi da sanyi mai shiga jiki kwance Diyana take a bed ta ƙudun dune da blanket sai kwasar baccinta takeyi .
Tunda Kamill ya dawo daga masallaci yake jinsa cikin wani yanayi , ɗakinsa ya wuce yana rawar sanyi , idanunsa sun kaɗa sunyi jawur dama a dai dai wanan time ɗin yakeda buƙatar mace " a duk lokacin da gari yai sanyi to baya cikin kwanciyar hankali ,ga gararsa kwanciyar tayi ya dawo palo ya kwanta yana rawar sanyi , haƙoransa babu inda baya rawa ga wani wahalalen nunfashi dayake sauƙarwa .
Kamar an tsikari Diyana ta miƙe tare da buɗe ƙofa ta fito palo ko me take nema oho , jiyo sautin sauƙar wahalalen nunfashi ya sata ƙarasawa da gudu domin taga waye , Kamill ne kwance jikinsa nata ɓari , abinka da mace mai tausayi sai ta tallafo kansa ta gyara masa kwanciya tare da miƙewa ta nufi ɗakinta ta haɗo masa shayi mai zafi ta kawo masa , tashi kasha , jiki na rawa Kamill ya fara shan shayin cikin ikon Allah zufa ta fara keto masa ta ko ina yadena jin sanyin , tunda Diyana ta tabbatar ya dawo

hayyacin sa ta janyeshi tare da cewa " kaci darajar tausayin da Allah yasa min amma badan haka ba babu dalilin da zai sa in temakeka taja tsaki.
Kamill dai jiki babu ƙwari dan haka bai kulata ba ya maida kansa ya kwanta ,
Zuwa ƙarfe goma da rabi yaji sauƙi sai ciwon mara dake ɗan damunsa , haka dai ya haura zuwa ɗakinsa yai wanka ya sauya kaya sai ƙamshi yake zubawa dole duk macen da ta gansa sai ta yi sha'awar ya kasance mijinta , fararen kayane a jikinsa ta baƙar hula mai adon farin zare ga tsadaden agogon sa da takalminsa fari , sakowa yakeyi a hankali kamar ba shine mai rashin lafiya ba , direct ɗakin Diyana ya dosa ya murɗa handle ɗin ƙofar cikin sa'a ta buɗe , zaune ya sameta tana makeup itama fa tayi kyau sosai ta haɗe cikin baƙin leshi mai adon jan flawoyi tagama shafa powder tana shafa pink ɗin janbaki ɗakin ya game da ƙamshi , tsayawa Kamill yayi yana ƙare mata kallo cikin zuciyarsa yana cewa " gaskiya da auran soyayya mukayi da na more wanan mai zan so a jikinta mtsw ya kauda tunanin da ɓacin rai ,
Baiyi magana ba ya fice itako tun shigowar sa tana kallonsa ta mirorr bata kulasa ba , ɗage kafaɗa tayi irin ko a jikina ɗinnan .
Ba'a jima ba taji ƙarar tsayawar motarsa tasan shine ya dawo , kuloli ne masu kyau a hanunsa guda biyu ya nufi dining dasu ya jere su tare da ɗauko su fanta da 5alive da sauransu ya ajiye , kuma komawa ɗakin Diyana yayi wanan karon harda sallama , amsawa tayi cikin siririyar muryarta , zama yai a gefen bed tare da cewa am sorry mata ta kiyi haƙuri da dukkan laifukan da nayi miki nasan ban kyauta ba , nan danan zuciyar Diyana ta karaya kasancewar ta mai saurin fushi dakuma tausayi uwa uba ga son a risina mata, bakice komai ba my Diya? sharesa tayi tana ƙoƙarin miƙewa , janyota yayi ta faɗa jikinsa suna jin ninfashin juna ya kai fuskarsa kan tata tare da cewa nayi miki magana tare da bada haƙuri kinƙi kulani ko kinason Allah yayi fushi dake ? tuno nasihar su momy da dady tayi cikin karayar zuciya tace " na haƙura wata irin runguma ya kai mata tare da manna mata kiss a kumatunta , munada baƙi fa , waro ido Diyana tayi tare da cewa " mai za'a dafa musu ? no nasiyo kawai inason ki zama cikin shiri , oky Diyana ta faɗa da murmishi ɗauke a fuskarta.
[23/06, 9:45 pm] Mom Islam Ce: 25 & 26

Yana shirin fita wayarsa tayi ring number abokinsa ke yawo a screen ɗin wayar , amsawa yayi tare da sallama yace "Nasir kun iso ne ? daga can ɓangaren naji ance gamu nan shigowa muna bakin get , ok Kamill yace " ya ajiye wayar .
ɗauko turare yayi ya feshe Diyana tare da cewa " yakamata kiyi wanan murmishin mai kyau lumshe ido Diyana tayi tana ƙarewa bakinsa da yake mata magana kallo .
Suna haka sukaci ana ƙwan ƙwasa ƙofa , da sauri Kamill ya fita ya taro su yana yimusu sannu da zuwa kasancewar su biyu ne shida matarsa Fadila , iso yayi musu zuwa inda zasu zauna , Nasir na zama yace " aboki ina amarya ne nifa kasan akwai surutu , dariya Kamill yasa yace " karka damu amarya na ciki tana fitowa inaga ko kunya ce ta hanata amma barinje ina zuwa , daga haka Kamill ya miƙe ya nufi bedroom ɗin Diyana samunta yayi da waya a hanun ta tanata ɗaukar kanta a photo , eyee Kamill yace " tare da zama ya rungumeta yafara yimusu salfe , oya tashi suna son ganinki , kukan shagwaɓa Diyana ta fara tana cewa " nikam kunyarsu nakeji , sorry my Diya kawai ya sunkuceta ya goya kamar baby ya kawo ta palo ya zaunar da ita kan kujera yana cewa " to munzo Nasir ga amarya ta iso , dariya Fadila da Nasir suka sa Fadila tace " mu ba baƙi bane Diyana , tun Diyana na noƙewa har ta sake suka gaisa suka fara hira , miƙewa Diyana tayi tafara jido musu kayan abinci tana jere musu , masha Allah sunci babu laifi sukayi godiya , Fadila ce ta kamo hanun Diyana tace " zomuje Nasir da baki baya shiru yace " mata iyayen gulma zaki koya mata halin naki ko ? suka kwashe da Dariya , suna cikin tafiya Fadila tace " inane bedroom ɗinki ? gashi nan Diyana tace " cikin jin kunya.
Shigewa sukayi Fadila ta rufo ƙofar tare da zama a gefen gadon Diyana .
sunana Fadila wanan mijina ne wato yaya Nasir Allah bai bamu aihuwa ba kuma har yanzu bamu fidda rai ba , muna zaune a garin kano nima yar Kano ce .Allah sarki Diyana tace " Allah ya baku masu albarka , Fadila ce ta amsa da amen , janyo hand

bag ɗinta tayi kana tace " bamu sami damar yimuku tsaraba ba amma ke nayi miki , tunda naji sunanki Diyana sunan sis ɗita ne , murmishi Diyana tayi .
Fadila ce ta miƙawa Diyana wata ƙaramar jaka mai ɗauke da tsadadun humra da magunguna , duk da batasan ko maganin meye ba tace " nagode , Fadila ce tayi dariya kana tace " tun banyi miki bayani ba ? kinga wanan turaren a fuska ake shafawa inhar kinsan Kamill na gida karki sake ki shafa in zaki fita , to Diyana tace "ɗago wani turaren tayi a yar wata kwalba tace " kinga wanan turaren a ƙasan mararki in zakije gurin oga , rufe fuska Diyana tayi alamar jin kunya , akwai millk? eh Diyana tace " Fadila ce tace " ɗauko guda ɗaya , kasancewar ta kwaso kayan tea ɗin ɗakinta yasa ta miƙowa Fadila da cup ɗin da ta buƙata , ta koma ta zauna tana kallon Fadila ta fasa madara ta juye tare da garin maganin nan dakuma wani haɗin dabino ta cewa " Diyana ungo ki shanye , no bazan shaba Diyana tace " idanunta sunyi rau , pls kisha bazan kawo miki abinda zai cutar dake ba wanan haɗin da kike gani ba a siyar dashi a nan kasancewar kayan suna yiwa masu magani wuya daga Nigar yake , nifa anty kiyi hakuri dan kona sha ma ....ta mance da wa take magana ta rufe fuska tare da juyawa , dariya Fadila takuma yi a karo na biyu tace " a taƙaice dai kice Kamill bai karɓi haƙkinsa ba ? eh Diyana tace " sai kuma tayi shiru , to yanzu meye matsalar kece ko shine ? shine Diyana tayi saurin faɗa , maiya haɗaku ? ba auran soyayya kukayi ba ? a ' a gaskiya baya sona nima bana sonsa , innalilahi Fadila ta faɗa cikin mamaki , ga yanayin ku yana nuni kamar kuna son junanku ? uhm Diyana tace " dan maganar m ta isheta , to kwantar da hankalinki nayi miki alƙawarin sai Kamill yazo yana baki haƙuri amma tunda nariga na haɗa maganin nan kisha ƙila yau ya nemi haƙkinsa , nifa ba so nakeyi ba , Diyana tace " tana cuno baki , ke bakisan maza sai da lallami ba ko ? Fadila ta faɗa tana kallon Diyana daƙyar ta samu Diyana ta shanye wanan magani tass , Fadila ce ta jiyo ring ɗin wayarta tana duba mai sunan my lovely ne ya sata miƙewa tare da cewa " bani number ki , gaya mata Diyana tayi kana Fadila ta fice tabar Diyana , juyi Diyana takeyi a ɗakin tarasa mai zata bawa Fadila dan jininsu ya haɗu , ɗauko wani ƙaton turare na kwali tayi a akwatinta mai tsadar gaske tasa cikin leda ta yafo gyale ta fito dashi , samunsu tayi a tsaye suna shirin tafiya , Nasir ne yace " amarya bakya lefi kokin kashe ɗan masu gida , dariya Fadila tasa tace " bata kashe ba dai da anyi mata hukunci , Diyana dai tana riƙe da leda a hannu sai da taji suna cewa " to mun barku lafiya Nasir ya ajiye kuɗi masu yawa a kan kujera yace " abawa amarya , godiya sukayi masa kana duka suka fice , cikin sanyin jiki Diyana tabi bayansu dan ji takeyi kamar sun daɗe da Fadila , su Fadila na shiga mota ta ɗora mata ledar a cinyarta ta juya idanunta cike da hawaye , tana shiga bata tsaya ba ta wuce bedroom ɗinta ta faɗa bed tare da sakin kuka mai ban tausayi Allah yasa rayuwar auranta ta ɗore cikin farinciki tabbas inhar Kamill da gaske yakeyi to ta zubar da makaman yaƙinta zata farantawa iyayenta.
bacci mai nauyi ne yai masarar ɗaukarta ba ita ta farka ba sai misalin ƙarfe biyar na yamma ta jita a jiƙe kamar tayi fitsari , tuno maganar Fadila da tace " mata zataji hakan yasata miƙewa ta nufi toilet takumayin wanka ta zauya kaya , iya mai kawai ta shafa sai turare mai ƙamsi ta fito palo , bata sami kowa ba tunani ta fara kodai Kamill bai shigo bane tun fitarsa ta ɗazu ? batada mai bata amsa ya sata yin shiru ta nufi kitchen taliya jollof ta ɗora wacce taji kifi da kayan ƙamshi nan da nan gidan ya game da ƙamshin abincin Diyana , ta iya girki amma batayi a gidansu kasancewar abinci ba ya cikin lissafinta wanan ɗin ma dan ta farantawa Kamill tayishi, sai da ta gama ta wanke komai kana ta fito dasu ta dawo palo ta zauna tana mayarda nunfashi , yanzu kuma mamaki takeyi wai itace take wanan hidimar taɓ wanda da a gida ne ko nawa za'a bata bazatayi shi ba , kawar da zancen tayi ta miƙe ta nufi bedroom ɗinta , shiru shiru Kamill bai dawo ba har akayi magrib ,sai bayan isha'i sanan taji nocking cikin sauri ta miƙe tana rawar jiki ta iso palon , oyoyo my blood ka dawo lafiya ? haɗe rai Kamill yayi kamar an aiko masa da ranar mutuwarsa kana yace " dallah bani guri , mamaki ne ya cika Diyana a tunaninta ya bata haƙuri ai yanzu zama zasuyi na soyayya duk da iya kyanshi ke birgeta.

Tsayawa tayi sororo tana kallonsa da mamaki kusan tureta yayi ya wuce kamar zai tashi sama , mayarda ƙofar tayi tasa key kana ta nufi bedroom ɗinta ta kwanta ta kifa kanta tana kuka , mai yasa na damu dashi ? mai yasa nake yawan tunaninsa ? a iya sanina auran bana soyayya mukayi ba yakamata na fita harkarshi kar ya raina ni lol , duk ita kaɗai take wanan surutun
[24/06, 9:52 pm] Mom Islam Ce: 27 & 28

Mamaki da tuno lallaɓar da yayi mata tayi oh dama ashe haka maza suke ? ta tambayi kanta tana shirin miƙewa , jin ring ɗin wayarta ya sata dawo da baya dan ganin mai kiran , number Fadila ne da tayi seven da anty Fadila , ɗauka tayi tare da cewa " barka anty kun isa gida lafiya ? barka my lil sis wlh muna nan Abuja gidan ƙanin dadyn shi so ya oga , share hawayen da suka zubo mata tayi tace " tunda ya fita ban sashi a ido na ba sai yanzu nayi masa sannu da zuwa harda girki ko saurara ta baiyi ba , kusan tureni ma yayi , a 'a 'a anty Farida tace " tare da riƙe baki kamar suna tare , Diyana
Fadila ta kira sunanta , na'an anty , Fadila ce tace " yanzu yana ɗakinsa ne ? eh Diyana tace " tana jiran abinda Fadila zata faɗa mata , ki tashi kiyi wanka ki shafe jikinki da wanan humarar dana kawo miki ,ki shafa wanan turaren a fuskarki , to Diyana tace " cigaba Fadila tayi da cewa " kisami Sleeping dress mai kyau wanda zai bayana komai na jikinki kisa shima ki feshe shi da turare , kije gurinsa cikin murya mai sanyi kiyi masa kalami mai daɗi tare da ɗan shigewa jikinsa , taɓɓ Diyana tace " to bazai saurareni ba kinaso in dawo da tabo kenan bazan iya ba anty , no ƙanwata zaki iya inkinsa kanki karkiji komai inda kukayi ki kirani ki gayamin , to kawai Diyana ta iya cewa dan a halin yanzu bazata kuma yarda da shirya warsu ba , daganan sukayi sallama Diyana ta ajiye wayar tana ta tunanin maganar anty Fadila ,ta shafe lokuta a zaune a gurin har dare yayi nisa ta miƙe ta dannawa ƙofar key tare da yin adu'ar bacci ta kwanta , washe gari da safe bayan ta gyara gadonta tayi wanka ta sanya gajeran wandon jeans da riga ves mai siririn hannu rigar iya cibiyarta ta kifa cikinta a gado tana tuno rayuwarta ta gida , cikin farinciki , tunowa tayi Kamill yayiwa momy alƙawari zasuzo tun jiya amma bai kuma magana ba ,
Fitowa tayi tana shirin hawa up step sai kuma ta fasa tana ganin kamar zai wulaƙanta ta kuma tanson zuwa ganin momynta , wata zuciyar ce ta ingiza ta , cikin takunta a hankali ta haye zuwa ɗakin nasa da sallama ta tura door ɗin bataga kowa ba hakan ya bata damar shiga kai tsaye , kasancewar babu kowa a palo yasa ta shiga bedroom ɗinsa batare da jin tsoro ba , samun sa tayi a kwance yayi rup da ciki yana juyi idanunsa sun sauya launi , murmishi tayi kuma ta ƙudiri aniyar yau ɗinnan sai ta gigitashi amma bazata bari ya fiddata daga matsayinta na budurwa ba har sai lokacin da soyayyar su ta ɗore sosai , my blood Diyana ta faɗa da cold voice ɗinta hakan kuwa yakuma sa Kamill cikin yanayi , yafara kiranta a wahalce my Diya pls help me dan Allah zan mutu ki temakawa rayuwata , yau kam Kamill bai bata tausayi ba tunda bai san mai ake kira da hakan ba , kai tsaye taje gareshi tare da yi masa rumfa da ƙirjinta ɗago hanunsa tayi taji ya sakesa sharab hakan yasa ta tabbatar da bashida wani power a jikinsa good Diyana ta faɗa a cikin ranta , mirginoshi tayi kamar ƙaramin yaro ta haɗe bakinsu guri ɗaya , wani ƙamshi da ya ziyarci bakinta mai kamada na flevor yasata lumshe ido , Kamill abin nema ya samu yafara wasa da komai na jikinta yana fitarda nunfashi ƙasa ƙasa, itama wani yanayi ne ya ziyarce ta wanda ita kanta batayi tsammani ba , jin yana yimata wasu abubuwa wanda yake neman tarwatsa ƙudirinta yasata yin azama ta fizge da sauri tayi hanyar fita , pls my Diya ki temakeni karki tafi ki barni dan Allah , duk wanan surutan nasa basuyi tasiri a zuciyar Diyana ba sai ma dawowa ɗakinta da tayi tana maida nunfashi gashi jikinta duk ya yi sanyi ga ɓata jikinta da tayi , toilet ta shige ta haɗa ruwan wanka mai ɗan tsafi ta daɗe tana wankan zuciyarta cike da tunani iri iri , shin wai itace tayi wanan aika aikan ? anya idan Kamill ya fito bazai hukunta ta ba ? gashi yanada extra key na ɗakinta nashiga uku ni Diyana ko a mafarki ban taɓa tunanin zan iya haka ba .

Duk ita kaɗai ke wanan lissafin haka ta kwanta bata sa komai a cikinta ba , washe gari bataji motsin Kamil ya fito ba , tunani tafara kodai bashida lafiya ne oho ta bawa kanta amsa , karma inje in tarowa kaina masifa , ta shige kitchen tare da ɗora ruwan zafi ta soya ƙwai da bredi ta juyo a plet gakuma ruwan zafin a cup , jin kamar motsin mutum ya sata juyawa , ganinshi tayi yana mirginowa duk yabi ya rame kamar wanda yayi sati yana ciwo , ba shiri ta mayar da plet ɗin da cup ɗin nata ta dawo gurinsa ta tsuguna tare da cewa " bakada lafiya ne ? girgiza mata kai yayi alamar eh, to barin kira driver a wahalce Kamill, yace " ban saki ba waro ido Diyana tayi tana mamaki irin wulaƙanci na Kamill da har za'a temaka masa yake hanawa , haɗomin ruwan zafi da lipton kisa lemon tsami , sai da tayi kamar bazata je ba sai kuma ta tafi ta haɗo masa ta kawo tare da temaka masa ya zauna yana riƙe da mara , miƙa masa cup ɗin tayi tare da barin gurin takoma kitchen ta kwaso plet ɗin da ta mayar da cup tayi ɗakinta , Kamill na kallonta ta wuce , mayarda hankali yayi gurin shan shayin nasa cikin ikon Allah ya haɗa zufa ciwon marar ya lafa masa , a hankali ya miƙe ya sauka ƙasa a daddafe ya dawo palo ya kwanta akan 3siter .
Diyana na ɗaki sai da ta cika cikinta sanan ta janyo fillo ta kwanta .

Zaune momy da dady dakuma Hajiya da Tinene suke a palo Afreeda na zaune a gefe tana game a wayarta , Hajiya ce ta dubi dady tace " Alhaji zamuje dubo wanan zabiyar gobe , dady ne ya katse Hajiya da cewa " Hajiya kubari sai an kwana biyu man , faɗa Hajiya ta kamayi wai dady zai hanata zumunci , bayan sun gama momy ta dubi Hajiya tace " Hajiya mijin yace " suna nan zuwa , riƙe baki Hajiya tayi tare da jinjina kai kana tace " uhm wato yau naga surukar zamani to ko yanzu zasu zo sai naje garama ku ƙyaleni , zan tafi da Tinene ta dinga yimata wanke wanke , buɗe baki dady yayi suna haɗa ido da momy tayi masa alama da yayi shiru , momy tasan Diyana ba yarda zatayi ba shiyasa bata kula zancen ba.
Afreeda kam duk wanda yai magana take kallonsa dan kwana biyunnan ji takeyi kamar sis tanta na cikin wani hali , gudun karta fuskanci ɓacin rai a gurin Dady ya sa bata tambayeshi zuwa gidan ba , amma tunda Hajiya zataje itama zata bisu su tafi insha Allah .

Zuwa azhar jikin nasa yayi masa sauƙi kiran escort ɗinsa yayi a waya , jinayi yace " kayi min take away na farfesun kaza pls , angma oga , kana ya kashe wayar , bayan wasu mintuna ƙalilan sai aka fara nocking come in Kamill yace " har yanzu yana kan kujerar a zaune , shigowa akayi da wata leda mai kyau mutumin ya miƙa masa , karɓa yayi tare da bashi 5k yace " ga kuɗin mutumin ne yace " oga 2k ne no ka riƙe kawai , godiya yayi masa kana ya fice ,
Shiri Hajiya takeyi na zuwa gidan Diyana , Afreeda kam harta kammala kasancewar simple makeup tayi ta sanya doguwar riga fara mai adon black stone tayi kyau sosai , fitowa palo tayi da takalmin ta hill da pos ɗinta kalar takalmin baƙi da mayafinta a hannu , dakuma cake ɗin da momy ta bata ta kaiwa Diyana dan sun san bazata dinga cin abinci ta ƙoshi ba.
[25/06, 6:56 pm] Mom Islam Ce: 29 & 30

Kamill na gama abinda zai yi ya koma ɗakinsa dan har yanzu bai fara zuwa aiki ba , bayan Diyana ta tashi tayi sallahar azhar ta fito palo fridge ta nufa ko zata sami abu mai ɗan sanyi , cikin sa'a ta sami exotic buɗewa tayi tafara sha sai da ta tabbatar da ta cika cikinta tsaf sanan ta dawo kujera ta zauna tare da kunna tv wani film suka hasko a tasha tauraruwa hankalinta ya tafi a gurin kallon , bata ankara ba taji an ɗauketa cak gashi bataga wanda ya ɗauketa ba , ganin ɗakinta aka shige da ita ya sata shan jinin jikinta da cewa ba kowa bane sai Kamill , yana direta ta ɗago kai tana kallonsa , ita dai sajensa da ƙaramin lip ɗinsa suna birgeta , baiyi mata magana ba sai ma hararar ta daya soma yi , karki sake kiyi tunanin ina sonki ne auran fansa nayi a yayin da zan tada miki da GUGUWAR ZALUNCI na a lokacin zaki tabbatar da koni waye , mtsw Diyana taja tsaki , kana tace " haka kake faɗa kullum ai bansan ka cika

mai ZALUNCI ba har sai kasa na dena nunfashi , kuma nima ɗin banda biyayya mai zai kaini auran ka baka cikin kalar.....wani mahaukacin mari Kamill ya sakar mata tare da cewa ki adana kalamanki kar su gudu su barki na faɗa banasonki wawuya jaka , ya fice cikin zafin rai , kifa kanta tayi tana kuka tare da tunanin inhar ta ɗore Kamill na samun lagon dukanta to wataran zai yumata illa gara ta nemi mafita tun yanzu , wayarta ta janyo ta dubo lambar mom Khady wato aminiyar momynta , mom Khady ce ta amsa da my daughter nayi miki lefi ko ? rabona da gidanki tun biki , uhm kawai Diyana tace " sai kuma kuka daya kubce mata baji babu gani , innalilahi mom Khady tace " maiya sameki ne my daughter kodai babu lafiya ne ? cikin sha sheƙar kuka Diyana tace " momy banason aurannan wlh banaso , ya ilahi momyn Khadi tace " tana shirin janyo jakarta dake gefe dama yanzu ta dawo daga anguwa, ta miƙe da waya a hanunta come dwn daughter gani nan zuwa yanzu , duk wanan maganar da akeyi a kunnen Kamill dake ɗan duniya ne sai ya shigo ɗakin da fara'arsa yana cewa my Diya zoki tayani wanka tare da kashe mata ido , wani mugun kallo ta wurga masa duk da haka bai bi ta kanta ba ya janyota suka faɗa bed yayi mata rumfa da yalwataccen ƙirjinsa , haɗe bakinsu yayi guri ɗaya yana aika mata da saƙonni na musamman kasa hanashi tayi dan tanajin daɗin inda yake sarrafa harshen sa a cikin bakinta , jin yana lalubar breast ɗinta ya sata saita nutsuwarta tana shirin ƙwacewa , shiko Kamill gaba ɗaya ya fita hayyacinsa sai sauke nunfashi yake , suna cikin haka sukaji an turo ƙofa , a razane Diyana tayi namijin ƙoƙari ta fizge daga riƙon da Kamill yayi mata , tabi bayan momyn Khady da ta shigo ta koma palo ta zauna , tana zuwa ta faɗa cinyarta tare da sakin kuka , murmishi momyn Khady tayi tare da ɗago Diyana ta zaunar gefenta .
Wanka Kamill ya shiga a ɗakin Diyana kana ya buɗe wata ƴar drower dake cike da sabbin kayansa ya ɗauko boyel fari mai tsadar gaske ya sanya bai tsaya shafa mai ba ya ɗauko takalmi da wayoyinsa ya fito , kai tsaye palo ya nufo inda ya tarar dasu a zaune Diyana na kuka tana wurga masa harar shiko yana sakar mata murmishin gefen baki , duk abinda sukeyi a idon momyn Khady tana karantar su , durƙusawa Kamil yayi tare da cewa ina yini , cikin sakin fuska momyn ta amsa tace " masa ya aiki anyi taro lafiya , miƙewa Kamill yayi tare da cewa alhmdulilh ya nufi fridge kayan sha ya direwa momyn a kan table ya kawo mata cup , yce " Diyana kizo , ya juya zuwa ɗakinsa kallonta momy tayi tace " tashi kije man ni banga wata matsala a zamanku ba wlh kin tayarmin da hankali ko tambayar dadyn Khady banyi ba na fito , momy bazaki gane bane wlh ...shiittt cewar momyn tashi kije mijinki na kiranki ni zan tafi zan aiko Khady zuwa gobe kuma anjima zamuyi waya , hawaye na zuba a fuskar Diyana tace " momy yanzu bazaki zauna kiji dalilin kukana ba ?" no dalili shine kisani aure ibada ne kowa da haka ya saba kinaso Allah yayi fushi dake ko ? ganin kukan Diyanan ya tsananta yasa momy fita tana cewa sai munyi waya kije mijinki na nemanki, juyowa tayi hankalinta a tashe shin kowa ya kasa fahimtar zaman da takeyi a gidan auranta ne wanan wace irin jarabawa ce ? my Diya tajiyo kiran daga sama batayi ƙoƙarin amsawa ba ta wuce izuwa ɗakin kamill ɗin , ko sallama batayi ba ta tura ƙofar ganinsa tayi zaune da waya a hanunsa yana murmishi , yana jin ta shigo ya ɗago fuskarsa tare da waso mata mugun kallo yace " waye yabaki izinin shigomin ɗaki maza ki fita banason ƙazamin jikinki a ɗakinnan , kai ka kirani cewar Diyana kifita nace ....cikin tsawa yake yimata maganar mamaki da al ajabi sun hana Diyana matsawa mutum kamar aljan yanzu ya gama kiranta da muryarsa mai daɗi harda yimata murmishi amma yanzu tazo yana wulaƙantata , bazaki fita ba ko nan ɗakinki ne ? ok zonan na gane sai kice min kina buƙatata ne kin kawo kanki , har yanzu dai Diyana na tsaye batace " komai ba sbda lamarin yafara bata tsoro anya bashida aljanu ? ta tambayi kanta ashe maganar ta fito fili , ba aljanu ba a bishiyar kuka nake kwana Kamill ya bata amsa tare da rausayar da kansa gefe kamar mace , lunshe ido Diyana tayi ta juya zuwa ɗakinta , tana shiga taci gaba da kukanta tunaninta shine shin mutane basa ganin halin da nake ciki ne ya Allah ka kawomin ɗauki , ɗaga kanta tayi cikin mamaki ta kalli agogon dake manne a jikin bango tace " har biyar tayi ko sallah banyi ba ? miƙewa tayi ta shiga toilet ta watso ruwa tare da ɗauro alwalah ta

shimfiɗa darduma ta tada sallah , tana idarwa taji yunwa tayi mata sallama , kasancewar tanada ruwan zafi da kayan shayi yasata ɗauko cup ta tsiyayi ruwan zafin ta haɗa tea mai kauri ta janyo kwanon cake ɗinta tafara aikawa cikinta , sai da taji tayi nak sanan ta ajiye cup ɗin ta janyo wayarta , number sister Afreeda ta dannawa kira cikin sa'a tana ring sau ɗaya Afreeda ta ɗauka tare da cewa " oyoyo my sis kwana biyu ? turo baki Diyana tayi tace " bawani ko nemana bakuyi kun mance dani kwata kwata , dan Allah kiyi haƙuri da yau zamuzo da Hajiya sai dady ya tsayar damu wai mubari sai end of this month , zaro ido Diyana tayi tace " to ai yanzu saura kwana goma wata ya ƙare har sai lokacin zakuzo taɓɓ , kiyi haƙuri barin kaiwa momy wayar ku gaisa , no zan kirata barshi kawai, ko sallama Diyana bata yiwa Afreeda ba ta katse wayar , momy ta kira suka gaisa take tambayarta yaushe zata zo , dariya momy tasa tce " banda abinki daughter waya bani zuwa gidanki yanzu ? kidai ƙara haƙuri zanzo amma ba yanzu ba kici gaba da yiwa mijinki biyayya pls dan Allah ki kula da tsaftar jikinki da gidanki , to momy Diyana ta faɗa tanajin kamar tayi tsuntsuwa ta ganta a jikin momynta amma babu hali , zan aiko driver ya kawo miki saƙo kinji ? tom Diyana tace " tare da cewa ki gaida dady nakira wayarsa akashe , daganan sukayi sallama .
Yau kwanan diyana goma sha ɗaya tunda tazo bata taɓa leƙa wjen gidan ba , sanya hijab har ƙasa tayi ta fito tana zagayawa ashe gidan yanada ɗan girma babu laifi , ga swimming pool gwanin sha'awa jitayi tana sha'awar sanya ƙafafunta a ciki , zama tayi a kujerar dake maƙale a gefen gurin ta zura ƙafafunta tana tuno rayuwa idanunta a lumshe kamar mai bacci , tuno zamanta na ƙauye tayi abin sai ya fara bata dariya idanunta a rufe amma sai ƙyal ƙyala dariya takeyi kamar tana magana da wasu.
[27/06, 3:48 pm] Mom Islam Ce: 31 & 32

Jitayi ance waye ya baki izinin fitowa waje ? sanin mai muryar ya sata juyo da kanta gareshi tace " waye mai bani izini ? zaki tashi ki wuce kokuma kinaso ranki ya ɓaci ? tuno nasihar momy ya sata miƙewa ta nufi ciki ranta a ɓace kamar zatayi kuka , bata tsaya a palo ba ta wuce bedroom ɗinta tana mita tare da sawa ƙofar key.
Shirin fita yayi batare da ya waiwayi Diyana ba , motar da ya dawo da ita ya shiga tare da ficewa da gudu yahau titi , direct gidan abokinsa ya nufa da rabonsu da haɗuwa tun bikinsa sai dai suna haɗuwa a waya , yayi tafiya mai nisa ya iso anguwar mai suna gadon ƙaya , wani ƙerarren gida naga ya nufa tare da yin horn , cikin sa'a driver ya buɗe get ɗin tare da ɗagawa Kamill hannu yana cewa " barka da zuwa Alhaji , cikin isa Kamill ke amsa gaisuwar tare da ƙarasawa ciki yana parkin abokin nasa ya fito mai suna Abubakar oyoyo my ango na amarya suka kwashe da dariya , riƙe masa hanunsa Abubakar yayi suka nufi cikin gidan , wani rantsatsen palo naga sun shiga bazan ce yafi na Kamill haɗuwa ba amma shima wanan ƙarshe ne gurin kyau , kujera Abubakar ya nuna wa Kamill tare da cewa " barin kirawo amarya ku gaisa , mirmishi Kamill yayi tare da maida hankalinsa kan waya , ɗago kan da zaiyi yaga Abubakar tare da amaryarsa Safeena tana ɗauke da ciki , hakan ba ƙaramin birgeshi sukayi ba sai yaji inama ace Diyana ce da cikinnan da yafi kowa jin daɗi , kawar da kansa yayi ba tare da ya bari sun gano komai ba ,Kamill ga amarya fa , dariya Kamill yasa kana yace " amarya munkusa zuwa shan suna Allah ya ƙara lafiya , kan Safeena a sunkuye ta gaida Kamill ta tambayi matarsa cikin sakin fuska yace " lafiyanta lau tace " a gaisheki , ina amsawa Safeena tace " tare da miƙewa ta janyo table tafara jerawa Kamill kayan motsa baki , taje fridge ɗauko drinks har kala hudu Abubakar ya miƙe da gudu ya rungumota tare da raɗa mata a kunne karfa ki wahalar min da baby dan zanyi miki hukunci my honey kashe masa ido tayi ta raɗa masa a hankali abokinka na kalonka ko bakajin kunyarsa ?" juyawa Abubakar yayi bayan ya karɓi kayan hanun Safeena ya isa gurin Kamill da duk abinda sukeyi yana kan idon sa , ango ayi mana haƙuri fa , dariya Kamill yakuma sawa kana yace" kuyi dai ku gama baby na kallonku , suka tuntsure da dariya , komawa ɗaki Safeena tayi ta bar musu gurin sbda tsaro , abokina naji daɗin ganin zamanku cikin kwanciyar hankali , Kamill ya faɗa tare da dafa Abubakar , kana yakuma yi shiru .

Kallonsa Abubakar yayi cikin fahimta da karantar yanda walwalar fuskarsa ta sauya lokaci guda , matsowa Abubakar yayi kana yace "karka ɓoye min komai game da zamanku da matarka dan yanayin ka ya nuna baka cikin farinciki , gashi maimakon da kayi aure kayi ƙiba kayi kyau kawai sai naga akasin hakan ko lafiya ? Abubakar ya tambayi Kamil ,hmm Kamill yace " wato Abbak sunan da Kamill ke kiransa kenan tun suna yara kasancewar iyayensu ƙawaye ne haka iyayensu maza ma abokai ne , Kamill yace " tunda muke da Diyana ban taɓa sanin daɗin aure ba , haka bama zaman lafiya ko kaɗan bugu da ƙari banama kulata , buɗe baki Abubakar yayi cikin mamaki yace " yau watanku ɗaya da kwana biyu amma haka kuke zaman doya da manja ? dana sani da haka bata faru ba tun farko gaskiya dan lefin yana gurinka inda ka tafi da ita haka zaku zauna so inason kasan a rayuwa babu abinda yafi aure daɗi da sanya kwanciyar hankali , ba auran soyayya kukayi ba ? Abubakar ya tambayi Kamill . cewa" Kamill yayi gaskiya ba auran soyayya mukayi ba sbda wani lefi da tayimin shi ya sanya na aureta dan na rama ta gane kurenta , amma badan haka ba ni banida larabar yin aure yanzu , innalilahi Abubakar yace " tare da tafa hannu yanzu abokina har kayi hankalin da zaka wulaƙanta mace gaskiya da sake , inhar kanaso kaji daɗin aure dole ka koya mata soyayya zallah ,kwashe labarin gurin bikin da suka haɗu da Diyana yayi ya gayawa Abubakar tare da cewa nifa banison raini wlh badan bazan iya riƙe mata biyu ba da aure zanyi ni bazan iya ɗaukar raini ba kamata ace ina bin mace taɓɓ , murmishi Abubakar yayi kana yace " ai dole mubi mata tunda sune iyayenmu kuma abin jan raini da kake faɗa yanzu ai zamanku ma zai sa ta koyi rashin kunya sosai ma , tunda baka jata a jikinka ba dole sai ka sauke girman kannan inhar kanason farinciki , kuma maganar fansa ka ajiyeta a gefe ka rungumi matarka kuyi zaman lafiya Kamill.
Jinjina kai Kamill yayi yanajin abin kamar tatsuniya Abubakar ya fahimci duk mganar dayayi batayi tasiri a kansa ba dan haka yace " kadai bi a hankali wlh kar daga baya kazo kana dana sani , babu wani dana sani da zanyi abokina kadai tayani da adu'a Allah ya saka min auran mata biyu wanan ba ajina bace ksancewar babanta ma talaka ne , zaro ido Abubakar yayi yana mamakin raina talaka da sukeyi amma ba abin mamaki bane dan Kamill baisan menene talauci ba tun tashinsa bare yanzu da inyaga dama yakan leƙa ofisoshin mahaifinsa amma baya aikin komai iyakaci yadinga jin alart ta waya koda wane lokaci , Kamill har yanzu baka ma fahimci me nake cewa " ba shi so kokuma zaman soyayya anayi da almajira ma sai tafi wata yar mai kuɗin iya kula da miji bare matarka mahaifinta nada arziki dai dai gwargwado , dariya Kamill yasa kana yace " to ni mema zance menene soyayyar caɓ akwai aiki gaskiya.
Babu wani aiki sai dai inhar kai ka maida abin aiki amma inkabi shawara ta to zaka zauna lafiya kuma zaka gode min , shafa sajensa Kamill yayi tare da cewa " zan gwada barin wuce kasa amarya ta gudu ɗaki , dariya Abubakar yayi kana yace " ok muje in rakaka mota suka fice sunata hirar maganar gidan Kamill .
Kamill na shiga mota Abubakar ya koma gida shikuma aka buɗe masa get ya fita , gidansu ya zarce sbda ya kira mahaifinsa yana nan , da shigarsa ya samu anata rabon abinci kasancewar al'adar gidan ne hakan in wata yayi nisa , kowa sai gaisuwa yake miƙo masa daya gaji da amsawa ya ƙyalesu a gurin , palon mahaifin nasa ya ƙule inda ya samesa kishingiɗe a kan gado da jarida a hanunsa, da sallama ya shiga ya nemi kujera mai zaman mutum ɗaya ya zauna tare da ɗan rusunawa yace " barka da yamma Abba ya jama'a , lafiya lau Abban yace " tare da kai dubansa ga fuskar Kamill my son , Abba yace " har yanzu bai dena kallonsa ba . na'am Abba , yanaga kabi ka rame menene matsalar dafatan dai gidanka babu damuwa dan na tabbatar da yarinyar tanada hankali dakuma tarbiya , babu komai Abba Kamill ya faɗa tare da ƙaƙalo fara'a a fuskarsa , to amma wane tunani kakeyi da ya sanyaka rama ? wlh Abba ba komai badan Abban ya yarda ba ya ƙyakeshi , kaje ka gaida mamanka kuwa , haɗe fuska yayi kana yace " tana ciki ne ? eh Abban yace " ka gaisheta kazo ina son ganinka jiya dana dawo na taho muku da tsaraba kai da matarka , tom Abba Kamill yace " ya nufi cikin gidan , samunta yayi a babban palo tana riƙe da remote a

hanunta gefe kuma Apple ne take ci kamar mara lafiya a yanayin taunar da take yimasa , sallama yayi kana ya nemi kujera ya zauna bai jira amsawarta ba yace " barka da yamma ya jama'a lafiya Ameena tace " tare da yanƙare baki gefe , miƙewa Kamill.
[28/06, 3:39 pm] Mom Islam Ce: 33 & 34

Miƙewa yayi tare da barin gurin ya koma palon Abba inda sabo ya saba hakan sam baya damunsa tunda haka ya taso tun yana ƙarami Abbansa kawai ya sani mai yi masa gata gashi ya taso cikin nera amma babu wulaƙancin da bai sha a gurin Ameena ba , hasali ma yana zarginta da kisan mahaifiyarsa , dare ɗaya ta kwanta ciwo a ranar kafin hakan bazai taɓa mantawa ba dan duk da yana yaro bai hanashi mugun wayo ba wata kalma da ta tsaya masa a rai itace " lokacin yana ƙarami yazo wucewa ta saitin ƙofar Ameena zashi ɗakin mahaifiyarsa yaji suna hira ita da ƙawayenta suna cewa ki sanya mata abinda boka ya baki man , mamansa na mutuwa ya laƙawa Ameena amma har yau bai bari kowa yaji ba , tayu ƙoƙari rabashi da ubansa Allah baiyi ba haka ta haƙura da cutar baƙin cikinta , koda Kamill ya koma ɗakin Abbansa kaya ya gani zube a kan gado ƙarasowa yayi kana yace " Abba wanan kayan fa ? nakune yaron kirki kai da matarka , indian fation ne masu kyau dakuma parkistan riga da wando harya hango irin kyan da Diyana zatayi a cikin wanan kayan , ya kayi shiru my son ? Abba ya jefo masa tambayar kunya ce ta kamasa dan kayan Diyana ne a hanunsa yanata jujuyawa , mungode Abba Allah ya ƙara lafiya da nisan kwana , zan koma Abba , murmishin su na manya Abba yayi tare da cewa to a gaida ƴar tawa insha Allah Abba Kamill yace " kana ya fice ya nufi motarsa kasancewar kwana biyunnan kan yayi zafi ba'a batun dreba ma .

Bashi ya isa gida ba sai da ya tsaya a masallaci yayi sallahar isha'i kana ya wuce gida yana parkin ya shige babu kowa a palo sai tashin ƙamshi yakeyi , kai tsaye ɗakinta ya nufa tana zaune a bakin gado da waya a hanunta tayi wanka ta haɗe cikin shadda blue taji ɗinki mai kyau ga wata sarƙa mai walwali da ta sanya a wuyanta , aslamu alaikum , yi tayi kamar bazata amsa ba sanin darajar amsa sallama ya sata amsawa ko kallon inda yake batayi ba , bare yasa ran zatayi masa magana , sannu da hutaww Kamill yace " da sa, sanyar muryarsa yawwa sannu , daga haka ta miƙe tabi lafiyar gado , wata zuciyar ce tace " ka bita kawai gashi ta nuna maka abinda take so , wata zuciyar kuma tace " karfa ka jawa kanka raini dan inbaka man taba ƴan mata nawa ne a waje suke sonka ƴaƴan manya baka sauraresu ba , tuno nasihar Abubakar yayi da yace " dole ka bita ahankali dakuma nuna soyayya , toshi kam yarasa ma menene soyayyar kasancewar shi ba ma'abocin shirme bane dan ya ɗauki soyayya ahirme shikam amma wai gashi yau shine yake yiwa mace magana take ƙin kulasa taɓɓ akwa aiki , ɗaga waya yayi ya kira mai gadi tare da cewa ya buɗe bayan motarsa ya ɗibo masa kaya angama mai gadi yace " ya ruga da gudu zuwa inda aka aikeshi shikuma ya kashe wayar , bubuga ƙofar da yaji ne ya sashi miƙewa ya karɓo kayan ya dawo ya zauna yana cigaba da kallon Diyana da tayi kamar mai jin bacci , yakai waje 30 mins a haka ganin babu sarki sai Allah ya sashi barin ledar a gurin ya fice daga ɗakin ya nufi nasa , kwanciya yayi a kan bed yana mamakin kansa wai shine yabi mace , tab gaskiya Abbak yana neman badasa a gurin wanan yarinyar wai kuma a cewarsa ta haka ne bazata rainasa ba , to gashi tun yau an fara shikam yanajin bazai iya cigaba da binta ba gaskiya , gara ko ciwon mararshi ce ta motsa yasha magani uban me ma zai samu a gunta banda yarinta lol sai surutansa yake kamar zautacce , bayan ya gama ya cire kayan jikinsa ya shige toilet ya watsa ruwa , yana shirin kwanciya yaji yunwa ta taso masa babu shiri ya miƙe ya nufi palonsa ya buɗe fridge ya ɗauki malte yasha kana ya dawo bedroom ya kwanta da tunani iri iri bacci ya kwashesa .
Itama Diyana wanan kwanciyar da tayi batasan lokacin da bacci yayi gaba da ita ba sai farkawa tayi taga agogo ƙarfe huɗu , miƙewa tayi tare da ɗauro alwalah ta tada sallah , nafiloli tayi tana cikin yi taji ankira asbha bayan ta idar ta tada sallahar farilla

tana idarwa tabi gado ta kwanta tanajin kewar momynta , wani lokacin d share hawaye gashi Kamill yaƙi kaita gidan batasan da wace irin murya zata yi masa magana ya amsa mata ba.
Washe gari da safe misalin 7:am ya shirya cikin pink ɗin yadi mai laushi kana mai tsadar gaske bayan ya gama shafa mayukansa masu ƙamshi ya sanya hula a kansa ya feshe jikinsa da turaruka masu ƙamshi ya kwashi wayoyinsa da keys ya fito , kai tsaye bedroom ɗin Diyana ya nufa yana shirin buɗe door yaji wayarsa na ring dawowa yayi da baya ya amsa wayar , jinayi yace " Abbak ya gida ya kuma mom twins ?lapiya naji Abubakar yace " can kuma ya jefowa Kamill tambaya , an dace kuwa ? ko ɗaya Kamill yace " nifa nakasa shawo kanta pls i need your help , ka temaka yanzu dai abinda nakeso da kai shine karka gajiya dan dole zakasha wuya kafin aci nasara abokina , sallama sukayi Kamill ya shige bedroom ɗin , samunta yayi da cup a hannu tanata juya cokali da ruwan shayi a ciki ko madara babu gashi fuskarta ta jiƙe da hawaye , innalilahi Kamill yace " a fili tare da ƙarasawa gurin da take zaune dama inhar tana bedroom gurin zamanta baya wuce bakin bed , zama yayi kusa da ita kana ya rungumota yafara shafa kanta a hankali alamar rarrashi , am sorry my baby insha Allah wani abu bazai ƙara faruwa ba a tsakaninmu dan Allah ki tausaya min yanayi yana shafa gashin kanta da yayi luf ya kusan rufe mata fuska , batayi ƙoƙarin hanashi ba sai ma wani marayan kuka da ta saki sbda tuno kwanaki da zaiyi baƙi yayi mata wayo dan karsu gano meke faruwa tsakaninsu, ya salam Kamil yace " lokacin daya ɗauketa cak ya ɗora kan jinyarsa , baki haƙura ba kenan? wlh kinji na rantse bazan ƙara wulaƙantaki ba na gano kuskurena mu gyara zaman auranmu pls my Diya , lumshe ido Diyana tayi, kana tace " ka daɗe kana wanan kalamin halan yau ma baƙi za'ayi shine ake lallami na , murmishin yaƙe Kamil yayi kana yace " yau babu wanda zai zo kawai inason gina farinciki ne a jikin gidana , rungumeshi tayi tana kuka mai ban tausayi shima ƙara matseta yayi a jikinsa yana jin sonta tana bin kowacce gaɓa ta jikinsa , gyara mata zama yayi tare da kashe mata ido yace " my Diya me zaki samomin insa a cikina dan yau da wuri nakejin yunwa , lumshe ido tayi kamar mai jin bacci tace " mai kake so muje mu dafa dan yau dole ka shiga kitchen , kamo hanunta yayi suka fito zuwa kitchen fuskokinsu cike da farinciki, doya ta ɗauko ta miƙa masa da wuƙa tace " ga naka aikin babu musu ya karɓa suka fara aikace ai kace , yam balls sukayi dakuma wainar kwai tare da yin zobo wanda yaji cocumber da flevor da abarba , kichen ɗin sai ƙamshi yake zubawa , suna gamawa Diyana tayi wanke wanke shikuma Kamill ya goge gurin , ɗaukar abincin sukayi tare da nufar dining Kamill da jug a hanunsa ita kuma Diyana hanunta ɗauke da foodflaks suna shirin kaiwa dining sukaji sallama , da ganin mai sallamar Kamill ya ɗauke kai , Diyana batasan ko waye ba hakan yasa ta amsa sallamar tare da yimata umarni da nuna gurin zama.
[29/06, 4:45 pm] Mom Islam Ce: 35 & 36

Yatsina fuska tayi ta zauna tare da ɗora ƙafa ɗaya kan ɗaya shidai Kamill bai kalli inda take ba sai ma kawar da kai dayayi yace " ina yini , Hajiya Ameena na karkaɗa ƙafa tace " lafiya amma kaji kunya haka ka koma ?ina isar taka da rashin kunya yanzu mace ce mai juyaka koda yake babu mamaki haka uwarka tayiwa mahaifinka , yanzu Diyana tafara gano ko wacece Hajiya Ameena , cikin zafin nama ya isa gabanta da shirin wanketa da mari Diyana ta riƙe masa hannu tare da durƙusawa tana hawaye tace " inba ban faɗa dai dai ba wanan ɗin uwa ce a gurinka kome zatace karka fara yimata rashin biyayya , zuciyar Kamill tafasa take dan wanan matar ta kaishi maƙura tabbas wataran zai illata ta tunda ta tako har gidansa take zagin mahaifiyarsa da take kwnce a kabari , barshi ya mareni indai rashin tarbiya ne ai ya saba wlh kinyi kuskure da kika auri ɗan wahala , mai maitawa Diyana tayi cikin zuciyarta ɗan wahala kuma ? wucewa ɗaki tayi da gudu dan kuka yaci ƙarfinta , tana zuwa ta faɗa gado tare da sakin sabon kuka shin wanan matar tazo tarwatsa mata aure ne kokuma so takeyi ta kaita ta baro inko haka ne kota ƙara zuwa bazataje gaisheta ba , hankalin Kamill a tashe ya nuawa Hajiya Ameena ƙofa tare da cewa "

kifita tunda ba gidanki bane , kutumar uba Hajiya ameena tace" tana haki kamar mai shirin dambe , bazan fita ba kasa a fitar dani banza marar tarbiya kawai , ganin batada alamar fita yasa Kamill danna lambar Abba ring ɗaya Abba ya ɗaga amma Kamill bai bari tasan kira yayi ba , cigaba yayi da cewa zansa a fitar dake , kalmar da Abba yaji ne yasashi cewa kai da waye Kamill , Kamill baiyi magana ba maganar da Abba yaji itace " kayi asara da ka ɗauki halin tsiya agun uwarka , idanun Kamill cike da hawaye yace " Abba wanan Ameena ce fa har gidana tazo take zagin mahaifiyata a gaban mata ta , innalilahi Abba yace " ku jirani dukkan ku ganinan zuwa dama jiya mukazo Abuja nida Ameenan yau ta cemin zata gidan ƙawarta ashe nan zatazo , Abba ne yasa drivern sa ya juyo da mota zuwa anguwarsu Kamill , drivern na yin horn aka buɗe get ya shige ajiye motar yayi a parking spice drivern na shirin buɗewa Abba mota cikin azama Abba harya buɗe ya fito , Ameena dake ruwan bala'i tana cewa aure ka keso ka kashemin to wlh ta Allah ba taka ba , karaf a kunnen Abba yace " ai naji komai ya ƙarasa shigowa yana yimata kallon banza, tsabar masifarki kin biyo ɗana har gidan sa kina ci masa mutunci a gaban matarsa to wlh bazai yuwu ba kuma bazan lamunta ba naji duk wani abu da kike faɗi Kamill , Abba ya kira sunansa , kiramin matarka da sauri Kamill ya nufi bedroom ɗinta yana tura ƙofa ya sameta zaune kan stool ta kifa kai da guwaiwa tana gursheƙen kuka , rungumota Kamill yayi tare da share mata hawayen yace " taso muje Abba ya zo yanzu kuma yana son ganinki , miƙewa tayi ta zura hijab har ƙasa tabi bayan Kamill daya rigata wucewa , samun Abba tayi zaune kan kujera samun guri tayi a ƙasa kan kafet ta zauna tare da sunkuyar da kai kasa ta gaida Abba , amsawa Abba yayi da fara'a ɗauke kan fuskarsa yace " Allah yayi muku albarka insha Allah auranku har mutuwa alfarmar shugaban Halitta , Ameena dake gefe tana zaro ido dan yanzu gani take tata ta ƙare Abba ne yace " ki wuce mota kafin inzo babu musu ta fice cikin sauri ta zauna gidan gaba dan yau bazata zauna gata gashi ba tasan bata kyauta ba amma inta tuno burin zuciyarta na saita raba Kamill da farinciki shike ƙara mata ƙaimi gurin aikata tsiyarta san ranta, zufa babu inda baya keto mata dan tsa tsauran ra'ayin Abba tasan zuwan da dawowar.
Abba ne yaci gaba da cewa insha Allah wata mai kamawa zaku ziyarci ƙasa mai tarki Diyana batasan lokacin da murmishi ya kufce mata ba Kamill godiya yayi itama haka , ya kamata ka siya mata mota son inma driver ne sai a samo , to Abba Kamill yace " cikin fara'a , ajiye diyana bandir ɗin yan dubu dubu yayi a gefenta cikin jin kunya Diyana tace "Abba mun gode Allah ya ƙara lafiya , daga haka Abba ya miƙe tare da gyara malun malun ɗinsa yayi musu sallama , yana ficewa ya nufi mota back side ya shige batare da ya kalli Ameena ba driver yaja suka wuce masaukinsu.
koda suka isa kowa gurin kwanciya ya nema Amena bata bi takan Abba ba kasancewarsa mai sauƙin kai dakuma bijirewa , washe gari Diyana tana ta haɗa Kamill da Allah akan yakaita gidan su , da zarar tayi magana sai yace " yafison tace " da ciki suganta tayi nauyi , cuno baki tayi tare da kai masa dukan wasa , suyita zagaye palo suna guje guje , da yamma Kamill na zaune yana kallo Diyana na kitchen taje duba girki , wani uban ihu yaji da ya sashi tashi da gudu ya haura sama yana kiran sunanta , wayo my blood na ƙone da mai wayo Allah na , jiyayi kamar zafin ya koma jikinsa abinka da masoya ƙunar ma ba wata mai yawa bace amma duk sunbi sun ruɗe , komawa gefe tayi ya ƙarasa aikin tana gaya masa abinda zaiyi, suna gamawa aka nufi dining aka jere komai , Kamill yace " yazu saura wanka ya rage mana , rufe ido Diyana tayi dan kunyarsa takeji sosai , kamo hanunta yayi suka haura zuwa ɗakinsa ya cire mata kaya shima ya cire nasa , idanuta arufe gam haka suka shige toilet shiko ogan hankalinshi ya tashi da ganin kyan diri irinna Diyana , tabbas yayi sa'ar mata daya bari dayaga samu yaga rashi , a gurin wanka ma sai da akayi drama duk da idonta a rufe yake taƙi yarda ya taɓata rabi wanka rabi tsokana duk inda ya taɓa sai ta zille tana dariya , naɗota yai a towl ya shimfiɗeta a kan bed , rufa mata baya yai tare da ja musu blanket , tunda Diyana taga haka tasan daƙyar yau idan mai afkuwa bata afku ba ga shegen tsoro , ganin Kamill yayi kamar mai bacci yasata miƙewa a hankali , batagai ga sauka daga kan gadon ba taji ya cafko mata

hannu tare da matseta a jikinsa , tsam ta matse jikinta dan yau jikinma rawa yakeyi to meye dalili ? batada mai bata amsa yasa tabar abin a cikin zuciyarta ,jin salon komai ya sauya yasa Diyana runtse ido tare da adu'ar Allah ya bata ikon farantawa mijinta Allah kar ya bata ikon wulaƙantashi ko nuna gajiyawa , babu ta inda baya aika mata da message na jikinta cikin sa'a ko ina na amsar saƙon , ada yana taraiyya yana ywan harka da mata amma duk abinda ya keyi bai taɓa sanin kowacce macce ba gashi ma tunda yai aure komai ya lafa , dama ance aure ni'ima ne tabbas kuma ya yarda , jin ya cire towel ɗin da ya naɗeta yayi mata rumfa da ƙirjinsa ya sata runtse ido tana ambato sunayen Allah adu'ar saduwa da iyali yayi sabda gudun sheɗan kana yafara neman hanya , cikin salo daƙwarewa yake aikinsa yayin da yake adu'oi kala kala a cikin zuciyarsa, tun Diyana na daurewa har ta kai ga haɗashi da Allah da ya barta amma ina Kamil yayi nisa , bashi ya sarara mata ba sai da ya tabbatar da ya mai data cikakkiyar mace sannan ya mirgina gefe yana mai da nunfashi , kana daga palo kana jin surutunsa yana cewa " Allah yayi miki albarka my Diya haƙiƙa nayi sa'ar mata mai tarbiya ilimi dakuma hankali kin biyani my Diyana ya rungumeta tsam a jikinsa yana shin shinar gashin kanta tare da raɗa mata i love you cikin sa ssanyar muryasa mai ratsa jijiya , idanunta a lumshe ga hawaye dake zarya tausayi ta basa amma da yake shiɗin shine , yace" tunda baza kiyi shiru ba bari in samo mana baby ai ɗazu inata hangosu sunata cewa " dady ina momy dariya Diyana tasa tare da rufe ido cikin jin kunya.
[29/06, 8:27 pm] Mom Islam Ce□: 37 & 38

Ƙara langwaɓewa tayi a jikinsa tana yi masa kukan shagwaɓa , shiko sai ƙara lallaɓata yake kamar ƙwai , tashi muje muyi wanka , uhm ni bazani ba kace kai ƙadai pls , Diyana ta faɗa cike da shagwaɓa , Kamill dake dariya yace " nikuma dole sai da ke kitashi kawai kokuma in tasheki , maƙe kafaɗa tayi tana shirin sanya masa kuka , to barin ƙara Kamill ya faɗa tare da haɗe rai , babu shiri ta miƙe ta yayibo towel ɗin zata ɗaura ya ƙwace tare da ciciɓarta zuwa toilet , yana direta taji wani azababben zafi na shigarta wayo momy ta fara kira tana tsale ga sabon hawaye yana yimata sintiri a fuska , sorry my Diya Kamill ya faɗa fuskarsa da alamun damuwa , tara mata ruwan zafi yayi a bahon wanka kana ya ɗiga detol ya ɗago ta ya sanya ciki , ihu tasa tare da riƙeshi gam tana cewa wlh da zafi ruwan ka cireni dan Allah , bai kulata ba sai ma ƙare ma halittarta kalo da ya keyi ita kam tsabar wuya tama mance tsirara take , jin tayi shuru tayi luf yasa Kamill tabbatar da ruwan ya ratsa ta , buɗe gurin tafiyar ruwan yayi wanan ya tafi yakuma tara mata wani , sai da yayi hakan har sau uku kana ya temaka mata tayi wanka shima yayi idonta a rufe dan muraran kunyar ganin halittarsa takeyi bare shi kansa , a haka suka gama ya naɗeta kamar jaririya shikuma ya ɗaure ƙugunsa da wani ƙaramin towel a hanunsa ya ɗaurawa Diyana a kanta suka fice , kayana na ɗaki na fa zani in ɗauko , no bazakije ba yau sabuwa kike dole sai sabon kaya , shagwaɓe fuska tayi tana turo baki , dariya Kamill yasa yana ƙare mata kallo kamar yau ya taɓa ganinta , my Diya .
Kamill ya kira sunata cikin sanyin murya , na 'am tace " tare da mai da hankalinta gareshi , kina sona ? zaro ido tayi dan bata taɓa tunanin zata tsinkayo irin maganar nan a gurinsa ba anya shine kuwa ? katse mata tunani tayi dan duk maganar da takeyi a cikin zuciyarta take " My Diya kina sona , Kamill ya faɗa a karo na biyu , kallon ƙwayar idonsa tayi sai kuma ta sunkuyar ƙasa tana wasa da zoben hanunta , miƙewa yayi tare da nufar gaban mirror ya nemi stool ya zauna yana ƙarewa kansa kallo , tabbas ba yabon kai ba ni kyakyawa ne nasani to meye yasa Diyana bazata bani amsar tambayata ba ? kodai dagaske bata fara sona ba ? duk kansa yake yiwa wanan tambayar , kawar da tunanin yayi ya ɗauki lotion ɗinsa mai ƙamshi ya shafa tare da turaruka masu sanyi ya yiwa kansa gyara tare da shafa mayukan daya saba ya miƙe zuwa drower , kayansa ya ciro sabbi wanda bai taɓa sawa ba kasancewar yakanyi ɗinki duk ƙarshen wata yakanyi kusan kala goma banda ƙana nan kaya da yake siya , shadda ce gezna brown tasha aiki ba ƙarya , hula ya ciro kakar shaddar sai agogo daya ɗauka a glass ɗin da suke a jere kamar shago kana ya ɗauki

takalminsa ya juyo ko kallon inda Diyana take baiyi ba ya fice palo ,jin ana kiran sallahar magrib yasa shi miƙewa ya nufi masallacin dake gidan yai sallah , yana idarwa ya dawo gida ya nufi dining bai sauka ba sai da ya tabbatar da ya cika cikinsa tab sanan ya dawo kan doguwar kujera 3siter ya kwanta tare da zubawa kwaliyar sama ido , tunani iri iri gashi ya fara ɗawainiyar son Diyana gashi kuma tana nema taƙi karɓar soyayyarsa.
Gajiya da zama Diyana tayi cikin lokaci ƙalilan zazzaɓi mai zafi ya rufeta wanda ko buɗe ido bata iya yi ga azabar ciwon kai , daƙyar ta samu ta janyo pilo ta kwanta ga wani sanyi dake addabarta , bata lura da blanket a kusa da ita ba hakan yasa kana nesa kana jin ƙarar kaɗawar haƙoranta, kamar an tsikare shi ya miƙe ya nufi ɗakinsa , yaje da niyar ko kulata bazai yi ba yaci karo da ita tana ta rawar sanyi , da sauri ya ƙarasa tare da cewa " ya illahi my Diya maiya sameki kodai nine in ni na ɓata miki rai pls kiyi haƙuri bada son raina bane am srry mgna yake kamar wani zautacce amma Diyana ta kasa koda ɗaga yatsanta banda hawaye babu abinda ke fita daga fuskarta , matsowa yayi ya rungumeta yana jin ɗumin jikinta sosai ,jin ana kiran sallahar isha'i yasa shi shimfiɗa darduma ya tada sallah yana idarwa ya nufi inda Diyana take shafa fuskarta yayi idanunsa cike da hawaye ya fice ya nufi bedroom ɗinta , hankalinshi a tashe ledar kayan da Abba ya basa jiya ya dubo mata doguwar riga baƙa mai adon golden stone dakuma ɗankwalinta , ya buɗe drower ya ciro mata pant da under ya fito , yana shiga ya samu ta ɗan miƙe tana cewa " zan sha ruwa cikin azama ya nufi fridge ya ɗauko swan water marar sanyi ya buɗe ya bata tasha , babu batun shafa mai ya sanya mata kayan ya fito da ita palo ya kwantar , ɗauko keys ɗin ƙofar palon yayi kana ya goyata a baya ya fito ya kulle ƙofar ya nufi mota , drivers abin ya basu mamaki ganin Kamill zai yi driving da kansa , ganin abinda ya goyo yasa kowannen su tashin hankali masu kula da shi duk babu wanda yayi gigin zuwa tambayarsa , kasancewar sun sani inhar yana cikin ɓacin rai basa tunkarar shi , kai tsaye ana buɗe masa get ya fice da uban gudu ya ɗauki hanya Rahama hospital ya kaita asibitin kuɗi , kasancewar shine mafi kusa dasu , suna isa ma'aikatan hospital ɗin suka fito domin taryar su Kamill , zasu ɗauki Diyana ya dakar dasu da kansa ya ɗauketa ya shiga da ita , suna shiga aka fara bata temakon gaggawa hankalin Kamill a matuƙar tashe sai zaga libraryn asibitin yake zama ma ya ga gareshi , kira yaji a wayarsa hakan yasa shi saurin ɗagawa kasancewar yaba wa doctors number sa , kazo ina office abinda yaji ance kenan aka katse wayar , da sauri ya nufi office ɗin babban likitan , samunsa yayi zauns a kujera da farin glass manne a fuskarsa yana yɔn rubuce rubuce , kaine mijin mara lafiyar da aka kawo ɗazu ? eh eh Kamill yace " dan burinshi yaji meke damun Diya ɗinsa , akwai abinda yai matuƙar tsorata ta har yake barazana da zuciyarta so a kula kar adinga tursasa ta abinda bataso kuma tana buƙatar bacci sosai sai zuwa gobe zamu sallameku , ajiyar zuciya Kamil yayi kana yace " babu damuwa nagode , ya tashi zai fita ya dawo am zan iya ganinta ? eh doctor yace , ok Kamill ya nufi ɗakin da shigarsa ya sameta kwance iya ciwon rana ɗaya ta rame abinka da marar ƙiba takuma sirancewa sai dogon hanci da dara daran idanuwa , lumshe ido tayi tare da miƙowa Kamill hannu , da sauri ya ƙarasa ya zauna a kujerar dake kusa da gadonta ya haɗe hanunsa cikin nata , sannu my Diya Allah ya baki lafiya , lumshe ido tayi kana tace " my blood naji sauƙi fa karka damu wlh, dole in damu farinciki na babu lafiya daga ke sai Abba kune farinciki na , hawaye yaga na bin kumatunta cikin sauri ya share mata yana cewa " wanan maganar ce ta saki kuka am sorry karki ƙara nima nayi shiru , ina mahaifiyarka .....sauran suka maƙale mata a bakinta , dama yana jiran wanan ranar , danginsu yɔn uwansa babu mai bibiyar gidansu babu mai tambayar mahaifiyarsa sai yau ko Abba ma baya maganar ta iya kaci yaji ance ta mutu tun yana ƙarami anya kuwa mutuwar tayi ? ya fara waswasi a cikin zuciyarsa bai kai ga bata amsa ba takuma jefo masa tambaya , wanan matar itace ta raineka ko ? eh Diya amma mai yasa bakida lafiya zaki tadawa kanki da hankali pls kidena kibari kiji sauƙi zanyi miki bayanin komai.
[30/06, 4:32 pm] Mom Islam Ce: 39 & 40

Uhm Diyana tace " tana shafo sajen fuskarshi dake matuƙar burgeta, tashi ɗaya tunanin mahaifiyarsa ya dawo masa da baya tunanin ta da yanzu kan hankalinsa yayi matuƙar tashi yana son yasan ta mutu ne kokuma akwai wani abun da ake ɓoye masa , juyawa yayi yaga bacci ya ɗauketa , ajiyar zuciya ya sauke tare da duba agogon dake manne a tsintsiyar hanunsa , ƙarfe biyar na yamma , fitowa harabar hospital ɗin yayi yana dube dube wani katafaren shago ya hango da alamu baza'a rasa abin sawa a bakin salati ba , yana zuwa ya karɓi malte da viju milk dakuma donute ya biya kuɗin kana ya nufi hospital ɗin , idon ta a buɗe da yake baccin ba mai nauyi bane , ina kaje ? Diyana ta jefo masa tambaya da sa sanyar muryarta , naje nemo miki abinci ne , uhm bana jin yunwa fa , janyo ledar Kamill yayi ya ɗaauko maltina zai bata ta kawar da kai tare da ce masa babu mai madara ne , dariya taso bashi ya kwai kwayi yanayin maganarta yana dariya , haɗe rai Diyana tayi tace " nafasa sha ma sorry kar kiyi fushi pls my Diya , murmishi tayi masa wanda har dimple ɗinta ya loɓa , a baki ya diga bata viju ɗin har sai da tayi rabi ta kawar da kai , ƙin cin donut ɗin tayi shiko bawa cikinsa yake duk da yana cikin damuwa , my blood ka kira momy ka faɗa mata banida lafiya , cewar Diyana , no baza'a tada musu hankali ba nima ko Abba ban faɗawa ba karki damu insha Allah kinma samu lafiya gobe za'a sallamemu , barin kira securitys ɗina su siyo miki kayan da zaki canxa zuwa anjima , tom Diyana tace " dan batason yi masa musu , fita yayi ya nufi masallaci dan magrib tayi , bashi ya dawo ba har sai da akayi isha'i sanan ya fito ya kira aka siyo mata kaya ya karɓo dan bai bari sun shigo ba kasancewar Allah ya zuba masa kishi sosai , doguwar riga ce dakuma hijab ya shigo room ɗin da aka kwantar da ita , samunta yayi a zaune a kan gadon tana ta rarraba ido da sallama ya shiga ya sami kujera ya zauna , dubanta yai yace " gafa kayan nan , karɓa tayi tare da godiya ta ajiyesu a gefe , ta kallesa tace " zanyi sallah , tana shirin miƙewa doctors suka shigo su biyu mace da namiji ya yanayin jikin ? suka tambayeta tare da tambayar ko akwai abinda yake damunta , babu komai Diyana tace " suka gama abinda zasuyi suka fice. temaka mata yayi tayi alwalah ya fita zuwa mota ya ɗauko sallah yana shigowa ya shimfiɗa mata ta sanya hijab ta tada sallah , neman gurin zama yayi yana ƙare mata kallo , tana idarwa tayi adu'oi ta shafa ta ninke sallayar ta dawo bakin gado ta zauna Alhmdulilh Kamil yace ya sakar mata murmishi , itama maida masa tayi da haka dare yayi sosai , dan a lokacin ƙarfe takwas , gadon kusa da Diyana Kamill ya hau yaja sabon blanket ɗin dake ajiye a ko wane gado , itama kwanciyar tayi , kasancewar zirga zirga da yasha yana kwanciya bacci yayi awon gaba dashi , itama baccin ne ya kwasheta sbda allurori da tasha , washe gari da asbha kowanensu ya tashi bayan sunyi sallah ta shiga toilet ta haɗa ruwan wanka wata likita ce ta shigo da sabon soso da sabulu ta miƙawa Diyana , Kamill ne yace " my Diya ko inzo inyi miki wankan ne ? da sauri ta shige tare da turo ƙofar da ƙarfi tana dariya , tana gama wanka ta leƙo ta huduwar ƙofar tace " my blood miƙomin kayana , yana ji yaƙi kulata , sai da ta sake magana a karo na biyu ya miƙa mata yana mamakin kunya irin ta Diyana kamar ba wayayya ba taɓɓ , tana gama sanya kayan ta fito kasancewar bbu mai wani kallo da Kamill ke binta dashi ne yasa ta hura masa iska a ido tare da cewa " kamar an sauya ni ? murmishi yayi yace " sauyi kuma waye ? kaine kaine ta faɗa tana nunasa , tama bashi dariya sosai sai da ya dara, suna haka aka kawo takardar sallama , tare da cikon kuɗi 40k haka ya biya suka nufi gida.

yau su Abba suka koma Kano har yanzu tsakaninsa da Ameena sai dai haɗuwa ta mota ko kulata beyi itama bata bi ta kansa ba tasan inhar ta matsa sai tayi nadama , suna sauka a mota kowa yai part ɗinsa , waya naga ta ciro ko zama batayi ba tahau kiran wata number da babu suna , ji nayi ance Hajiya barka dai yawwa bos ina maganar matar da kazo ka tafi da ita shekara talatin da suka wuce ? wacce kenan ? bos ɗin ya tambaya , ko ka mance Hajiya ameena ok ok na tuna ,ai a hanyar Lagos na yar da ita kwanaki naga an nunota a tv na tsorata kar asirinmu ya tonu zaro ido Hajiya Ameena tayi tare da cewa " nshiga uku Allah ya auna mana arziƙi taɓ , daga

haka ya katse wayar bai sake bi takan maganar ba , zufa ce ke karyo mata ta ko ina, magana ta fara kamar wata taɓaɓɓiya , nasa boka ya rufe bakin kowa gashi asiri na yana neman tonuwa , inhar hankalin Alhaji dana ɗansa suka dawo to babu makawa nariga na mutu wlh gashi rabona da boka tun lokacin da yaimin aikinnan , jimami da fargaba suka taru a zuciyar Amina , koda wane lokaci gani take za'a iya hasko fuskar mahaifiyar Kamill shiyasa ma kwana biyunnan ta ƙauracewa tv kwata kwata.
Hajiya ce riƙe da hanun Tinene tana yimata mita akan tanaso yau ma sai sun shirya Alhaji yace baza su ba to bazata lamunta ba babu mai zuwa dubota , haka dai ta cika gidan da masifa shigowar Alhaji yaci karo dasu harda Afreeda a jikin mota , ina zuwa kuma Hajiya ? ko kallonsa batayi ba bare yasa ran da zata amsa masa , sadda kai ƙasa yayi tare da cewa "Allah ya baki haƙuri Hajiya , yana tafiya sai da ta tabbatar ya ƙule cikin gidan ta kira driver tace " ya kaisu gidan su zabiya , cikin sauri suka shige driver ya tada mota suka ɗauki hanya , sun ɗanyi tafiya sanan suka iso anguwar , horn drivern yayi mai gadi ya buɗe masa suka shige , yana parking suka fito Afreeda da gudu ta shige ciki ta fara ƙwanƙwasa ƙofa , jitayi Kamill yace " waye zaro ido tayi ta ƙame a gurin dole ta jira Hajiya ta iso , ai basu buɗe bane ? suka barki a tsaye kamar bishiya ? eh Afreeda tace " tana dariya , masifa Hajiya ta fara tana cewa " zaku buɗe ko sai mun rotsa gilahin da taɓarya , jin muryar Hajiya yasa Diyana miƙewa tace " my blood granny ce tazo , cikin fara' a yace " barkansu barin je in sako kaya ya miƙe da sauri ya haura sama, buɗe musu ƙofar tayi tare da rungumo Afreeda suka shigo ciki , halan mu ba mutane bane da zaki ƙyalemu ko ? cewar Hajiya , laa yi haƙuri granny barkanku , taɓe baki Hajiya tayi tahau waige tana cewa " ina shugaban naji maganarsa ina ya ɓuya , ya shiga ciki Diyana tace " tana kallon Afreeda da ta ƙara girma tayi ƙiba , sis bakida lafiya ne ? Afreeda ta tambayeta , eh sis cewar Diyana , Hajiya ce ta kalli Diyana tace " an gamu kenan sai a kiyaye shan magani mai ɗaci ku yaran zamani da sanabe , yanzu gashi ashe rabo ne ke kiranki , sunkuyar da kai Diyana tayi sbda taji takun takalmin Kamill yana tahowa , ga kunya da ta kamata , Hajiya ce tace " to abamu ruwa musha tunda sai mun roƙa , sis pls tashi ki ɗibo ruwa , ajiye mayafinta Afreeda tayi ta nufi fridge ta kwaso su drinks da ruwa ta ka wowa hajiya , tare da neman gurin zama , Hango Kamill Hajiya tayi daga nesa taga kamar balarabe , to shikuma wancan waye ? dan naga ba kalar fatarmu ce da shi ba , dariya ce taso kubcewa Diyana tace " bature ne nima a gidan na gansa.
[30/06, 6:40 pm] Mom Islam Ce: 41 & 42

Kamill dake sauko wa cikin takunsa na ƙasaita ya durƙusa har ƙasa ya gaida Hajiya kana ya dubi Afreeda kallon inda Diyana take yayi sai yaga kamar yan biyu dariya Diyana tasa dan ta lura da kallon da yake yi musu sunkuyar da kai Afreeda tayi tare da cewa " barka da rana ywwa barka yasu momy cewar Kamill , suna lafiya Afreeda tace " komawa ciki Kamill yayi naga ya ciro wayarsa ya danna lambar Diyana , bata ɗaga ba dan tasan mai kiran yasa ta miƙewa tayi bedroom ɗinta dan taga kamar nan ya shiga , oh ni ya su yaran zamani babu kunya ta tafi ta shanyamu yayi har ana hanani zuwa ina masifa , tana shiga Kamill ya rufo ƙofa tare da rungumota yace " my Diya kin yi baƙi kin mance dani ko ? to ya jikin naki ? da sauƙi tace " tare da lumshe ido , ciro kuɗi yayi zasukai 20k ya bata yace " tabawa su Hajiya shi zai je Abuja yau ɗinnan amma bazai dawo yau ba , rau rau tayi da ido kamar mai shirin kuka tace " to muje tare man nikam bazan iya zama ni kaɗai ba , kiyi haƙuri zamuje amma ba yau ba jirgi zan hau kinga yanzu ƙarfe biyu , da ƙyar ya rarrashe ta ta amince zasuje sati na gaba , Allah ya tsare tayi masa ta ɗauki kuɗin ta dawo palo , wani mugun kallo Hajiya ta wurga mata tare da cewa dusa kika shuka ke daɗi miji ko kin tafi kin barmu ko wai waya babu , Diyana dai batayi magana ba ta dire wa Hajiya kuɗi a jikinta , zaro ido hajiya tayi zatayi magana Diyana tace " kiyi masa godiya , Kamill da ya fito hanunsa riƙe da wayoyi hajiya tace " to mai gida an gode fa , babu komai Kamill yace " a gaida momy ya fice , Diyana sai kallonsa take fuskarta da alamun damuwa ta dawo kujera ta zauna , to duk Allah ya tsaren da kikayi masa beyi ba sai kin ɓata ranki a banza to wlh ki kula , ko bi ta kanta Diyana batayi ba tace " sis zomu shiga

kitchen , miƙewa Afreeda tayi suna shirin tafiya Hajiya tace " Tinene rakasu tunda sun wareki Diyana bataso ba amma Afreeda tace " tazo suje , da shigarsu aka fara tunanin abinda za'a girka muyi faten doya mai kifi pls sis cewar Afreeda ok bakida matsala , sis ɗauko mu fere no cewar Diyana miƙawa wanan yarinyar ta fere ɗauko kaza a fridge a soya , haka suka dinga aiki baji ba gani ga faten doya ga soyayyar kaza ga lemon abarba da yaji kayan ƙamshi suna gamawa aka fara jerawa a dining Hajiya na zaune hankalinta ya tafi gurin kallo, gyara kitchen ɗin sukayi kana suka dawo palo aka zubawa kowa a plet ƙa'idar Hajiya ita da jikarta basa zama a kan kujera hakan yasa aka zuba musu a faranti babba aka zubo kazar a plet shikuma juice ɗin a jug hira sukeyi tsakanin Diyana da Afreeda wani sa'in kaji Hajiya tace " ƙarya ne lokacin da suka gama cin abinci ƙarfe biyar na yama suka fara shirin tafiya , Hajiya ce tace " zan bar miki Tinene ta tayaki zaman kaɗaici , no ki tafi da ita kawai Diyana ta faɗa tana yamutsa fuska , kan uba Hajiya tace " to karki ɗauketan Allah yasa ina sonta masu mugun hali kawai kedai wanan yaya bansan inda kika kwaso mummunan hali ba ke zomu tafi , ta nuna Afreeda Diyana ce tace " gobe driver zai kawota ƙundun uba wlh baku isa ba , kinƙi riƙe Tinene shine kikeson ki bar ƙanwarki to ƙafata ƙafarta , haɗa ido Diyana sukayi da Afreeda Diyana tace " pls dont follow her my sis , iye yo ko Alhaji ne ya zageni da turanci na barshi bare ku marasa kunya maza fito mu tafi , Guduwa Afreeda tayi har mgrib bata fito ba ga Diyana anyi juyin duniya taƙi magana da Hajiya taga uwar bari dole ta riƙe hanun Tinene suka bar palon tana masifa kamar zata ari baki, suna zuwa driver ya taso da gudu da har zai tambayi Afreeda jin faɗan da Hajiya ke surfawa yasa shi jan baki yayi shiru , haka dai suka shiga mota bata dena masifa ba sai da sukayi nisa ta fara gyan gyaɗi Tinene kam ranta ya ɓaci ashe dama haka yan binni ke ƙyamatar yan ƙauye take magana cikin zuciyarta , suna isowa Tinene ta tashi Hajiya , ana buɗe musu mota suka fice , da shigar su palon suka sami momy da dady suna cin abinci , zama sukayi a kan kujera Hajiya tace " faɗima kinga mun dawo babu wanan yarinyar ko , to nayi nayi dasu ina kunen ƙashi garesu nace tazo mu tafi taƙi wlh haka na barta , ita wace na tafi da ita ta tayata aiki, wanan mai kamada zabiyar taƙi ƙarɓarta oh ni naga duniya , dady ne yace " to ai shikenan momy tace " amma Diyana batada kirki ko kaɗan kai da ɗan uwanka , ita kuma Afreedan mijin nata na nan shine tazauna musu ko , ina driver yazo ya ɗauko ta , barin kirata a waya dady yace " yana ɗauko wayarsa a aljihu , lambar Diyana ya danna cikin sa'a ta shiga , ina Afreeda ? tambayar da dady ya wurgowa Diyana kenan , Afreeda gata nan ina yini dady lafiya dady yace " yaci gaba da magana mijin naki na nan shine dan bakuda hankali kika barta anan ko ? lahh dady bayanan wlh ɗazu ya tafi Abuja gidan su , oky dady yace " tare da katse wayar , ajiyar zuciya Diyana da Afreeda sukayi sunata tsalle , Hajiya dake jin abinda ake faɗe tace " ƙarya suke ko kafin mu fito yana gida yama fita aiki ne , momy dai batada bakin magana dady ma ci gaba yayi da cin abincin sa dan rigimar Hajiya ta musamman ce , miƙewa tayi ta nufi ɗakinsu dan yin sallah , momy ce ta kalli Tinene tace " kije kiyi sallah kizo kici abinci to Tinene tace " ta miƙe .

Kamill na isa kai tsaye gidansu ya wuce part ɗin Abbansa , cikin sa'a ya sameshi yana zaune da wani akwati a hanunsa , oyoyo my son Abba ya faɗa cikin farinciki , zama kusa da Abba Kamill yayi tare da risinawa ya gaishesa , bayan Abba ya amsa ne yake tambayar Diyana lafiya lau Kamill yace " jiya ma aka sallamo mu daga hospital , a firgice Abba yace " mai ya sameta ? wlh zazzaɓi shiru Abba yayi dan ya fara ƙisima wani abu a ransa , to Allah ya bata lafiya Abba yace yana cigaba da duba akwatin dake gabansa, hankalin Kamill ne ya koma kan akwatin ya zubawa kayan akwatin ido , cikin azama Kamill ya ɗauko wani photo yana gogewa yace " Abba munyi kama da wanan matar kodai itace " umma na ? shiru Abba yayi hawaye nabin kuncin sa , Abba meya faru dan Allah bata mutu bane ko ta mutu ? ina zan sani my son Abba ya faɗa da muryar kuka to ina take saceta akayi , tagumi Abba ya zuba dan wanan amsar kalma ɗaya zai iya gayawa Kamill itace " mun nemeta mun rasa kaf dangina da danginku babu mai ambatarta bare su tambayeka , ya ilahi koni mancewa nayi da ita tun daga lokacin da ta ɓata, miƙewa Kamill yayi idanunsa sunyi jawur da

alamun damuwa a ransa kimanin shekaru talatin da ƙyar ma idan tana raye , jikin bango yaje ya zame yana kuka mai ban tausayi ya taso cikin gata da soyayya a guri ubansa amma bai san daɗin mahaifiya ba tabbas dole ya nemo mahaifiyarsa ko labarinta koda hakan zaiyi sanadin rayuwarsa , kuka yake mai sauti yayin da Abba ya kasa rarrashin sa , shima kukan yake babu mai bawa wani haƙuri.
Muje masallaci muyi isha'i inyaso sai muyi magana anjima in mun dawo , haka suka fita fuskarsu babu walwalh masallacin gidan suka nufa inda sukayi alwalah Kamill ya daɗe yana adu'ar Allah ya baiyana mahaifiyarsa haka ma ɓangaren Abba suna idarwa suka dawo babban palon Abban , abinci masu aiki suka jere musu , Abba ne yace " kaci abinci tukun sai muyi magana.
[01/07, 6:16 pm] Mom Islam Ce: 43 & 44

Cikin sauri ya dinga tura abincin badan komai ba sai dan yana jin yunwa banda haka abincin ma ba daɗi yake yimasa ba , koda ya gama dawowa yayi gurin wanan akwatin ya buɗesa , hotunansa ya gani lokacin yana ƙarami gakuma matar da Abba yace mahaifiyarsa na tungume dashi sunyi kama sosai , Abba ina jin mu bada cigiya gidan redio da gidajen tv dakuma zaridu duk dai kafafen sada zumunta , em my son Abba yace " zamuje amma sai zuwa gobe yanzu kam dare yayi , haka suka zauna su saƙa wanan su kunce wanan , misalin ƙarfe tara na dare Kamil ya miƙe tare da nufar part ɗinsa duk da yayi aure ɗakin bai sauya a mazaunin nasa ba , yana shiga yayi wa ƙofar key kana ya cire kayan jikinsa yasa na bacci , tunowa yayi da Diyana tabbas baiyi adlci ba tunda yaga photon mahaifiyarsa ya kashe waya ,number ta ya shiga gwada a cikin rashin sa'a yaji switch of abu goma da ashirin shikam wace jarabawa ce take neman sa , da haka bacci ya ɗaukesa cike da mafarkin Diyana tana ta kuka , washe gari tunda yai sallah ya kasa komawa bacci ƙara gwada lamar yayi jin a kunne yasa shi sakin murmishi , aslm my blood haɗe fuska Kamill yayi kamar tana ganinsa yace " nayi fushi ai, dariya Diyana tasa kana tace " wato ka iya wayo ni banyi fushi ba sai kai ? to afuwan mijina yau ɗin zaka taho , jim Kamill yayi kana yace " my Diya wata yɔar matsala ce ta taso dan Allah ki kwantar da hankalinki zuwa gobe da wuri zan dawo ,bu buha ƙafa Diyana ta shiga yi tana cewa " to mai ke faruwa naga mood ɗinka duk ya sauya ina ji a jikina babu lafiya fa , murmishin yaƙe yayi dan ya kwantar mata da hankali sanin sharuɗan da likita ya bada yasa shi cewa " kawai muna zuwa duba company ɗinmu ne shi yasa , uhm Diyana tace " ina Abba kace ina gai she shi , zai ji kina shan magani kuwa ? eh Diyana tace " gama Afreeda tare muka kwana , Kamill ne yace " bata wayar , miƙa mata wayar Diyana tayi cikin jin kunya Afreeda tace " barka da safiya yaya , yawwa barka ƙanwarmu dafatan kin tashi lafiya ? lafiya lau Afreeda tace " yasu Abba , Abba yana lafiya cewar Kamill , me zan siyo miki ?" amma sai zuwa gobe zaki tafi ko ? cewar Kamill , a'a anjima driver zai zo , dariya Kamill yasa yace " aiko babu inda zaki kibari zuwa gobe zan taho miki da tsaraba kinji cikin jin kunya Afreeda tace " Allah ya kaimu ta miƙawa Diyana wayar, my Diya Kamill ya faɗa cikin sanyin murya kinsan me ? a'a Diyana tace " nayi mafarki kin haifi twins cikin dakiya yake maganar dakuma ƙoƙarin ganin ya sanyata farinciki , dariya tasa tana cewa " to wazai tayani raino ? ni da ke man my Diya sai zuwa anjima ya katse zancen , ok ka kulamin da kanka mijina ta manna wawayar kiss , katse wayar yayi tare da furzar da isaka mai huci ya fito tare da sanya takalminsa ya nufi part ɗin Abba , samun Abba yayi yana breakfast , cikin ladabi ya durƙusa ya gai dashi , shafa kansa Abba yayi tare da sanya masa albarka , neman guri Kamill yayi ya ƙurawa Abba ido , yɔan kwanakin nan ya rame matuƙa , tausayin kansa ne ya kamashi ashe ko gawar mahaifiyarsa babu labari taɓɓ innalilahi shikam yaga tasku , lura da duniyar da ya tafi ne yasa Abba cewa " my son ka rage tunani fa , to Abba Kamill yace " badan yanajin zai iya ba , ƙara dubansa Abba yayi a karo na biyu yace " son zo kayi breakfast yanzu zamu fita , cofee kawai zan sha Abba bazan iya cin abinci ba , kallon tausayi Abba yayi masa bai ce komai ba , Abba ne ya haɗa masa cofee ɗin tare da bashi a baki kai kace " ƙaramin yaro , yana gama sha Abba ya tattaro wayoyinsa da abubuwan da zai buƙata suka fito shida Kamill , ko ɗakin Ameena basu nema ba

sukayi ficewar su ,driver na ganinsu ya tada mota tare da buɗe musu back side suka shige , kai tsaye gidan redio suka nufa tare da bada cigiya , suna fitowa Abba yaje gidan jarida zasu nan ma suka bada cigiya harda gidan tv sanan suka dawo gida , kafin su dawo suna hanyar tahowa sukaji ana cigiyar mahaifiyar Kamill , jikin Kamill ne yai sanyi yace " Abba kaji har an fara sanarwa , eh Abba yace " batare da ya ƙara magana ba , gida suka wuce lokacin ƙarfe uku na rana , a gajiya suka zarce bedromm ɗin Abba , wash Kamill yace " dubansa Abba yayi kana yace " ka kira yatinyar nan kaji ya jikin nata , wlh na mance Abba amma ɗazu da safe munyi waya , ok Abba yace " Kamill ne yace " Abba mai zai hana mu kira malamai ayi abin sadaka dakuma saukar alqur'ani mai girma akan Allah ya baiyano da mamana , idanun Abba ne suka ciciko da hawaye sbda kar ya karayar wa da Kamill zuciya yasa bai bari ya gane ba , za'ayi Kamill insha Allah kuma zansa a tayamu da adu'a yanzu ma barin kira malam Usman cewar Abba , ciro wayarsa yayi tare da danna number , cikin sa'a ta shiga yana ɗauka suka gaisa , Abba yayi masa bayanin komai , malam Usman ne yace " wato wanan al'amarin akwai rikitarwa an yiwa matarka abinda bazaku sake haɗuwa ba kuma bazata sake wai wayar yan uwanta ba , tana nan a raye insha Allah zamu ƙoƙarta da adu'a kuma za'a ganta , farinciki fal zuciyar Kamill , washe gari yau kwanan Kamill biyu yau yake shirin tafiya gida gashi yanason su ƙara bincike , zaune suke a Familly palo wanda inhar kana zaune zakaga kowa mai shige da fice koma wanene kasacewar ƙifofin glass ne , labarin da aka hasko ne a tv yaja hankalinsu sosai , jin an saki cup a ƙasa sukayi an gurfana da guwaiwa , juyawar da za suyi Ameena ce take uban kuka tana cewa na shiga uku , anga wanan matar a garin Kaduna a gindin gadar bakin dogo tana bara , a gigice Abba ya miƙe bai tsaya saurarar Ameena ba ya fice da gudu yana ƙwalawa drivers kira , cikin sauri suka iso tare da durƙusawa , maza kuje offic ɗin police na kaduna ga adrees ga number waya kuna isa ku kira anga Maimunatu , masha Allah suke faɗi kasancewar duk sun santa , suka ɗibi mota Abba yace" zan dinga kiranku inajin yanayin tafiyar taku , Allah ya tsare Abba yayi musu tare da komowa ciki ya sami Kamil yana ta kaiwa Amenna naushi baji ba gani, A'a meye haka son ? idanun Kamill sunkaɗa sunyi jazur kamar garwashi yace " Abba itace itace ,itace me ? Abba ya tambaya zata gaya maka koma menene , Kamill na saketa tahau cewa " nice na koreta gashi boka ya mutu na rabata da kowa nata na korata gari mai nisa gashi an ganta sai na kasheta sai na kashe ta , ran Abba ne ya ɓaci ya danna number mahaifiyar Ameena tare da cewa " zan sakota a mota a kawota gida zata gai sheku daga haka yayi mata sallama ya nufi bedroom ɗinsa ya fali takarda ya rubuta mata saki uku , ya dawo palo ya wurga mata , akwati ɗaya Abba ya wurgo mata tare da kiran ragowar drivern da ya rage yace " ya kaita bauchi , ihu ta sanya tare da ɗurawa Abba zagi ga dukka halamu sai dai muce inzaka gina ramin mugunta ka gina dai dai kai gudun kar wata rana ya rifta da mai haƙin ramin , tana kuka haka suka shiga mota ga takardar sakinta a hanunta tana ta surutai.

10:pm shiru shiru babu labarin Kamill gashi tana ta gwada waya taƙi shiga , a kira na shida ne ya ɗaga tare da cewa " dan Allah kiyi haƙuri anga Ummana shine ya hanani dawowa , tsalle Diyana ta doka tare da miƙa godiya ga Allah tace " kodai muzo gobe ne ? kibari zuwa jibi kafin nan ta warware sai kizo kiyi1 week cikin farinciki Diyana ta ce a gaisheta sukayi sallama ,Afreeda dake kallo bacci na shirin ɗaukarta tace " sis dafa bakison mijin amma naga yanzu kamar zaku haɗiye juna ? dariya Diyana tasa tace " to yar sa ido zomuje mu kwanta jibi zamu wuce kano zaki ko ? zaro ido Afreeda tayi kana tace " ina tsoron dady sai dai in shi yayan ne zai kira ya faɗa , karki damu insha Allah tare ma zamu tafi ki kwantar da hankalinki suka wuce bedroom suka kwanta sai muce asha ta gari.

sai 11:pm drivers suka shigo inda gidan ya turare da ƙamshi iri iri Abba yasa ayi girki girke masu rai da lafiya , shigo da umman Kamill sukayi duk tayi tsufan wuya dama shekaru sun ja , wanka ta shiga a ɗakin da yake nata a da tana fitowa Abba ya shafa mata mai ya sanya mata powder ya ɗauko doguwar riga yar kanti fara da ɗankwalinta ya shirya umma tsaf ya fito da ita hanunta riƙe da nashi suka fito palo

inda Kamill ke zaune yana hawayen farinciki , ganin umma da Abbansa ba ƙaramin daɗi yaji ba har yana musu photo Abba ne yace " son baka girma ko , ita dai Umma sai raba ido take hankalinta na dawowa jikinta a hankali amma batasan ko waye Kamill ba ,cikin ladabi ya durƙusa yace " umma ina yini , lafiya tace " tana ƙare masa kallo da mai kamada tanason gano wani abu , Abba ne ya katse mata tunani ta hanyar cewa "ɗanki ne Kamill fa , nan da nan hawaye suka zubo a fuskarta tace " Kamilu ashe Allah zai haɗamu ? shima Kamill ɗin kuka yake yaje ya rungumeta .
Diyana ce ta kira dady take sanar masa abinda ke faruwa a gidansu Kamill na ganin mahaifiyarsa da akayi sun tayashi farinciki dady yace " goben idan kun shirya kubiyo ta nan sai mu je mu dubo ta ,
washe gari Diyana da Afreeda sun gama shiri suka fito Diyana ce ta miƙowa Afreeda bag ɗin kayansu kasancewar duk yanayin jikinsu ɗaya kuma Afreeda bata ɗauko kaya ba , suka nufi mota , driver na tada mota suka ce anguwar su za'a kaisu babu musu cikin lokaci ƙalilan sai gasu yai horn aka buɗe suka shige , da gudu Diyana ta shige tana kiran momy , momy dake tsaye da gyale a hanunta batasan lokacin da ta rungume Diyana ba tana murna , Hajiya ce ta fito sanye da hijab a karkace tana cewa in kun gama rashin kunyar kufito muje kar muyi dare , bayan sun gaisa da kowa suka nufi tasu motar da ban Diyana ma tasu daban suka ɗauki hanya zuwa Kano ,sunyi tafiya mai nisan gaske kana suka iso garin kano sai da suja kuma yin wata tafiyar sai gasu a bakin wani tangamemen get wato gidasu Kamill , ana buɗe get suka shige akayi parking kowa ya fito dama Diyana ta gayawa Kamill zasuzo suna shiga da sallama suka sami Abba da umma zaune a kujera ɗaya Kamill na gefe yana dadanna waya , durƙusawa yai ya gaida su dady tare da Hajiya da momy , zama sukayi tare da yi musu murna na ganin umma Abba ne ya dubi Umma yace surukanki ne fa murmishi Uma tayi aka sake sabuwar gaisuwa , tashi ɗaya aka cika musu gabansu da kayan motsa baki, Kamill ne ya fice tare da kashe wa Diyana ido , umma ta lura da komai murmishi kawai tayi , Diyana na ganin Kamill ya fita ta fara shirin kiran wayar ƙarya itama ta fice kaf cikin ɗakin sun gano su amma babu wanda yai magana , Afreeda na ganin basuda kunya, kai tsaye harabar gidan ta fito ta rasa ina zata dosa ya sadata da ɗakinsa , ji tayi an ɗagata sama ana tafiya da ita dariya tashiga yi tana cewa my blood baka ganin masu aiki ne , bai kulata basai da ya sauketa a tsararren ɗakinsa mai sanyin ƙamshi , direta yayi a tangamemen bed ɗinsa tare da raɗa mata nayi missing ɗinki fa , rufe fuska tayi adu'arta Allah yasa kar ya taɓa mata lafiyar jiki , zoki shirya min kaya anjima zamu wuce , no ni bazan tafi ba gurin umma zan zauna , dariya Kamil yasa yace " umma taga Abba sai kuma yai shiru , daga haka suka shiga hirar yadda sukayi kewar junansu .
 dady da momy dakuma hajiya ne suka fito da niyar tafiya aikuwa Abba yasa an haɗa musu hidima sosai , umma tayi murna , ganin babu Diyana babu alamarta yasa su wucewa batare da sun nemeta ba.

After nine months
Diyana na hango da ƙaton cikinta aihuwa yau ko gobe wata ranar laraba tana zaune taji azabar ciwon baya da mara , hajiya dake zaune a gidan tunda cikinta ya tsufa ta lura da naƙuda take hakan ya sata yi mata adu'a ta bata tasha cikin ikon Allah mai sosai ya fara sai gashi ta santalo yarinyarta mace , fara kyakyawa , gyara baby Hajiya tayi kana ta gyara gurin dakuma mai jego , sai da Diyana tayi wanka Hajiya taga tana cikin ƙoshin lafiya aka kira su momy aka sanar musu dasu Abba da Kamill dake Kano farinciki ba'a magana ranar suna yarinya taci sunan umma gata kam Diyana ta ganshi , motsi kaɗan tayi za'a tambayeta meye , farinciki a famillyn abin sai san barka.
Ansa bikin Afreeda inda ta sami wani ma'aikaci shima yanada kuɗi sosai cikin wata uku akayi biki lokacin yarinyar Diyana ta fara wayo da suke yimata laƙabi da Umaima , ga dariya , biki akayi na manya kasancewar gagarumar gudun mawar da Abban Kamill dakuma shi Kamill ɗin ya bada ranar ɗaurin aure anyi event sosai bikin ya birge kowa ankai amarya cikin Abuja A. Y. A anguwa ce ta manyan mutane gidanta ita

ɗaya , sai dai muyi mata fatan Allah ya kawo ƙazantar ɗaki , anan na kawo ƙarshen wanan littafi kurakuren dake ciki Allah ka yafe mana Allah kasa ya faɗakar kana yakuma amfani al'umma bissalam .

Domin neman ƙarin bayani 08141799224.

MOM ISLAM